Littafin kyauta ne; Ba na sayarwa ba

وقف لله تعالى: فلا يجوز بيعه

# SHARHIN LITTAFIN

## "Muhimman darussa ga daukacin Al'umma"

## شرح كتاب

## "الدروس المهمة لعامة الأمة"




Na Shehun Malami
Abdul'aziz dan Abdullahi Ibnu Baaz

Malami Mai Sharhi
Dr. Haisam dan Muhammadu Jamil Sarhan

Tarjamar
Dr. Abubakar Hamza Zakariyya Misau

# SHARHIN LITTAFIN

## "Muhimman darussa ga daukacin Al-umma"

## (الدروس المهمة لعامة الأمة)

Na Shehun Malami Abdul'aziz dan Abdullahi **Ibn Baaz**
–Allah ya yi rahama a gare shi-

Malami Mai sharhi:

**Dr. Haisam dan Muhammadu Jamil Sarhan**
Tsohon Mai karantarwa a Sakandaren Masallacin Annabi SAW
http://attasseel-alelmi.com

Allah ya gafarta masa, da iyayensa biyu, da wanda ya taimaka masa wajen buga littafin

Tarjamar
**Dr. Abubakar Hamza Zakariyya Misau**

**Littafin kyauta ne, Ba na sayarwa ba**

Bugun farko

**2020 = 1442AH**

Tuntube mu:

islamtorrent@gmail.com

فسح وزارة الإعلام

## Sharhin MUKADDIMAR Mawallafin

Shehin Malami Abdul'aziz dan Abdullahi bn Baaz – رَحِمَهُ اللَّهُ - ya ce:

Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai! Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai. Kyakkyawar makoma ta masu tsoron Allah ce. Tsira da amincin Allah su kara tabbata ga BawanSa kuma ManzonSa Annabinmu Muhammadu, da Iyalan gidanSa da SahabbanSa baki daya.

**Bayan haka:** Wadannan takaitattun kalmomi ne, dangane da abinda ya wajaba ga dukan Mutane su sani game da addinin Musulumci. Na sanya masa suna (**MUHIMMAN DARUSSA GA DUKAN AL'UMMA).**

Ina rokon Allah ya amfanar da Musulmai da su, kuma Ya karba min; lallai Shi Mai kyauta ne Mai karamci.

**Abdul'aziz dan Abdullahi dan Baaz**

## Me yasa muke karatun littafin MUHIMMAN DARUSSA?

Saboda darussan suna da muhimmanci, kamar yadda Mawallafin littafin – رَحِمَهُ اللَّهُ- ya basu suna, kuma Maluma sun yi nasiha kan karanta su.

Da mai Magana zai ce: E, darussan suna da muhimmanci, amma ga Mutane gama-gari, ba daliban ilimi ba, saboda jin cewa martabarsa ta ketare ta gama-garin Mutane!

**Amsa:** Za mu masa tambaya kan abinda littafin kunsa, idan har bai sansu ba, to gama-garin Mutane sun fi shi alheri. Kuma Dalibin ilimi ya dace ya zama mai tawali'u, kuma kada ya yi girman kai ga ilimi da Maluma, sai kuma ya tafi akan tafarkin da Malaman Allah suka tafi a kai. Ya zo cikin Sahihul Bukhariy: Mujahid ya ce: **MAI KUNYA DA MAI GIRMAN KAI BA SU KOYAN ILIMI**.

## Me littafin "Muhimman darussa" ya kunsa?

1. Ya kunshi hanyar Magabatan kwarai wajen mu'amalantar Alkur'ani, ta fiskar karatunsa da haddarsa, da fahimtarsa, da yin aiki da shi.
2. Bayanin hakikanin Musulunci, da imani, da ihsani, da tauhidi, da karkasuwan shirka.
3. Bayani akan sallah.
4. Bayani akan alwala.
5. Sifantuwa da halayen da aka shar'anta, da ladabtuwa da ladubban Musulunci.
6. Tsawatarwa daga shirka, da kuma nau'ukan sabo.
7. Shirya matacce, da yin sallah a gare shi, da bunne shi.

### Me yasa Maluma suke fara littatafansu da Bismillah?

1. Domin koyi da littafin Allah, da Annabawa da Manzanni
2. Saboda hadisin "Dukkan lamari me muhimmanci, albarkarsa tana yankewa idan ba a fara da sunan Allah ba". Tare da raunin hadisin.
3. Domin koyi da Maluman Magabata, wadanda suke bude littatafansu da Bismillah (sunan Allah).
4. Domin neman albarkar farawa da sunan Allah Ta'alah.

## Darasin farko

### SURATUL FATIHA DA GAJERUN SURORI

A koyi karatun suratul Fatiha, tare da abinda ya sawwaka na gajerun surori, kamar daga suratu (Izazul) zuwa (Nasi), a koye su daga bakin Malamai, a inganta karatunsu, a hardace su, tare da sanin fassarar abinda ya wajaba a fahimce shi na ma'anoninsu.

### Karin bayani:

Ya dace Mutum ya yi hadda kamar yadda Magabata suke yi, wato kowane yini ayoyi goma, tare da karanta tafsirinsu, daga littafin tafsiri takaitacce, kamar tafsirin Sheikh Ibnu-Sa'adiy, domin hakan ya taimaka wajen yin aiki da ayoyin.

### Da wane tafsiri 'Dalibin ilimi zai fara?

'Dalibi ana masa nasihar ya fara da **"TAISIRUL KARIMIR RAHMAN FI TAFSIRI KALAMIL MANNAN"** Na Shehun Malami Abdurrahman dan Nasir As-Sa'adiy –Allah ya yi masa rahama kuma ya gafarta masa-. **Don me?**

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| Saboda Malamai sun yi nasihar a rika karanta shi, kuma sun bashi muhimmanci. | Saboda Tafsirin takaitacce ne, sai ya dace karamin 'Dalibi ya rika karanta shi. | Saboda kalmomin Tafsirin suna da sauki kuma ma'anarsu a fili take; babu rikitarwa. | Saboda yana taimako wajen yin aiki da Alkur'ani, da izinin Allah. | Saboda Mawallafin –Allah ya masa rahama- ya bada muhimmanci ga lamarin Tauhidi. |

**Menene rabe-raben Mutane dangane da mu'amalantar Alkur'ani?**

Mutane dangane da Alkur'ani sun kasu zuwa bangare biyu abin ki, da tsaka-tsaki:

**Mai sakaci**
Yana kaurace wa Alkur'ani, kuma hakan yana kasancewa ta wadannan fiskoki

**Mai ketare iyaka**
Yana karanta shi, haddace shi, amma baya kokarin fahimtarsa, ko aiki da shi.

**Mai tsakaitawa**
Yana lazimtar karatunsa, haddarsa, yana kokarin sanin ma'anarsa, yana kuma neman taimakon Allah wajen aiki da sakonsa.
Wannan shine halin Magabatan kwarai, da Mabiyansu.

- Kaurace wa karatunsa
- Kaurace wa haddarsa
- Kaurace wa neman fahimtarsa
- Kaurace wa yin aiki dashi
- Kaurace wa neman waraka dashi

**Allah Ta'alah ya ce:** "Kuma Manzo ya ce: Ya Ubangijina! Lallai Mutanena, sun riki wannan Alkur'anin abin kauracewa" (Furkan: 30). Kuma Annabi –sallal Lahu alaihi wa sallama- ya ce: "Lallai daga tsatson wannan Mutum (wato daga bayansa da 'ya'yansa) za a samu wasu Mutane suna karanta Alkur'ani baya wuce makogoronsu, suna kashe ma'abota Musulunci, suna kuma barin ma'abota gumaka, suna ficewa daga Musulunci kamar yadda kibiya take fita daga dabbar da aka harba, lallai idan Na riske su, zan kashe su irin kisan jama'ar Adawa" **(Bukhari 3610 and Muslim 1064).**

## *TSAKURA DAGA LITTAFIN "TAISIRUL KARIMIR RAHMAN FI TAFSIRI KALAMIL MANNAN" NA SHEHUN MALAMI ABDURRAHMAAN AS-SA'DIY -ALLAH YA YI MASA RAHAMA-, TARE DA TAMBAYOYI AKANSU*

### *[Tafsirin suratul* Fatiha*, wanda ta sauka a Makkah]*

**1. Da sunan Allah, Mai rahama, Mai jin kai. 2. Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin halittu. 3. Mai rahama Mai jin kai. 4. Mai nuna mulki a ranar sakamako. 5. A kai muke yin bauta, kuma daga gare ka muke neman taimako. 6. Ka shiryar da mu ga hanya madaidaiciya. 7. Hanyar wadanda ka yi wa ni'ima, ba wadanda aka yi wa fushi ba, kuma ba batattu ba.**

**(1)** Ma'ana: Ina farawa da dukkan sunayen Allah Ta'alah; domin lafazin (ismun) tilo ne da aka yi idafarsa, sai ya game dukkan sunayen Allah. "**Allah**", shine abin bauta wanda ya cancanci a kebance shi da bautar, saboda abinda ya sifantu da su na sifofin cancantar bauta, wadanda sune sifofin kamala. **"ArRahmanir Rahim; Mai rahama Mai jin kai"**. Sunaye ne guda biyu da suka yi nuni cewa lallai Allah Ta'alah Ma'abucin yalwatacciyar rahama ne mai girma, wanda ta game dukkan komai, da dukkan rayayye, kuma ya rubutata ga masu takawa mabiya AnnabawanSa da ManzanninSa. Su muminai suna da cikakkiyar rahama gamammiya. Wanda ba Musulmi ba, shi kuma yana da wani abu daga cikinta.

Lallai ka sani; Yana cikin ka'idodin da aka yi ittifaki akansu, wato Magabatan wannan al'ummar da Malamanta; ka'idar ita ce: Yin imani da Sunayen Allah, da sifofinSa, da hukunce-hukuncen sifofin, sai su yi imani –ga misali- da cewa: Shi Allah Rahamanu ne kuma Rahimu, Ma'abucin rahamar da ya sifantu da ita, wanda take ta'allaka da bayinsa da ya yi wa rahama, kuma ni'imomi gabadayansu suna daga tasirin rahamar Allah. To, haka sauran sunayenSa.

Za a fada dangane da sunan **Al-Alimu**; Cewa Allah Al-Alimu sunanSa ne, kuma Masani ne, ya san kowane abu. **Kadirun**, Ma'abucin iko, wanda yake da kudura da iko akan komai.

**(2) "Godiya ta tabbata ga Allah"**, Yabo ne ga Allah da sifofin kamala, da kuma ayyukansa wadanda ba su ficewa daga falala da adalci. Don haka, yabo cikakke nasa ne, ta dukkan sifofi. **"Ubangijin halittu",** Rabbu (Ubangiji) wanda yake renon halittu gaba daya. Su kuma "Alamina" sune duk wanda ba Allah ba, kuma shine ya halitta su, ya samar musu da kayan amfani, yake kuma kwararo musu da ni'imominsa masu girma, wadanda idan suka rasa su, ba za su wanzu ba, domin babu wata ni'ima face daga wajensa suke shi kadai. Kuma renon Allah Ta'alah ga Halittunsa, nau'i biyu ne; Mai gamewa da kebantacce:

- **Mai gamewar** ita ce, yadda ya halitta su, ya ke azurta su, yake shiryatar da su ga maslahohinsu, wanda sai da su za su iya wanzuwa a Duniya.
- **Kebantacciyar** kuma, ita ce, TarbiyyarSa ga WaliyyanSa; sai ya rene su da imani, ya datar da su gare shi, ya basu kamala, ya tunkude musu dukkan abubuwan da za su kautar da su daga gare shi. Kuma hakikaninta shine: Tarbiyyar dace ga kowane alkhairi, da kariya daga dukkan sharri. Kuma la'alla wannan shine sirrin da ya sanya addu'oin Annabawa suka kasance da lafazin: Ya Rabbi (Ya Ubangiji), domin bukatunsu gaba daya sun kunsu ne karkashin kebantaccen renonSa. Sai fadinSa **"Ubangijin halittu"**; ya yi nuni kan kebantuwar Allah da halitta, da jujjuya lamari, da yin ni'ima, da cikar wadacinSa da kuma bukatuwar dukkan halittu gare shi ta kowace fiska da yanayi.

**(4) "Mai nuna mulki a ranar sakamako".** Mamallaki: Shine wanda ya sifantu da sifar mulki wanda cikin tasirinta akwai bada umurni da hani, da yin sakayya da ukuba, kuma yana aikata dukkan abinda yake so da bayinsa da ya mallaka. Kuma ya jingina mulkin ne ga ranar sakamako, wanda shine ranar kiyama, ranar da za a yi hisabi a cikinsa ga Mutane kan ayyukansu; na alkhairi da sharri; saboda a wannan yinin ne cikar mulkin Allah da adalcinSa da hikimarSa za su bayyana ga halittu a fili, kuma mallaka irin ta halittu za ta yanke, sai masu mulki a wannan ranar su daidaita da talakawa, dukkansu za su mika wuya ga girmar Allah, su kaskantar da kai ga buwayarSa, suna jiran sakayyarSa, suna fatan ladanSa, suna tsoron azabarSa; Wannan ya sanya Allah ya ware wannan yinin da ambato, tare da cewa shine Mai mulkin yinin sakamako da sauran yini gaba dayansu.

**(5) Fadinsa: "A kai muke bautawa, kuma a gare ka muke neman taimako"**, Ma'ana: Muna kebe ka kai- kadai da bauta da kuma neman taimako, saboda gabatar da ambaton kalmar (iyyaka) tana amfanar da (hasr) wato kebewa, ko tabbatar da hukunci ga wanda aka ambata, da kore shi ga wanda ba shi ba; wato kamar yana cewa: Muna yin bautarka, ba za mu bauta wa waninka ba, muna neman taimakonka ba mu neman taimakon waninka. Gabatar da ambaton bauta akan neman taimako yana daga gabatar da lafazi mai gamewar ma'ana akan kebantacce. Da muhimmata ko gabatar da hakkin Allah akan hakkin Bawa. Ita kuma ibada "Suna ne na dukkan abinda Allah yake so, kuma ya yarda da shi; na ayyuka da zantuka na zahiri da na boye". Neman taimako (**isti'anah**) shi kuma "Shine: Dogaro ga Allah Ta'alah, wurin janyo amfani, da tunkude abubuwa masu cutarwa, tare da amintuwar zuci wajen neman tabbatuwan hakan".

Kuma tsayuwa wajen bautar Allah da neman taimakonsa sune hanyoyin samun sa'ada na har abada, da tsira daga dukkan sharri, kuma babu hanyar samun tsira sai ta hanyar su biyun. Kuma ibada tana kasancewa ibada ne idan ta kasance an koyo ta daga Manzon Allah (SAW), kuma an nufi Allah da ita, da wadannan lamuran biyu ne za ta kasance ibada. Kuma ambaton (isti'anah) bayan (ibadah) tare da cewa tana shiga cikin ibadar, ya kasance ne saboda Bawa a cikin dukkan ibadodinsa yana bukatar taimakawar Allah Ta'alah, domin idan Allah bai taimake shi ba, to lallai ba zai iya aiki da umurni, ya hanu da hani ba. Sa'annan Allah Ta'alah ya ce: **(6) "Ka shiryar da mu hanya madaidaiciya"** Ma'ana, ka nuna mana shi, ka nusar da mu, ka shiryatar da mu zuwa ga hanya madaidaiciya, wanda ita ce hanyar da take a fili, mai sadarwa zuwa ga Allah da samun AljannarSa. Wanda kuma ita ce sanin gaskiya da yin aiki da ita, sai ka shiryar da mu zuwa ga hanyar, kuma ka shiryar da mu a cikin hanyar, saboda shiryuwa zuwa ga wannan hanyar shine lazimtar addinin Musulunci, da barin sauran addinai, shi kuma shiryuwa a cikin hanyar, yana kunsar dukkan ayyukan addini ta fiskar ilimi da aiki, don haka, Wannan addu'ar tana da gamewar ma'ana, kuma ita ce tafi amfani ga Bawa, wannan ya sanya Mutum ya rika yin wannan addu'ar a cikin kowace raka'a ta sallarsa ya kasance wajibi, saboda bukatuwarsa zuwa ga hakan, kuma wannan tafarki madaidaici shine: **(7) "Hanyar wadanda ka yi ni'ima a gare su"** na daga Annabawa da Siddikai da Shahidai da Salihai, **"Ba"** hanyar **"wadanda aka yi fushi da su ba"** wadanda suka san gaskiya sai suka yi watsi da ita, kamar Yahudu da makamantansu, kuma **"ba"** hanyar **"batattu ba"** wadanda suka bar gaskiya saboda jahilci da bata, kamar Nasara da makamantansu.

Wannan surar duk da gajarcinta, ta kunshi abinda babu wata sura a cikin Alkur'ani da ta kunshe shi; kasancewar ta kunshi nau'ukan Tauhidi uku; *Tauhidin Rububiyyah*, kadaituwar Ubangiji, wanda ake daukansa daga fadinsa: **"Ubangijin dukkan Duniya"**; *Tauhidin Ilaahiyyah*, Kadaituwar abin bauta, shine ka kadaita Allah a cikin bauta, wanda ake daukarsa daga lafazin **"Allah"** da kuma cikin fadinsa: **"A kai muke bauta, kuma daga gare ka muke neman taimako"**; da *Tauhidin Asma´u wasSifaat*, wanda shine tabbatar da sifofin kamala ga Allah Ta'alah, wadanda ya tabbatar da su ga kansa, kuma AnnabinSa (SAW) ya tabbatar masa da su, ba tare da *ta'adil* (kore wa Allah sifofi ba), ko *tamsil* da *tashbih* (kamanta Mai halitta da halittu ba) kuma ya yi nuni akan wannan, lafazin **"Alhamdu"** kamar yadda ya gabata.

Kuma surar ta kunshi tabbatar da Annabta, a cikin fadin Allah **"Ka shiryar da mu hanya madaidaiciya"** saboda nusarwar ba za ta yi wu ba, face ta hanyar Manzanci. Da kuma tabbatar da lamarin sakayya akan ayyuka, wanda ya zo cikin fadin Allah: "**Mamallakin ranar sakamako"** saboda sakamakon yana kasancewa da adalci; domin kalmar „"**addini**" tana nufin bada sakamako cikin adalci. Kuma surar ta kunshi tabbatar da kaddara, da kasancewar Bawa tabbas shi yake aikata aikinsa, sabanin akidar *Kadariyyawah*, wadanda suke kore kaddarar Allah, da kuma *Jabariyyawah*, wadanda suke korewa Mutum aikinsa. Bal wannan surar ta kunshi raddi da martini ga daukacin 'Yan bidi'a batattu, a cikin fadin Allah: "**Ka shiryar da mu hanya madaidaiciya**" saboda hakan shine sanin gaskiya da yin aiki da ita. Kuma dukkan batacce 'Dan bidi'a ya saba wa hakan.

Kuma surar ta kunshi tsarkake addini ga Allah Ta'alah, ta bangaren dukkan ibada da neman taimako, a cikin fadinSa: **"A kai kadai muke bauta, kuma a gare ka muke neman taimako".**

Don haka, Godiya ta tabbata ga Allah, Ubangijin Talikai.

# TAFSIRIN *'AYATUL KURSIY'*

**"Allah babu wani abin bautawa da gaskiya face shi, Rayayye Tsayayye Mai tsayar da komai, Gyangyadi baya kama shi, haka barci. Nasa ne abinda ke cikin sammai da abinda ke cikin kassai. Babu mai ceto a wurinSa face da izininSa. Ya san abinda ke gaba gare su, da wanda yake bayansu. Kuma basu kewaye da komai daga iliminSa, face da abinda ya so. Girman KursiyyinSa ya yalwaci sammai da kasa. Kuma tsare su baya zama mai nauyi a gare shi. Kuma shine Madaukaki Mai girma". (Bakara: 255)**

(255) Manzon Allah –S.A.W- ya bamu labarin cewa, lallai wannan ayar ita ce ayar da tafi girma a cikin Alkur'ani, saboda abinda ta kunsa na ma'anonin Tauhidi, da girma da fadin sifofin Makagi; Allah Ta'alah; Saboda shine "Allah": Wato, wanda yake da dukkan ma'anoni na cancantar bauta (Uluhiyyah); don haka babu wanda ya cancanci a masa bauta idan ba Allah ba, kuma yin bauta ga waninsa barna ne. Kuma Allah shine "Al-Hayy" : Wato, wanda yake da dukkan ma'anonin cikakkiyar rayuwa, na ji da gani da iko da nufi da sauran sifofin zati. Kamar yadda Allah shine "Al-Qayyum" wannan sunan dukkan sifofin aiki za su shiga cikinsa; saboda shine tsayayye da-kansa; wanda ya wadata daga dukkan halittunsa, kuma ya tsayar da dukkan samammun abubuwa; ta hanyar samar da su, da wanzar da su, da kuma basu dukkan abinda sai sun same su gabanin samuwarsu da wanzuwarsu. Kuma yana daga cikin kamalar rayuwar Allah da tsayuwarsa, kasancewarsa:

"Gyangyadi baya kama shi haka kuma barci". Domin gyangyadi da barci suna bijirowa ne ga Halitta, wanda rauni yake samunsu da gajiyawa da karewa. Kuma wadannan basu bijiro wa Ma'abocin girma da daraja.

Kuma ya bada labari cewa, shine Mamallakin dukkan abinda yake cikin sammai da kasa, kuma dukkansu bayi ne, mallakan Allah; babu wani daga cikinsu da yake iya fita daga wannan matsayi "Dukkan wadanda suke cikin sammai da kasa, babu wani face ya zo wa Mai rahama a matsayin Bawa" (19:93). Don haka, Shine ya mallaki dukkan abin mallaka, kuma shine yake da sifar mulki da juya lamura da iko da girma.

Kuma yana cikin cikar mulkinsa, kasancewarsa babu wani da zai yi ceto a wurin Allah face da izininsa; saboda dukkan masu wani matsayi da masu yin ceto bayinsa ne mallakarsa; ba za su iya wata ceto ba sai bayan ya musu izini: "Ka ce: Ceton gaba dayansa na Allah ne, saboda mallakar abinda ke cikin sammai da kasa nasa ne…" (39:44). Kuma Allah ba zai yi izinin ayi ceto ga wani ba, sai ga wanda ya yarda, kuma ba zai yarda ba, face da Tauhidinsa da bin Annabawansa, don haka duk wanda bai siffantu da wannan ba, bashi da rabo cikin samun ceto.

Sai kuma Allah ya bada labarin iliminsa mai yalwar fadi da gamewa, da cewar, Yana sanin abinda ke gaban halittu na al'amurran da ake fiskanta, wadanda basu da iyaka, "da kuma abinda ke bayansu", na al'amurran da suka shude, wadanda basu da iyaka, kuma lallai shi babu abinda yake iya buya a gare shi: "Yana sanin idanu masu ha'inci da abinda kiraza suke boyewa" (40:19).

Kuma lallai halittu gaba dayansu babu wani da yake kewaye da ilimin Allah da ababen da ya sani, "**sai da abinda ya so**", daga cikinsu, na al'amurran shari'a da kaddara wadanda ya tsinkayar da su iliminsu. Wanda kuma bangare ne dan kadan; wanda ba komai ba a cikin ilimin Allah.

Kamar yadda Halittun da suka fi sanin Allah; wato Manzanni da Mala'iku suka fada:

"Tsarki ya tabbata a gare ka, Bamu da wani ilimi face wanda ka ilmantar da mu" (2:32).

Sai Allah ya bada labarin girmansa, da cewa **"Kursiyyunsa ya yalwaci sammai da kasa"**, kuma Allah yana kiyaye su da abinda ke cikinsu na halittu, da sabubba da kuma tsare-tsare wanda Allah ya sanya su a cikin halittu, amma tare da hakan, kiyaye su baya masa nauyi, saboda kamalar girmansa da ikonsa da yalwar hikimarsa a cikin hukunce-hukuncensa. "**Kuma shine Madaukaki**" da zatinsa, akan dukkan Halittunsa, saboda shine madaukaki da girman sifofinsa, kuma shine madaukaki wanda ya rinjayi halittunsa, kuma suke kankan da kai a gare shi.

Kuma shine "**Mai girma**": saboda shine ya hade dukkan sifofin girma da daukaka wanda zukata suke sonsu, kuma rayuka suke girmama su.

Kuma masana sun san cewa: lallai girman kowane abu, koda yafi karfin a sifanta shi, to lallai kamar babu ne idan aka danganta shi da girman Madaukaki Mai girma (Allah).

Don haka ayar da take dauke da wadannan ma'anonin, wadanda kuma sune mafi girman ma'anoni, lallai hakkinta ne ta kasance ayar da tafi dukkan ayoyin Alkur'ani girma, Kuma ya dace ga wanda ya karanta wannan ayar da tadabburi da kokarin fahimtarta, zuciyarsa ta cika da yakini da ilimi da imani. Kuma ya kasance abin kiyayewa daga sharrace-sharracen Shaidan.

## [TAFSIRIN SURATUL *'ZALZALAH'* WANDA TA SAUKA A MADINAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai, 1. Idan aka girgiza kasa girgizawa. 2. Kuma kasa ta fitar da kayanta masu nauyi. 3. Kuma Mutum ya ce: Menene ya same ta?!' 4. A ranar nan, za ta fadi labarinta 5. Saboda ta samu umurni daga Ubangijinka. 6. A wannan ranar, Mutune za su fito daban-daban domin a nuna musu ayyukansu. 7. Saidai wanda ya aikata aiki gwargwadon nauyin zarra na alheri zai gan shi. 8. Kuma wanda ya aikata gwargwadon nauyin zarra na sharri, zai gan shi.**

---

**(1-2)** Allah yana bada labarin abubuwan da za su kasance a ranar kiyamah, da cewa lallai kasa za a girgiza ta har sai abinda yake kanta na dukkan gini da alamomi sun fadi, sai duwatsunta su ramarmashe, a daidaita tuddanta, su kasance fako mai santsi, wanda babu karkata a cikinsa kuma babu wani tudu, **"Sai kasa ta fitar da abinda ke cikinta masu nauyi"** na matattun halittu da taskoki.

**(3) "Sai Mutum ya ce"** idan ya ga abinda ya zo mata na wannan lamari mai girma; cikin firgici da ganin girman hakan: **"Me nene ya same ta?"** me yake faruwa ga kasa?!

**(4-5) "A wannan ranar"** lallai **"zata amayar da dukkan labarunta"** saboda zata yi shaida ga masu aiki akan ayyukan da suka aikata na alheri da sharri akan kasa. Kasancewar itama kasa tana daga jerin shaidun da za su yi shaida ga Bayi akan ayyukansu.

Wannan kuma **"saboda Ubangijinka ya mata wahayi"** wato ya bata umurnin ta bada labarin abinda aka aikata akanta; saboda haka ba za ta saba wa umurninsa ba.

**(6)** "A ranar, Mutane za su fito" daga filin kiyama a lokacin da Allah yake hukunci a tsakaninsu, "daban-daban" jama'a-jama'a wani sama da wani "domin a nuna musu ayyukansu" wato, domin Allah ya nuna musu abinda suka aikata munana da kyawawa, kuma ya nuna musu sakamakonsu a cike.

**(7-8)** "Lallai, wanda ya aikata gwargwadon nauyin zarra, na alheri zai gan shi. Wanda ya aikata gwargwadon nauyin zarra na sharri, zai gan shi" Wannan kuma ya kunshi alheri da sharri dukkansu; saboda idan ba a boye masa daidai da kwayar zarra - wanda shine mafi karancin abu-; Mutum ya ga abunsa, aka masa sakayya akansa, to abinda yake sama da haka ta fiskar girma, shine mafi cancantar hakan, kamar yadda Allah Ta'alah yake cewa: "Ranar da kowace rai zata samu abinda ta aikata na alheri a halarce, shi kuma abinda ta aikata mummuna zata yi fatan da a tsakaninta da tsakaninsa akwai tafiya mai nisa". "Kuma suka samu abinda suka aikata a halarce" (3:30).

Wannan ayoyi biyu a cikinsu akwai kwadaitarwa kan aikata alheri koda kadan ne, da kuma tsawatarwa kan aikata sharri, koda kadan ne.

**[TAFSIRIN SURATUL *'ADIYAAT'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]**

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Ina rantsuwa da dawaki masu gudu suna fitar da kukan ciki. 2. Masu kyasta wuta (da kofatonsu) kunnawa. 3. Sa'annan masu yin hari a lokacin asuba. 4. Sai su tayar da kura saboda hakan. 5. Sai su shigar da kurar a cikin jama'ar makiya.**

**6. Lallai ne Mutum mai tsananin butulci ne ga UbangijinSa. 7. Lallai ne shi mai shaida ne akan laifinsa. 8. Kuma lallai ne ga dukiya mai tsananin so ne. 9. Shin, ba shi da sanin lokacin da ake tone abinda yake cikin kaburbura?! 10. Aka bayyana abinda ke cikin zukata. 11. Lallai ne Ubangijinsu, game da su, a ranar nan, Mai kididdigewa ne?**

**(1)** Allah Tabaraka wa Ta'alah ya yi rantsuwa da dawakai, saboda abinda yake cikinsu na ayoyinSa manya, da ni'imominSa da suke bayyane ga halittu. Kuma ya yi rantsuwar ne da su, a cikin halinsu wanda sauran dabbobi basu yin tarayya da su, a cikin fadinsa: " Ina rantsuwa da dawakai masu gudu suna fitar da kukan ciki" wato, masu gudu mai tsanani, wanda yake fitar da irin wannan sauti, saboda "Dab,hu" sautin numfashin dawakai ne daga kirjinsu, a lokacin da gudunsu yake tsananta.

**(2)** "Masu kyasta wuta" da kofatonsu ga abinda suka taka na duwatsu, sai wuta ta rika fita saboda kwarin kofatonsu da karfin gudunsu.

**(3)** "Masu kai hari" ga Makiya "a lokacin asuba", ga mafi rinjaye, wato harinsu ya kan kasance da asuba.

**(4-5)** "Sai su rika tayar da kura" saboda masifar gudun kai hari, "Sai su shigar da kurar a tsakanin jama'ar makiya" wadanda suke kai musu hari.

**(6)** Abinda aka yi rantsuwa akansa shine fadinsa "Tabbas, Mutum mai tsananin butulci ne ga UbangijinSa" "Kanud", ma'anarsa shine: mai hana alherin da Allah ya yi masa, saboda dabi'ar da aka halicci Mutum ita ce, lallai ransa bata bayar da hakkokin da suke kanta a cike, dabi'arta shine

kasala, da kokarin hana hakkokin da suka ta'allaka da dukiya da na jiki. Sai wanda Allah ya shiryar da shi, ya fita daga wannan dabi'ar zuwa ga dabi'ar bayar da hakkoki.

**(7)** "Lallai ne shi mai shaida ne da haka akan laifinsa", wato, Mutum akan abinda ya sani na dabi'ar ransa ta rowa da hani, mai yin shaida ne; bai isa ya yi musun hakan ba, saboda abu ne a bayyane a fili. Za a iya fassara lamirin suna "Shi (wato Allah) mai yin shaida ne akan hakan". Ma'ana: Allah mai yin shaida ne akan rowar Mutum, Wannan kuma tsawatarwa ne ga mai rowa da nuna masa Allah ya san halin da yake ciki.

**(8)** "Kuma lallai shi" wato, Mutum "Ga son alheri –wato dukiya- mai tsanani ne"" mai yawan son dukiya, kuma son da yake masa shine yake jagorantarsa ga barin bayar da hakkoki na wajibin da suke kansa, sai yake fifita sha'awar ransa akan yardar UbangijinSa. Wannan kuma saboda Mutum ya takaice ganinsa ne ga wannan gidan (Duniya), ya rafkana ya gafala daga gidan Lahira.

**(9-10)** Wannan ya sanya, Allah ya ce, alhalin yana kwadaitar da shi kan ranar alkawari, "Shin bai sani ba" to wannan rudadden ya san "Idan aka tone abinda ke cikin kaburbura" wato Allah ya fitar da matattu daga kabarinsu ya tattaro su "Kuma aka bayyana abinda ke cikin zukata" …

Sai abinda ya buya a cikinsu na alheri da sharri ya bayyana, sai sirri ya zama a fili, badini kuma ya komo zahiri, sai sakamakon ayyukan halittu ya bayyana a fiskokinsu.

**(11) "Lallai ne Ubangijinsu, game da su, a ranar nan, Mai kididdigewa ne"** ma'ana: ya san ayyukansu na zahiri da badini, da wadanda suka buya da bayyanannu, kuma zai musu sakayya akansu. Kuma ya kebe ranar kiyama da cewa zai basu labari akansu tare da cewa, shi mai bada labari ne akansu a kowane lokaci, saboda muradin shine, zai yi sakayya akan ayyukan da Allah ya riga ya sansu.

## [TAFSIRIN SURATUL *'KARI'AH'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Mai kwankwasar zukata da tsoro. 2. Menene mai kwankwasa? 3. Kuma me ya sanar da kai abinda ake ce wa mai kwankwasa? 4. Ranar da Mutane za su kasance kamar 'ya'yan fari masu watsuwa, 5. Kuma duwatsu su kasance kamar gashin da aka sabe, 6. To, amma wanda ma'aunansa suka yi nauyi (da kyawawan aiki), 7. Shi yana cikin rayuwa yardadda. 8. Amma wanda ma'aunansa suka yi rashin nauyi, 9. To, Uwarsa ce Hawiyah. 10. Kuma me ya sanar da kai menene ita? 11. Wata wuta ce mai zafi!**

**(1-3)** "Mai kwankwasa" yana daga cikin sunayen ranar kiyama. An sanya mata (Alkari'ah) saboda kwankwasar Mutane, tana kuma firgitar da su da abubuwan da suke aukuwa a cikinta. Da wannan dalilin Allah ya girmama sha'aninta, da tambayar da ya gabatar, "Mene ne mai kwankwasa? 3. Kuma me ya sanar da kai abinda ake ce wa mai kwankwasa?". **(4) "Ranar da Mutane suke kasancewa..."**, saboda tsananin firgici da tashin hankali, **"kamar 'ya'yan fari masu watsuwa**", wato kamar 'ya'yan fari a cikin dare wadanda sashensu suke cakuda da sashe; basu san ina za su fiskanta ba, idan kuma aka kunna musu wuta sai suyi ta cincirindo akanta, saboda raunin hankalinsu, To irin wannan shine halin Mutane ma'abota hankula (a ranar kiyama).

**(5)** Amma su kuma kuramen duwatsu manya, sai su kasance **kamar gashin sufin da aka sabe**" sai ya zama da rauni, ta yadda kowace iska zata iya wurgi da shi. Allah Ta'alah ya ce: "Kuma kana ganin duwatsu, kana zatonsu sandararru, alhali suna tafiya irin na girgije" (27:88). Sa'annan bayan haka sai a mayar da su kamar kura abar shekewa, sai duwatsun su tafi; babu wani abu da za a gani a cikinsu da zai saura. To, a lokacin za a kafa ma'aunan ayyuka, sai Mutane su kasu kashi biyu; Masu rabo da shakiyyai;

**(6-7) To, amma wanda ma'aunansa suka yi nauyi**," wato, kyawawan ayyukansa suka rinjayi munanansa **"To, shi yana a cikin wata rayuwa yardadda"** a cikin Aljannonin ni'ima.

**(8-11) "Amma wanda ma'aunansa suka yi sako-sako (babu nauyi)"**, kasancewar kyawawan ayyukansu basu kai munanan ba **"To, uwarsa Hawiya ce"**, ma'ana: makomarsa da mazauninsa itace Wuta, wanda cikin sunayenta: Hawiya. Wutar zata kasance masa, kamar uwar da take lazimtarsa, "Lallai azabarta ta kasance mai lazimta" (25:65). Wasu suka ce: Ma'anar wannan, Uwar kwakwalwarsa zata fara kasancewa a cikin Wuta, wato za a jefa shi cikin wuta da kansa. **"Me ya sanar da kai, mecece ita?"**" Wannan tambaya ce domin girmama al'amarinta, Sa'annan sai ya amsa da cewa: **"Wuta ce mai kuna"**, mai tsananin zafi, zafinta yafi Wutar Duniya da fiye da ninki saba'in. Muna neman tsarin Allah daga gare ta.

## [TAFSIRIN SURATUT *'TAKASUR'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Alfaharinku da yawa ya shagaltar da ku (daga ibada). 2. Har kuka ziyarci kaburbura. 3. A'aha! Kusa-kusa zaku sani. 4. Sa'annan tabbas da sannu za ku sani. 5. Hakika da kuna da sani, sani na yakini. 6. Lallai, da kun ga wutar Jahimu.**
**7. Sa'annan lallai za ku ganta da idanu, a bayyane. 8. Sa'annan lallai ne za a tambaye ku, a ranar nan, dangane da ni'imomi.**

**(1)** Allah Ta'alah ya kausasa lafazi ga BayinSa wadanda suka bar abinda aka halitta su dominsa; na bautar Allah shi kadai, da al'amarin saninSa da mayar da lamari gare shi, da fifita soyayyarSa akan son komai, a in da ya ce: "**Ya halakar da ku**" daga abinda aka ambata, "**Alfaharin yawa**" Amma sai bai ambaci abinda suke alfaharin da shi ba, domin hakan ya bada

daman shigan dukkan abinda masu alfahari suke alfaharin da shi; na yawan dukiya, da 'ya'ya, da mataimaka, da rundunoni, da hadimai, da wanin wannan daga cikin abinda masu alfaharin yawa, dayansu ya kan ji yafi wasu, kuma ba suna jin hakan da nufin Allah ne ba.

**(2)** Sai gafalarku da warginku da shagaltuwarku ta cigaba **"Har kuka ziyarci kaburbura"**, to a lokacin ne rufin da ke kwakwalenku ya yaye! Saidai kuma a lokacin, babu wani abu wanda za ku iya. Fadinsa kuma: **"Har kuka ziyarci kaburbura"** ya nuna cewa lallai *Barzakhu*, wato rayuwar kabari, gida ne wanda manufarta shine tsallakawa zuwa gidan Lahira; saboda Allah a al'amarin makabartai ya kira su da suna: masu ziyara, bai kira su da wadanda za su zauna ba, sai wannan ya nuna cewa, lallai tayarwa da sakamako akan ayyuka, za su kasance ne a gida mai wanzuwa (Lahira); ba a gidan da zata kare ba.

**(3-6)** Wannan ne kuma ya sanya Allah ya fadi narkonsa akansu; ya ce: **"A'aha! Kusa-kusa zaku sani. * Sa'annan tabbas da sannu za ku sani. * Hakika da kuna da sani, sani na yakini. * Lallai, da kun ga wutar jahimu"** wato; Da kun san abinda yake gabanku ilimin da yake kaiwa zukata, to da alfari da yawanku bai shagalar da ku ba, kuma da kun yi ta gaggawar aikata ayyukan kwarai. Sai dai rashin ilimi na hakika shine ya kaiku ga abinda kuke gani, **"Lallai, da kun ga wutar Jahimu"**, Ma'ana: Lallai za ku ga kiyama, kuma lallai za ku ga wutar Jahimu wanda Allah ya yi tanadinta ga Kafirai.

**(7)** "Sa'annan lallai za ku ga wutar da idanu, a bayyane", gani irin na idanu a zahiri, kamar yadda Allah Ta'alah ya ce: "*Kuma mujrimai suka ga Wuta, sai suka tabbatar cewa za su fada cikinta, kuma basu da hanyar kauce mata*" (18:53).

**(8)** "Sa'annan lallai ne za a tambaye ku, a ranar nan, dangane da

ni'imomi", wato, wanda kuka ni'imtu da su a gidan Duniya; a ce: Shin kun tsayu wajen gode masa, kuma kun bayar da hakkin Allah a cikinsu, kuma baku yi amfani da ni'imomin cikin sabonSa ba, Sai Allah ya baku wasu ni'imomin da suka fi daukaka, kuma suka fi falala? Ko kun rudu da ni'imomin, sannan baku tsayu da godiyarsu ba, ko kuma a wasu lokutan kun yi amfani da su cikin sabo, sai Allah ya muku ukuba akan hakan?

Allah Ta'alah ya ce: "*Kuma a ranar da za a bijiro da Kafirai ga Wuta, (a ce musu:) kun tafiyar da dadinku, a cikin rayuwarku ta Duniya, kuma kun nemi jin dadi da su, to a yau za a saka muku da azabar wulakanci…*"(46:20), har karshen ayar.

## [TAFSIRIN SURATUL *'ASR'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Ina rantsuwa da zamani! 2. Lallai ne Mutum yana cikin hasara. 3. Face wadanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan kwarai, kuma suka yi wa juna wasiyya da bin gaskiya, kuma suka yi wa juna wasiyya da yin hakuri (su kam basu cikin hasara) .**

**(1-3)** Allah Ta'alah ya rantse da zamani wanda shine dare da yini, kuma lokacin da Bayi suke yin aiki a cikinsa, cewa kowane Mutum ya yi hasara, shi kuma mai hasara kishiyan wanda ya samu riba ne, kuma asarar mataki-mataki ne mabanbanta, zai iya kasancewa asara ne gamamme ta kowace fiska, irin halin wanda ya yi asarar Duniya da Lahira, kuma ya rasa shiga ni'ima, kuma ya cancanci shiga wuta. Kuma zai iya kasancewa ya yi asara ne ta wasu fiskoki banda wasu, Wannan kuma shi ya sanya Allah ya game dukkan Mutum da sifanta su da asara, in banda wanda ya sifanta da sifofi guda hudu:

- **Imani** da abinda Allah ya bada umurnin ayi imani da su, Saidai imani baya kasancewa idan babu ilimi, don haka: ilimi reshe ne na imani; baya cika face da shi.

- **Aiki na kwarai,** wannan kuma ya game dukkan ayyukan alkhairi; na zahiri da boye, wanda suke da alaka da hakkokin Allah ko kuma hakkokin Bayi, na wajibi, da mustahabbi.
- **Wasici da gaskiya;** wanda shi ne, wasiyya da imani da kuma aiki na kwarai; sai sashe ya rika wasiya ga sashe da aikata hakan, yana kwadaitar da shi akan hakan.
- Sai kuma sashe ya rika wasiyya ga sashe akan hakurin biyayya ga Allah, da nisantar saba masa, da kuma hakuri akan abinda Allah ya kaddara, masu zogi. Kuma da al'amuran farko guda biyu Mutum zai samu kamala a ransa, da kuma biyun karshe zai yi kokari domin wasu su samu kamala. Kuma da cika al'amuran ne guda hudu Bawa zai kasance ya kubuta daga asara, ya kuma rabauta da samun rabo mai girma.

## [TAFSIRIN SURATUL *'HUMAZAH'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Bone ya tabbata ga duk mai nune, mai zunde (rada), 2. Wanda ya tara dukiya, kuma ya mayar da ita abar tattalawa, 3. Yana zaton cewa dukiyarsa zata dawwamar da shi! 4. A'aha! Lallai ne za a jefa shi a cikin Hudama. 5. Me ya sanar da kai abinda ake ce wa Hudama? 6. Wutar Allah ce wanda ake hurawa,
7. Wanda take lekawa akan zukata. 8. Lallai ne ita abar kullewa ce akansu, 9. A cikin wasu ginshikai mikakku.**

**(1) "Wailun",** wato narko, da bone da tsananin azaba **"ya tabbata ga duk mai nune, mai rada"**, wato, wanda yake aibanta Mutane da aikinsa, yake kuma zaginsu da zancensa. Saboda *Hammaz* shine yake aibanta Mutane yana sukansu ta hanyar nuni da aiki, Shi kuma *Lammaz* shine wanda yake aibanta su da zancensa.

**(2)** Yana daga cikin sifar wannan Mai nune mai zunde kasancewar bashi da wata damuwa face tattara dukiya, da tattalata da alfahari da ita, kuma bashi

da kwadayin ciyar da ita a hanyoyin alheri da sadar da zumunci da makamantan haka.

**(3) "Yana zato"**, da jahilcinsa **"lallai dukiyarsa zata dawwamar da shi"** a wannan Duniyar. Kuma don haka ne, wahalarsa da aikinsa gaba daya suka kasance kan bunkasa dukiyarsa, wanda yake zaton zata bunkasa rayuwarsa, alhalin bai san cewa, rowa tana ruguza rayuwa tana rusa gidaje ba, kuma bai san kyauta da sadar da zumunci su kuma suna kara tsare da bunkasa rayuwa ba.

**4-7)** " A'aha! Lallai ne za a jefa shi a cikin Hudama. * Me ya sanar da kai abinda ake ce wa Hudama?" Wannan tambayar domin girmama lamarin Wutar ne, da kuma tsoratarwa kan sha'aninta. Sa'annan sai ya fassara ta, da fadinSa: "Wutar Allah ce wanda ake hurawa", wanda kuma makamashinta sune Mutane da duwatsu, kuma yana daga cikin tsananinta "lallai tana lekawa akan zukata"; wato tana zarcewa daga jiki izuwa zuciya.

(8-9) Tare da irin wannan matsanancin zafi, su za a kulle su a cikinta; ta yadda za su debe tsammani daga ficewa daga cikinta, wannan ya sanya Allah ya ce: " Lallai ne ita abar kullewa ce akansu", wato an rurrufe su, "A cikin wasu ginshikai" ta bayan kofofinta "mikakku" wannan kuma domin kada su fice daga cikinta; "Duk lokacin da suka yi nufin ficewa daga cikinta, sai a dawo da su cikinta" (32: 20). Muna neman tsarin Allah daga shiga Wuta, kuma muna rokonsa afuwa da lafiya.

**[TAFSIRIN SURATUL '*FIL*' WANDA TA SAUKA A MAKKAH]**

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Ashe ba ka ga yadda Ubangijinka ya aikata da Ma'abutan rundunar giwa ba? 2. Ashe bai sanya kaidinsu cikin bata ba? 3. Sai ya saukar akansu da rundunar tsuntsaye jama'a-jama'a, 4. Suna jifansu da wasu duwatsu na yunbun Wuta 5. Sai ya sanya su kamar karmami wanda aka cinye.**

**(1-5)** Ashe baka ga kudurar Allah da girman sha'aninSa, da rahamarSa ga BayinSa,da dalilan kadaita shi, da gaskiyar manzancin ManzonSa Muhammaduﷺ irin abinda Ubangijinka ya aikata **"da mayakan da suke akan giwaye"** wadanda suka kulla makirci ga dakinsa mai alfarma, da kudurin rusa shi, kuma suka gama shirinsu domin zartar da hakan, su ka zo da giwaye a tattare da su, domin rushe shi, a cikin dinbin tawagar da Larabawa ba za su iya ja da su ba, su ka zo daga kasar Habasha da Yaman. Kuma a lokacin da suka zo kusa da garin Makkah, alhalin Larabawa basu da karfin da za su iya tinkararsu, sai Mutanen Makkah suka fice daga cikin Makkan, saboda tsoronsu. Sai Allah **"ya aike musu rundunar tsuntsaye jama'a-jama'a",** wasu bayan wasu, suna dauke da duwatsun da aka babbaka su da wutar sijjil, sai suke jifansu da su; suna binsu na nesa da na kusa, suka yi laga- laga da su, suka zubar da su, sannan suka karkashe su, **"su ka mayar da su kamar karmami wanda aka cinye".** Allah ya ruguza sharrinsu, ya mayar da kaidinsu a gare su. Kissarsu sananna ce wanda ta shahara. Kuma wannan lamarin ya auku ne a shekarar da aka haifi Ma'aikin Allah sai ta kasance daya daga cikin mu'ujizozin da'awarsa, da kuma dalilai kan manzancinsa. Yabo da godiya duka na Allah ne.

## [TAFSIRIN SURATUL *KURAISH* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Saboda sabawar Kuraishawa 2. Sabonsu na tafiyar hunturu da ta bazara 3. Saboda haka sai su bauta wa Ubangijin wannan daki (Ka'abah) 4. Wanda ya ciyar da su daga yunwa, kuma ya amintar da su daga tsoro.**

**(1-4)** Malaman tafsiri dayawa sun ce: Lallai kalmar "jari da majruri" (a farkon ayar Li iylafi) ta ta'allaku ne da surar da ta gabace ta (surar rundunar giwaye), Ma'ana: Mun aikata abinda muka aikata ne da rundunar giwaye, saboda Kuraishawa; da lamarin amincinsu, da tsayuwar maslahohinsu, da cigaban bulaguronsu zuwa Yaman a lokacin sanyi, da kuma zuwa Sham a lokacin zafi saboda kasuwanci da neman kudi. Sai Allah ya halakar da wanda ya nufi Kuraishawa da mummuna, ya kuma girmama al'amarin harami da Ma'abutansa a zukatan sauran Larabawa; sai suke girmama su, ba su kange su daga dukkan bulaguron da suka yi nufin yi, don haka ne Allah ya umurce su da yin godiya a gare shi, a inda ya ce:
**"Sai su bauta wa Ubangijin wannan dakin (Ka'aba)"**, wato, su kadaita shi, su kuma tsantsanta nufin bauta a gare shi. **"Wanda ya ciyar da su daga yunwa, kuma ya amintar da su daga tsoro"**, domin warwalar arziki, da amintuwa daga tsoro lamura ne guda biyu daga cikin manyan ni'imomi ta bangaren Duniya, wadanda suke hukunta a yi godiya ga Allah Ta'alah. Don haka, yabo da godiya sun tabbata ga Allah akan ni'imominSa na zahiri da badini. Kuma Allah ya kebe rububiyyarSa ga dakinSa ne, domin falalar dakin da matsayinsa, tare da cewa shine Ubangijin kowane abu.

## [TAFSIRIN SURATUL *'MA'UNA'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Shin ba ka ga wanda yake karyata sakamako (addini) ba 2. To wannan shine wanda yake tunkude Maraya (daga hakkinsu), 3. Kuma baya kwadaitarwa bisa ga bayar da abinci ga matalauci. 4. To bone ya tabbata ga Masallata 5. Wadanda suke masu shagala daga sallarsu 6. Wadanda suke yin riya ga ayyukansu 7. Kuma suke hana taimako.**

**(1)** Allah Ta'alah, yana fada alhalin yana zargin wanda ya ke kin bayar da hakkokinSa, da cinye hakkokin bayinSa: "Shin ba ka ga wanda yake karyata sakamako ba", wato, yake karyata akwai sakamako, kuma baya imani da abinda Manzanni suka zo da shi.

**(2)** "To irin wannan shine yake tunkude Maraya (daga hakkinsa)" ma'ana, yake tunkude shi da tsanani; baya tausayinsa. Saboda kaikashewar zuciyarsa, kuma saboda baya fatan wani lada, kuma baya tsoron wata ukuba.

**(3)** "Kuma baya kwadaitar" da wasu "bisa ga bayar da abinci ga matalauci", Kuma tun da ba ya kwadaitar da wasu, to shi yafi cancantar ya zamto baya ciyar da Miskinin!

**(4-5)** "Bone ya tabbata ga Masallata" masu yinta, saidai "sune masu shagala daga sallarsu" wato, suna tozarta ta, suna fitar da ita daga lokatanta, suna tauye rukunnanta. Wannan kuma saboda rashin muhimmantar da al'amarin Allah, saboda sun tozarta sallah wanda ita ce, aikin biyayya wanda yafi muhimmanci; Kuma lallai shagala daga sallah, Ma'abucinsa ya cancanci aibantawa da zargi. Yayin da shi kuma yin mantuwa a cikin sallah yana iya aukuwa daga kowa, har ma daga Annabi –sallal Lahu alaihi wa sallama-.

(6-7) Wannan ya sanya Allah ya sifanta wadannan da, riya, da kaikashewar zuciya da rashin taimako, ya ce: "Wadanda suke yin riya ga ayyukansu"

wato, suna aiwatar da ayyukansu ne don Mutane su gani, "Kuma suna hana taimako" ma'ana, suna kin bayar da abinda bayar da shi ba zai cutar da su ba, ta hanyar aro ko kyauta, kamar kofi, guga, fartanya da makamancin abinda a al'adance ana bayar da shi. Wadannan -saboda tsananin rowarsu- suna hana aro, To yaya kuma abinda yafi hakan!

A cikin wannan surar, akwai kwadaitarwa kan ciyar da Maraya da talakawa, da zaburarwa akan hakan, da kula da sallah da kiyaye ta, da tsarkake niyya a cikinta da kuma a cikin sauran ayyuka, da kwadaitarwa kan ayyukan jin-kai, da bayar da kananan abubuwa, kamar aron kwano da guga da littafi da makamancin haka, domin Allah ya zargi wanda baya aikata hakan. Allah shine mafi sani.

## [TAFSIRIN SURATUL *'KAUSAR'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Lallai ne mun yi maka kyauta mai yawa (tafkin Alkausar). 2. Sai, ka yi sallah ga Ubangijinka, kuma ka yi baiko (sukan rakumi). 3. Lallai ne mai aibanta ka, shine mai yankakkiyar albarka.**

(1) Allah Ta'alah yana fada wa Annabinsa Muhammadu ﷺ - alhalin yana ambaton ni'imarSa akansa: "Lallai ne mun yi maka kyauta mai yawa (tafkin Alkausar)"; ma'ana: alheri mai yawa da falala dayawa, wanda a cikinsa akwai abinda Allah zai baiwa AnnabinSa – ﷺ ranar kiyama, na tafkin da ake kira da *Al-Kausar, da kuma dausayi (Haud) wanda* tsawonsa shine kimanin tafiyar wata guda, fadinsa tafiyar wata, ruwansa kalansa yafi nono tsananin haske, yafi zuma zaki, kofunansa gwargwadon adadin taurarin sama; wato ta fiskar yawa da haske; Wanda ya sha sau daya daga tafkin, har abada ba zai sake jin kishi ba!

(2) Da ya ambaci ni'imarSa akansa, sai kuma ya umurce shi da gode masa, a inda ya ce: "Sai, ka yi sallah ga Ubangijinka, kuma ka yi baiko (sukan rakumi)". Allah ya kebance ibadodin nan guda biyu da ambato, saboda sallah da yanka sune mafi girman ibada da fifiko. Kuma saboda sallah tana kunsar rusunawa ga Allah a cikin zuciya da sauran gabbai, kuma tana daukar Bawa zuwa ga sauran nau'ukan bauta. A cikin ibadar soke rakumi kuma akwai kusantar Allah da mafificin abinda yake wurin Bawa na ababen sokewa, kuma akwai fitar da dukiya wanda aka dabi'antar da rai kan sonta, da kin bayar da ita.

(3) "Lallai ne mai aibanta ka", wato makiyinka, mai sukarka, da aibanta ka "hakika shine mai yankakkiyar albarka", ma'ana: shine aka yanke shi daga dukkan alheri, shine aka yanke shi daga aiki, aka yanke shi daga kyakkyawan ambato. Amma annabi Muhammadu – ﷺ - to lallai shine kammalallen Mutum na hakika; wanda yake da dukkan kamalar da zata iya samuwa ga halitta, na daukaka ambatonsa da yawan mataimaka da mabiya –ﷺ-.

## [TAFSIRIN SURATUL *'KAFIRUNA'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. K ace: Ya ku kafirai! 2. Ba zan bauta wa abinda kuke bautawa ba. 3. Kuma ku ba ku zama masu bauta ga abinda nake bautawa ba . 4. Kuma ni ba zan bauta wa abinda kuke bautawa ba 5. Kuma ku ba ku zama masu bauta wa abinda nake bautawa ba. 6. Addininku na gare ku, nima addinna yana gare ni".**

**(1-6)** Ma'ana: Ka gaya wa kafirai, a bude kuma a fili, cewa: "Ba zan bauta wa abinda kuke bautawa ba" wato, ina mai barranta daga abinda suke bautawa koma bayan Allah a zahiri da badini. "Kuma ku ba ku zama masu bauta wa abinda nake bautawa ba" saboda baku tsarkake Allah a cikin bautarsa, don haka bautarku da ta hadu shirka ga Allah ba a kiranta bauta. Kuma Allah ya maimaita wannan jumlar, domin na farkon ya nuna rashin

samuwar aikin, na biyun kuma ya nuna cewa hakan ya zama sifa tabbatacciya. Kuma wannan ya sanya Allah ya rarrabe tsakanin bangarori biyun, ya sanya shamaki a tsakaninsu, ya ce: "Addininku na gare ku, kuma addinina yana gare ni". Daidai da fadin Allah Ta'alah: "Ka ce: Kowa yana aiki ne akan hanyarsa" (17:84); Lallai kun barranta daga abinda nake aikatawa, kuma nima na barranta daga abinda kuke aikatawa.

**[TAFSIRIN SURATUN *'NASR'* WANDA TA SAUKA A MADINAH]**

Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Idan taimakon Allah ya zo, da kuma cin nasara, 2. Kuma ka ga Mutane suna shiga addinin Allah jama'a-jama'a, 3. To, ka yi tasbihi, gami da gode wa Ubangijinka, kuma ka nemi gafararSa, Lallai shi ya kasance Mai yawan karbar tuba ne.

**(1-3)** A cikin wannan sura mai karamci akwai, bushara, da kuma umurni ga Manzon Allah a lokacin samun busharar, da kuma ishara da fadakarwa akan abinda zai ratayu da hakan.

Ita busharar ita ce bushara da cewa Allah zai bada nasara ga ManzonSa, zai bude masa garin Makkah, da al'amarin shigan Mutane "cikin addinin Allah jama'a-jama'a" ta yadda yawancinsu za su kasance cikin iyalansa da mataimakansa, bayan a farko sun kasance cikin makiyansa, kuma hakika abinda aka masa ya auku. Shi kuma umurnin da aka masa bayan samun nasara da bude Makkah, shine Allah ya umurci ManzonSa da cewar ya gode masa akan hakan, kuma ya yi tasbihi tare da gode masa, yana mai neman gafararSa.

Dangane da isharar kuma, akan wannan akwai isharori biyu: Na farkon shine nuni cewa lallai nasara zata cigaba da samuwa ga wannan addinin kuma zata rika karuwa a lokacin da Manzon Allah SAW yake yin tasbihi yana gode ma Allah yana neman gafararSa. Domin yin hakan yana cikin godiya, kuma Allah yana cewa: *"Lallai idan kuka gode, to hakika zan kara muku"*(14:9).

Kuma hakika an samu hakan, a lokacin khalifofi shiryayyu da bayansu, a cikin wannan al'ummar. Saboda nasarar Allah bata gushe ba tana cigaba har Musulunci ya kai ga inda wani addini bai taba kaiwa gare shi ba, kuma suka shiga addinin Musulunci adadin da basu shiga wani addinin na daban ba. Har zuwa lokacin da saba wa umurnin Allah ya auku daga wannan al'ummar, sai aka jarrabe ta da rarrabuwar kai da watsewar al'amura, sai abinda ya auku ya auku. Tare da haka, wannan al'ummar da shi addinin suna tare da jin-kan Allah da tausasawarSa, abinda tunaninka baya iya kaiwa gare shi!

Ita kuma ishara ta biyun ita ce, cewa lallai ajalin rasuwar Manzon Allah – - ﷺ ya kusanto, bayanin haka, shine lallai rayuwarsa al'amari ne mai girma, wanda Allah ya rantse da ita, kuma lallai al'amura masu girma an saba akan kare su ne da neman gafara, kamar sallah da hajji da makamancin haka, don haka umurnin da Allah ya yi wa ManzonSa cewa ya yi godiya da neman gafara a wannan halin ya nuna cewa lallai ajalinsa ya zo, don haka sai ya shirya domin haduwa da UbangijinSa, kuma ya cike rayuwarsa da mafificin zikiri da neman gafara, Sai Annabi – ﷺ ya kasance yana kokarin fassara Alkur'ani da aikinsa, kuma yana fadan hakan a cikin sallarsa, saboda a cikin ruku'insa da sujadarsa ya kasance yana yawaita fadin: "***Subhanakal***

**[TAFSIRIN SURATUL *'MASAD'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]**

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Hannaye biyu na Abu-Lahabi sun halaka, kuma shima ya halaka. 2. Dukiyarsa bata tsare masa komai ba, da abinda ya tara. 3. Zai shiga Wuta mai huruwa 4. Tare da Matarsa mai daukar itace, 5. A jikin wuyanta akwai igiyar kaba (ranar kiyamah).**

Abu Lahab baffah ne ga Annabi – ﷺ - , ya kasance mai tsananin gaba da cutarwa a gare shi, don haka, ya ki ya bi addininsa, kuma yaki bashi kariya ko don kusancin dangantaka, Sai Allah ya zarge shi da irin wannan zargin mai girma, wanda kuma aibi ne a gare shi, har tashin kiyama, a inda ya ce:

**(1) "Hannaye biyu na Abu-Lahabi sun halaka"**, Ma'ana: hannayensa sun yi asara, kuma ya tabe, "**kuma shima ya halaka**" bai samu wata riba ba.

**(2) "Dukiyarsa bata tsare masa komai ba"**, dukiyarsa da ta kasance a wurinsa sai ta halakar da shi, haka kuma **"abinda ya aikata"**; ba zai hana masa azabar Allah ba, a lokacin da azabar za ta sauka a gare shi.

**(3-5) "Zai shiga wuta mai huruwa"**, kuma Wutar zata masa kawanya ta kowane gefe, Shi, **"da kuma Matarsa mai daukar itace"**, itama ta kasance mai yawan cutar da Manzon Allah . Suna taimaka wa juna da mijinta akan sabo da ketare iyaka, da aikata sharri, da yin duk mai yiwuwa wajen cutar da Manzoﷺ Ta tara zunubai a gadon bayanta, kamar Mutumin da yake hada itatuwa, wanda ya tanada masa igiyar **"kaba"** a makale da wuyarsa. Ko kuma ma'anar ayar, ya zama cewa, lallai zata dauko itatuwa ga mijinta, tana rataye da igiyar kaba a makale da wuyanta.

Koma menene, Wannan Surar akwai mu'ujiza daga cikin ayoyin Allah (mu'ujizozi); saboda Allah ya saukar da wannan surar kafin mutuwar AbuLahabi da matarsa, kuma ya bada labarin cewa za a azabtar da su a Wuta. Wanda hakan kuma dole ya nuna cewa, lallai su ba za su karbi Musulunci ba, Sai kuma abin ya auku kamar yadda Masanin gaibi da abubuwan da suke a fili (Allah) ya bamu labari!

**[TAFSIRIN SURATUL *'IKHLAS'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]**

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Ka ce: Shine Allah Makadaici. 2. Allah, wanda ake nufinsa da bukata. 3. Bai Haifa ba, kuma ba a haife shi ba. 4. Kuma babu wani da yake tamka a gare shi.**

**(1) "Ka fadi"** zance mai tabbaci; wanda baka shakkarsa, kana mai kudurta shi, tare da sanin ma'anarsa, cewa: "Shine Allah Makadaici" wanda ma'anar dayantaka ta kadaitu da shi; domin shine Makadaicin da ya kadaita da kamala, wanda yake da sunaye kyawawa, da sifofi masu kamala madaukaka da ayyuka masu tsarki, wanda bashi da tsara ko makamanci.

**(2) "Allah, wanda ake nufinsa da neman biyan bukatu"** saboda halittar sama da ta kasa mabukata ne gare shi, matsananciyar bukata; suna rokonsa bukatunsu, kuma suna bayyanar da kwadayinsu wurin neman ya warware musu abubuwan da suka dame su. Wannan kuma saboda shi Allah kammalalle ne cikin dukkan sifofinSa: Masanin da yake da kamala cikin iliminSa, Mai hakurin da ya ke da kamala cikin hakurinSa, Mai jin kai wanda ya kai makura cikin tausayinSa, wanda rahamarSa ta game kowane abu. . . . ka fadi kamar haka, akan sauran sifofin Allah gaba daya.

**(3)** Yana daga cikin kamalarSa, kasancewar "Bai Haifa ba, kuma ba a haife shi ba", saboda cikar wadacinSa; baya bukatar komai.

**(4) "Kuma babu wani da yake tamka a gare shi",** la a cikin sunayenSa, ko a cikin sifofinSa, ko a cikin ayyukanSa, Albarkar Allah ta yawaita, kuma Ya daukaka! Wannan surar ta kunshi tauhidin Allah ne cikin sunayenSa da sifofinSa.

**[TAFSIRIN SURATUL *'FALAK'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]**

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Ka ce: Ina neman tsari daga Ubangijin safiya 2. Daga sharrin abinda ya halitta, 3. da sharrin dare idan ya yi duhu, 4. Da sharrin masu tofe-tofe a cikin kulle-kulle, 5. Da sharrin mai hassada idan ya yi hassada.**

**(1) "Ka fada"**, kana mai neman tsari " Ina neman tsari" ina neman mafaka, ina neman kariya, da tsarewa

"daga Ubangijin da ya tsage hasken safiya" ma'ana: wanda ya kagi kwayar hatsi da kwallon dabino, mai tsage hasken safiya.

**(2) "Daga sharrin abinda ya halitta"** wannan ya kunshi dukkan abinda Allah ya halitta; na Mutane da Aljanu da dabbobi, sai a nemi tsarin Mahaliccinsu daga sharrin da yake cikinsu.

**(3)** Sai Allah -bayan ya ambaci lafazin neman tsari mai gamewa-, ya sake kebance wasu halittun, ya ce: "da sharrin dare idan ya yi duhu", ma'ana daga sharrin abinda yake kasancewa a cikin dare a lokacin da duhu ya sauka wa Mutane, lokacin da dayawa daga rayuka masu sharri da dabbobi masu cutarwa, suke yaduwa.

**(4) "da sharrin masu tofe-tofe a cikin kulle-kulle"**, wato, daga sharrin masu sihiri wadanda suke amfani wajen sihirinsu da yin tofi a jikin kullin da suka kulla akan sihiri.

**(5) "da sharrin mai hassada idan ya yi hassada"**, Mai hassada shine yake son gushewar ni'ima daga wanda yake masa hassadar, sai ya yi kokarin bin dukkan sababin da ya samu iko akansa wajen gusar da ni'imar. Sai aka bukaci neman tsarin Allah daga sharrin mai hassada da lalata kaidinsa.

Mai ainu (idaniyar kambun baka) shima ya shiga cikin lafazin mai hassada, saboda kambun baka baya aukuwa sai daga mai hassada, mai sharrin dabi'a, mai mummunar rai.

Wannan surar ta kunshi neman tsari daga dukkan nau'ukan sharri, gamammu da kebantattu. Kuma ta yi nuni cewa lallai sihiri yana da hakika, ana tsoron cutarwarsa, kuma ana neman tsarin Allah daga gare shi, da kuma sharrin ma'abutansa.

❁❁❁❁❁❁

**[TAFSIRIN SURATUN *'NAS'* WANDA TA SAUKA A MAKKAH]**

**Da sunan Allah Mai rahama Mai jin-kai. 1. Ka ce: Ina neman tsari daga Ubangijin Mutane, 2. Mamallakin Mutane, 3. Abin bautar Mutane, 4. Daga sharrin mai sanya waswasi mai boyewa 5. Wanda yake sanya waswasi a cikin kirazan Mutane, 6. Na daga Aljanu da Mutane.**

**(1-6)** Wannan surar ta kunshi neman tsari daga Ubangijin Mutane, Mamallakinsu, Abin bautarsu, daga Shedan, wanda shine asalin sharrace-sharrace gaba dayansu kuma tushensu, wanda cikin fitinarsa da sharrinsa, akwai yadda **"yake sanya waswasi a cikin kirazan Mutane",** sai ya rika kyautata musu sharri, yana nuna musu shi a sura mai kyau, yana nashadantar da kudurinsu wajen aikata shi, kuma yana sanya musu kasalar aikata alheri, yana nuna musu shi a surar da ba surarsa ba. Kuma Shedan koyaushe yana kan wannan halin; wato yana sanya musu waswasi, yana buya, wato ya kan yi turus daga sanya waswasi a lokacin da Bawa ya ambaci UbangijinSa ya nemi taimakonSa wajen tunkude masa Shedan. Don haka, ya dace, Bawa ya rika neman taimako, yana neman tsari, yana neman kariya daga rububiyyar Allah ga Mutane gaba dayansu, kuma dukkan halittu suna karkashin renonsa da mulkinsa, domin kowace dabba Allah shine yake riko da makwarkwadarta, da kuma cancantarsa ga bauta, wanda Allan ya halitta su dominta; domin hakan ba zai cika a gare su ba, face idan ya tunkude musu sharrin makiyinsu (Shedan) wanda yake son ya yanke su daga bautar Allah, ya sanya shamaki tsakaninsu da bautar, kuma yake son ya sanya su cikin rundunoninsa, domin su kasance daga masu fadawa Wuta. Kuma mai sanya waswasi kamar yadda yake kasancewa daga Aljanu, to yana kasancewa daga Mutane, don haka Allah ya ce: " **daga Aljanu da Mutane**".

Dukkan yabo sun tabbata ga Allah Ubangijin Talikai a farkon lamari da karshensa, a zahiri da badini. Kuma muna rokon Allah Ta'alah ya cika mana ni'imarSa, kuma ya yi afuwa ga zunubanmu wadanda suka shamakance tsakaninmu da tsakanin yawa-yawan albarkokinSa, da kura-kurai da sha'awowin da suka tafiyar da zukatanmu daga barin tadabburin ayoyin littafinSa. Kuma muna fatan kada Allah ya haramta mana alherin da suke wurinSa saboda sharrin da ya ke wurinmu. domin babu mai debe tsammani daga rahamar Allah face Mutane kafirai. Kuma babu mai debe tsammani daga rahamarSa face Batattu.

Salatin Allah da sallamarSa su kara tabbata ga ManzonSa annabi Muhammadu, da iyalanSa da sahabbansa gaba daya, salati da sallama, masu dawwama, masu saduwa a tsawon dukkan lokatai.

Yabo ya kara tabbata ga Allah, wanda cikin ni'imarSa ne kyawawan ayyuka suke zama cikakku.

## TAMBAYOYI AKAN GABATARWA DA TAFSIRI

1. Wanene Mawallafin littafin "Darussa muhimmai…?
O Abdul'aziz ibn Baz O Muhammadu ibn Usaimin O Haisam Sarhan

2. Don me muke karanta littafin "Darussa muhimmai"?
O domin suna da muhimmanci O don Malamai sun yi wasici da a muhimmantar da su.
O saboda wadannan darussan a cikinsu akwai muhimman abinda Musulmi ya ke bukata O Duka amsoshin.

3. Wannan littafin a cikinsa, ya kunshi:
O Halin Musulmi tare da Alkur'ani, da Tauhid O Sallah da alwala O Ladubba da halaye O Tsawatarwa kan sabo. O Shirya Mutumin da ya Mutu O Duka amsoshin.

4. Musulmi za a fara lakkana masa, ana gyara masa karatun, ana haddatar da shi, ana masa sharhin …:
O Suratul Alak. O Suratul Fatiha. O Suratul Ikhlas.

5. Mutane sun kasu dangane da tadabburin Alkur'ani da aiki da shi zuwa bangare biyu abin zargi (Ma'abuta sakaci, da Masu ketare iyaka), da Masu tsakaitawa (Haka ne – Kuskure ne ).

6. Wane littafin Tafsiri Dalibi zai fara da shi?
O Ibn Kasir. O As-Sa'diy. O Al Kurdubiy .

7. Dalibi ya kan fara karatunsa ne da kananan littatafai gabanin manyan littatafai (Haka ne – A'a )

8. Dalibi zai fara nazarin littatafan tafsiri ne, da karanta tafsirin surar da zata kwadaitar da shi cigaban karatu, kamar: Kasas, Maryam, Kahf ( Haka ne - A'a ).

9. Zai yiwu Dalibi ya rika sauraron littatafan tafsirin da ake ji ake karantawa; idan karatu yana wahalar da shi ( Haka ne – A'a ); kamar shirin tafsirin Alkur'ani cikin sauti, wanda aka gina shi akan tafsirin Sa'adiy.

10. Annabi –SAW- ya tsawatar kan karatun Alkur'ani, ba tare da tadabburin ma'anarsa ba (Haka ne – A'a )

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL FATIHA

11. "Sura" an sanya mata suna sura ne, saboda kamar an mata wani ganuwa da datanga ne (suur); ta yadda babu wani abu daga cikinta da zai fita, haka babu wani abu daga wajenta da zai shiga cikinta (Haka ne – A'a).

12. An sanya wa *Fatiha* wannan sunan ne, saboda …
…………………………………………………………………………

13. Daga cikin sunayen *Suratul Fatiha* akwai:
O Ummul Kur'ani (Uwar Kur'ani). O Sab'ul masaniy (ayoyi 7 da ake yawan maimaitawa). O Surar rukiyyah O Surar sallah.
O Duka amsoshin.

14. Neman tsarin Allah wajibi ne gabanin fara karatun Alkur'ani, duk da cewa ibada za mu yi; ba sabo ba, To menene sababin hakan?

..................................................................................................

..................................................................................................

15. Menene ma'anar kalmar *'A'uzu'*?

..................................................................................................

16. *Shaidan* an kira shi da *'rajim' ne* saboda …

O Saboda shi korarre ne daga rahamar Allah. O Saboda ana jifansa da taurari.

O Saboda yana jifan 'yan Adam da cutukan sha'awowi da shubuhohi . O Duka amsoshin.

17. *Jariy* da *Majrur* a cikin kalmar Da sunan Allah *'Bismi-llahi'* suna kulle ne da wani fi'ili da aka share, wanda ake jinkirtawa, ake kaddara shi da abinda ya dace (Haka ne – A'a).

18. Allah…..

O Shine abin bautawa cikin soyayya da girmamawa.

O Babu wanda aka sanya masa wannan sunan, in banda Allah.

O Shine sunan da sauran sunayen Allah suke komowa gare shi.

O Ance shine sunan Allah, wanda yafi sauran sunayen girma (Ismul Lahil A'azam).

O Ba a share *Alif* da *Laam* a lokacin kiransa da (Ya Allahu).

O Gaba dayan abinda ya gabata.

19. Menene banbancin dake tsakanin sunayen Allah: *Ar-Rahmaan da Ar-Rahim*?

..........................................................................................

..........................................................................................

20. Renon Allah da kulawarSa ga halittunSa kashi biyu ne. Menene su?

O Gamamme da kebantacce. O Budadde da kayyadadde.

21. Mafi yawan addu'oin Annabawa –alaihimus salam- sukan kasance ne da lafazin…

O Allah . O Rabb .

22. Ranar Ad-*Din* shine…

O Ranar kiyama. O Ranar da za a yi sakamako ga Mutane kan ayyukansu. O Duka amsoshin.

23. "Ka shiryar da mu hanya madaidaiciya; IHDINAS SIRADAL MUSTAKIM" Shine addu'ar da yafi gamewa, kuma yafi amfani ga Bawa ( Haka ne –A'a )

24. Kalmar *Ad-Din* ana fadinta da ma'anar: O Sakamako. O Aiki O. Wani lokaci da ma'anar sakamako, wani lokaci dama'anar aiki.

25. Gabatar da ambaton "Iyyaka" gabanin "Na'abudu" a ilimin nahawu yana nuna…

O Kebance shi da yin bauta. O Bashi da wata fa'ida.

26. Gabatar da ambaton lamarin 'ibada' gabanin 'isti'ana; neman taimako' misali ne na ambaton…

O abu mai gamammen ma'ana gabanin kebantacce. O Gabatar da hakkin Allah akan hakkin BawanSa. ODuka gaba daya.

27. Me yasa ayar "Iyyaka na'abudu" ta zo da sigar jam'i?

……………………………………………………………………

28. Bauta……

O Suna ne da ya game dukkan abinda Allah yake so, kuma ya yarda da shi; na ayyuka da zantukan zahiri da badini .

O Kankan da kai ga Allah, ta hanyar bin umurninSa da hanuwa da haninSa, cikin sonsa da girmamawa.

O Ana fadar ibada da wannan ma'anar, wani lokacin kuma da wancan.

29. Shiriyar da ake nufi a cikin fadinSa Ta'alah "Ka shiryar da mu" itace…

O Nuna mana wannan hanya, ka sanar da mu ita. O Ka taimake mu wajen dacewa da bin hanyar (taufik). O Duka biyun.

30. Wadanda Allah ya musu ni'ima kuma ya nufe su da fadinSa "Hanyar wadanda ka yi ni'ima a gare su" sune…

O Duk masu imanin wannan al'ummar.

O Wadanda Allah ya musu ni'ima; wato Annabawa da Siddikai da Shahidai da Salihai.

31. "A kai kadai muke bauta, kuma a gare ka muke neman taimako" ya kunshi hada tsakanin shari'a da kaddara (Haka ne – A'a ).

32. Daga cikin abinda yake tafe, wanene ya kunshi abinda babu shi a waninsa a Alkur'ani?
O Suratul Fatihah. O Ayatul Kursiy. O Suratul Ikhlas.

33. Fadin Allah "Ka shiryar da mu hanya madaidaiciya" ya kunshi…
O Tabbatar da Annabci. O Raddi ga daukacin 'yan bidi'a, batattu O Duka biyun.

34. Fadin Allah Ta'alah "Mamallakin ranar sakamako" ya kunshi cewa…
O Sakamako zai kasance da adalci. O Bawa mai aiki ne hakikatan.
O Sakamako ya kan kasance ne akan ayyuka.
O Duka gabadaya.

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN AYATUL KURSIY

35. Ayatul *Kursiy* an sanya mata wannan sunan ne, saboda a cikinta an *ambaci kujerar Allah* ( Haka ne – A'a ).

36. Wace aya ce tafi girma a cikin Alkur'ani?
O Ayar sha'anin bashi. O Ayar hakkoki guda goma.
O Ayatul *Kursiyu*.

37. Alkur'ani ta fiskar ma'anoninsa wani yafi wani ( Gaskiya ne – Kuskure ne ).

38. Sunaye nawa daga sunayen Allah kyawawa ayatul *Kursiy* ta kunsa?
O Biyar. O Shida. O Bakwai.

**39.** Sunan Allah "**Rayayye; Alhayyu**" yana nuna kamala ta fiskar
O ZatinsaO Mulki.

**40.** Sunan Allah "**Tsayayye; Alkayyum**" yana nuna kamalarsa ta fiskar…
O zati O Karfin mulki.

**41.** Idan sunan, **Alhayyu** ya hadu da **Alkayyum**, sai su nuna kamala ta bangaren zati da karfin mulki ( Haka ne – Kuskure ne ).

**42.** Sunayen Allah, **Rayayye** da **Tsayayye** a hade, sun maimaitu a cikin Alkur'ani har …
O sau uku. O A wurare hudu. O Wurare biyu.

**43.** Dangane da sifofin da ake korewa, babu makawa za a kore su ga Allah, kamar yadda Allahn yake kore su ga kansa, kuma ManzonSa –Sallal Lahu alaihi wa sallama- ya kore masa su, tare da tabbatar masa da sifantuwa da kishiyoyinsu, saboda zallar kore abu ba kamala ba ne, Misalinsa: Muna kore wa Allah gyangyadi da barci ne, saboda sifantuwarsa da cikakkiyar rayuwa da Tsayuwa (haka ne – A'a ).

**44.** Allah ba zai yi izini ga wani kan yin ceto ba, face wanda ya yarda da shi, kuma baya yarda da komai sai …
O Tauhidi. O Bin Annabawa. ODuka biyun.

45. Abinda Allah ya sanar da Halittu na al'amuran shari'a da kaddara…
O Kadan ne. O Suna da yawa.

46. "Ya san abinda yake gaba gare su" ya kunshi yanayin da ake ciki, da wanda yake zuwa, "da abinda yake bayansu" ya kunshi wanda ya shude (Gaskiya ne – kuskure ne).

47. Ma'anar sunan Allah "Madaukaki" yana nufin…
O da zatinSa O da sifofinSa O Shine wanda saboda daukakarSa ya rinjayi dukkan halittu. O Duka gabadaya .

48. Wanda ya karanta ta a cikin dare ba zai gushe ba yana samun kariya daga Allah, kuma S*haidan* ba zai kusance shi, har ya wayi gari ba, Wace aya ce?
O Karshen suratul Bakarah. O Ayatul kursiyyi.

49. Ana karanta ayatul Kursiyyi …
O Bayan sallolin farilla biyar. O Kafin yin barci.
O da safiya da maraice. O Duka gabadaya.

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATU IZAZUL

50. *Suratuz Zalzala* sura ce da ta sauka a… O Makkah. O Madinah.

51. *Suratuz Zalzalah* a cikinta akwai… O Tsoratarwa O Kwadaitarwa.
O Duka biyun.

52. Fadin Allah: "Kuma kasa ta fitar da abinda ta kunsa (masu nauyi)" ma'anarsa shine:
O Duwatsu da Tuddai. O Matattu da taskoki.

53. Kasa itama zata bada shaida akan Bayi akan ayyukansu ( Gaskiya ne – A'a ).

54. Fadin Allah "Ashtatan" yana nufin…
O Kowa shi kadai. O Jama'a daban-daban.

55. Fadin Allah: "Wanda ya aikata daidai da kwayar zarra zai ganshi…" ya yi kama da fadinSa "*Kuma suka samu abinda suka aikata, a halarce*…" (Haka ne – Ba haka ba).

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL ADIYAAT

56. *Suratul Adiyaat* sura ce da ta sauka a … OMakkah. OMadinah.

57. Ma'anar lafazin *"Adiyaat"* shine…
O Dawakai. O Duk abinda yake motsawa. ODuka biyun.

58. Suratul *Adiyaat* a cikinta akwai tsoratarwa kan tozarta hakkoki na wajibi ( Gaskiya ne – kuskure ne).

59. Fadi ma'anonin wadannan kalmomin:
*Dabhan*: …………………………………………………………..
*Kad'han*: …………………………………………………………..
Nak'an: …………………………………………………………..
Lakanud: …………………………………………………………..

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN ALKARI'AH

**60.** **Suratul Kaari'ah** sura ce da ta sauka a … O Makkah. OMadinah.

61. Daga cikin manufofin suratul *Kaari'ah* akwai tsawatarwa daga: OFirgicin yinin kiyama O Akwai jarrabawa a rayuwar Duniya.

62. Alkaari'ah shine… O Ayoyin narkon azaba. O Yinin Kiyama.

63. Yi bayanin ma'anar jumlolin da suke tafe:
"Kamar 'ya'yan fari masu watsuwa" ……………………………..
"Kamar gashin sufin da aka sabe" ………………………..……….

64. Sikelin da aka ambato a cikin wannan surar … O Sikeli ne na hakika. O Kinaya ne kan yin adalci.

65. "rayuwa yardadda" wato … O a Duniya.O Aljannah.

66. "To, Uwarsa wutar Hawiya ce" yana nufin: O Zata kasance a gare shi kamar Uwar da ta lazimci 'danta. O Uwar kwakwalwarsa zata kasance a cikin Wuta O .Duka biyun.

**67.** Fadin Allah **"To, me ya sanar da kai mecece ita?"** … O akwai kara kambama lamarinta. O Tambaya akanta.

68. Daga cikin sunayen Wuta –Allah ya tsare mu daga shiga cikinta- akwai:
O Haawiyah. O Jahannam. O Hudamah. O Lazah. O Sa'ira. O Sakar. O Dukansu gabadaya.

69. “Wata wuta ce mai zafi" –Allah ya mana kariya daga gare ta- zafinta ya ninku akan zafin Wutar Duniya, da ninki nawa?
O Saba'in. O Casa'in . O Casa'in da tara.

**TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUT TAKASUR**

70. Wannan surar, ta sauka ne a... O Makah. O Madinah.

71. A cikin wannan surar akwai…
O Bada labari kan halayen Mutane. O Muzanta wa Bayi kan barin abinda aka halitta su dominsa (kadaita Allah).

72. Cikin wannan surar akwai hani kan alfahari da yawaitar abin Duniya, koda manufar alfaharin neman yardar Allah ne (Haka ne – Ba haka ba ne).

73. Fadin: *Ya tafi makwancinsa na karshe* ga wanda ya mutu: a cikinsa akwai…
O Karyata cewa za a tayar da Matattu. O Fadin hakan ya halatta.

74. Cikin fadin Allah "har kuka ziyarci…", Allah ya kira su masu ziyara, bai kira su masu zama a kabari dindin ba. Me ya sa?
O saboda rayuwar kabari (barzakhu) manufarta itace wucewa gidan Lahira.
O saboda an fitar da su daga gidajensu da suka mallaka a Duniya, zuwa kabari wanda ba mallakar su ba ne.

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL ASR

75. Suratul Asr sura ce da ta sauka a… O Makkah O Madinah.

76. Suratul Asr a cikinta akwai dalili akan mas'aloli hudu, wato ilimi, aiki da shi, da'awa da hakuri (Haka ne – Ba haka ba).

77. Wadanne jumloli ne suka inganta, dangane da rantsuwa da wanin Allah: O Allah yana da daman ya rantse da abinda ya so daga cikin halittunsa. O Bai halatta Halittu su yi rantsuwa da wani idan ba Allah ba. O Halitta zai iya yin rantsuwa da wanin Allah. O Amsar farko da ta biyu.

78. **Hakuri** ya kasu zuwa… O kashi biyu. O uku. O hudu.

79. Surar a cikinta akwai al'amura **hudu**: Da al'amuran farko biyu, Mutum zai samu kamala a karan-kansa. Da al'amuran karshe biyu zai yi kokarin wasu su samu kamala ( Haka ne – A'a ) .

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL HUMAZAH

80. Wannan surar ta sauka a… O Makkah. O Madinah.

81. Ma'anar kalmar *"Wailun"* shine…
O Kwari ne a Jahannama. O Narko ne da ya kunshi wannan kwarin a wutar Jahannama da waninsa.

82. *Hamz* yana kasancewa da zance, yayin da *Lamz* yake kasancewa da aiki ( Gaskiya ne – A'a ).

83. Ayar "Yana zaton dukiyarsa zata dawwamar da shi ne" tana amfanar da cewa: Lallai biyayya yana kara tsawon rayuwa ( Haka ne – A'a ).

84. Ma'anar fadin Allah Ta'alah "To me ya sanar da kai…" yana nuna lallai Annabi ﷺ … O ya san wannan Wutar O Bashi da ilimi akanta.

85. Cikin fadin Allah Ta'alah, "Wutar Allah ce da aka hura ta", abin hurawan nata, shine…
O Mutane. O Duwatsu. O Duka biyun.

86. Fadin Allah Ta'alah "wanda take lekawa akan zukata" ma'ana:
O take leka akidar zuciya. O wanda take shige jiki, har ta kona zukata.

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL FIL

87. Suratul "Fil" ta sauka ne a … O Makkah. O Madinah.

88. Daga fa'idodin wannan sura; Lallai babbar dabba a bayan kasa (giwa) tana tsoron ta yi ta'addanci ga dakin Allah, kenan Mutum shi yafi dacewa da jin tsoron hakan ( Gaskiya ne – A'a ).

89. An haifi Annabi ﷺ a shekarar … O Giwaye O Shekarar bakin ciki . O Shekarar toka .

90. `Wannan surar, tana daga mu'ujizozin annabcin Annabinmu ﷺ - (Irhasaat) wanda shine abun da ya saba wa al'ada, wanda yake bayyana ga Annabi gabanin annabcinsa ( Haka ne – A'a) .

**91.** Fadi ma'anonin laffuzan da suke tafe:
"*Dayran abaabil*"........................................................
"*Ka'asfin ma'kul*" ........................................................

## TAMBAYOYIN TAFSIRIN SURATU KURAISH

**92.** ***Suratu Kuraish*** ta sauka ne a... O Makkah. O Madinah.

**93.** Wannan surar suna da alaka da suratul... O Kafirun. O Fil. O Nas.

**94.** *Kuraishawa sun saba yin bulaguro* zuwa kasar *Shaam* a lokacin hunturu, a lokacin bazara kuma zuwa *Yamen* ( Haka ne – A'a ).

**95.** Allah ya girmama haramin Makkah da Mutanenta a cikin zukatan Larabawa, don haka suka girmama su, basu iya far musu...
O a garin Makkah.
O a Makkah, da kuma cikin halin bulaguronsu.

**96.** Allah ya kebance dakinsa, yace: Ubangijin daki, saboda falalarsa da darajarsa, tare da cewa shine Ubangijin kowane abu ( Haka ne – A'a ).

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL MA'UN

97. *Suratul Ma'una* ta sauka ne a... O Makkah. O Madinah.

98. Ma'anar kalmar *'Addini'* a cikin fadin Allah "Shin baka ga wanda yake karyata addini ba" shine...
O Tayar da Mutane da sakamako. O Cin bashi, da kin bayar da hakkoki .

99. Ma'anar '*yadu'u*' shine… O yana bari . O yana tunkudewa da karfi.

100. Maraya shine wanda _____ ya mutu. O Ubansa. O Uwarsa.

101. Ana kiransa maraya ne matukar … O bai balaga ba. O koda ya balaga .

102. Mantuwa a cikin sallah shine ma'abucinsa ya cancanci zargi, yayin da shagala ko mantawa da lamarinta kowa yana iya aukawa a cikinsa ( Haka ne – A'a ).

103. Hukuncin riya; wanda kuma ita ce kokarin nuna aiki … O halal ne. O makaruhi ne. O haramun ne. O karamar shirka. O babbar shirka

104. A cikin wannan surar akwai kwadaitarwa kan lamarin aikin tallafi ( E – A'a ).

105. *Al Maa'un* da aka ambata a cikin wannan surar shine…
O Kwano. O Duk abinda a al'adance ake bayar da aronsa.

## TAMBAYOYI KAN TAFSIRIN SURATUL KAUSAR

106. *Suratul Kausar* ta sauka ne a… O Makkah. O Madinah.

**107.** ***Al Kausara*** shine… O tafki (kogi) O alkhairi mai yawa da tarin falala.

**108.** Allah ya kebance ibadodin nan na salla da yanka, saboda sune ibadodin da suka fi girma, cikin dukkan abinda ake kusantar Allah da su ( Haka ne – A'a).

**109.** ***'Shaani'aka'*** yana nufin… O Mai kinka. O Mai zarginka
O Mai aibanta ka. O Duka gabadaya.

**110.** Fadin Allah **"…shine mai yankakken albarka"** a fakaice yana nuna, lallai masoyin Annabi –sallal Lahu alaihi wa sallama- ambatonsa da yabonsa za su wanzu ( haka ne – A'a ).

**111.** Wannan surah ta nuna cewa, lallai Annabi zai samu yawan mataimaka da mabiya ( Gaskiya ne – A'a ).

**TAMBAYOYI KAN TAFSIRIN SURATUL KAFIRUNA**

**112.** ***Suratul Kaafiruna*** sura ce da ta sauka a… O Makkah. O Madinah.

**113.** ***Suratul Kaafiruna*** ana karanta ta a raka'ar farko bayan fatiha a…
O Sunnar bayan ketowar alfijir. O Sunnar bayan Maghriba.
O Sunnar bayan kammala *Dawafi*. O Sallar *Witr*.
O Duka gaba daya.

**114.** Ibadar da a cikinta aka hada Allah da waninsa…
O Tana da nakasa . O Ba a daukarta a matsayin ibada.

**115.** Wanda aka nufa da fadin "ka ce" shine…O Annabi ﷺ .
O Annabi ﷺ da dukkan wanda za a iya fiskantar da maganar gare shi.

**116.** ***Kaafirai*** sune…
O Duk wanda addinin Annabi ﷺ ya kai gare su, sai basu yi imani da shi ba, misalin Yahudawa da Nasara. O Kafiran Makkah .

**117.** Wannan surar a cikinta akwai al'amarin barranta daga shirka da ma'abotansa, acikin zuciya da harshe da kuma gabbai ( Haka ne – A'a ).

**118.** Maimaicin da aka yi a surar…
O saboda karfafa zance ne. O domin na farkon ya nuna rashin samuwar aikin, Na biyun kuma, ya nuna, lallai hakan ya zama sifar da ta zama tabbatacciya.

**TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUN NASR**

**119.** ***Suratun Nasr*** ta sauka ne a … O Makkah. O Madinah.

**120.** Wannan surar a cikinta akwai, bushara, da labari, da umurni, da fadakarwa ( Haka ne – A'a ).

**121.** Wannan Al'ummar, da wannan addinin, suna da dinbin rahamar Allah da tausasawarSa abinda ba zai darsu a tunani ba ( Haka ne - A'a ).

**122.** A surar, an yi ishara cewa lallai ajalin rasuwar Manzon Allah ﷺ ya matso kusa ( Gaskiya ne – A'a).

**123.** Domin ya yi aiki da wannan surar, Annabi ﷺ ya kasance yana fada a cikin ruku'insa da sujjadarsa: "SUBHANAKAL LAHUMMA RABBANA WA BI HAMDIKA ALLAHUM MAG FIR LIY" ( Gaskiya ne – A'a ).

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL MASAD

**124.** ***Suratul Masad*** ta sauka ne a… O Makkah. O Madinah.

**125.** Abu Lahabi …
O Baffan Annabi neﷺ . O Bashi da wata alaka ta kusanci da Annabi .

**126.** Abin zargi ne shi, har zuwa ranar kiyama………
O Abu Lahabi. O Duk wanda ya yi adawa da Annabi.ﷺ

**127.** Ka ambaci ma'anonin wadannan kalmomin:
*Tabbat*………………………………………………………………………
*Maa-Kasaba*…………………………………………………………………
*Jidihaa*………………………………………………………………………
*Masad*………………………………………………………………………

**128.** Wannan surar ta kunshi mu'ujiza daga cikin ayoyin Allah akan Abu Lahabi da matarsa; cewa lallai su ba zai yiwu su karbi Musulunci ba( Gaskiya ne –A'a)

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL IKHLAS

**129.** ***Suratul Ikhlaas*** sura ce da ta sauka a … O Makkah. O Madinah.

**130.** ***Suratul Ikhlaas*** an kira ta da wannan sunan ne, saboda………
O Gabadayanta ta kebanta ne da kawo sifofin Allah
O Tana tseratar da mai karatunta daga yin shirka O Duka biyun.

**131.** Wannan surar, ta fiskar sakamako, tana daidai da........
O Rabin Alkur'ani O Daya bisa hudun Alkur'ani. O Daya bisa ukun Alkur'ani.

**132.** Ana karanta wannan surar, a raka'a ta biyu bayan Fatiha, a:
O Sunnar bayan ketowar alfijir. O Sunnar bayan Maghriba .
O Sunnar bayan Dawafi. O Sallar Witr. O Dukansu gabadaya.

**133.** Ana karanta Suratul ***Kaafiruna*** da ***Ikhlasi*** cikin yini da dare domin ka tabbatar da nau'ukan *Tauhid* guda uku ( Gaskiya ne – A'a ).

**134.** ***Suratul Ikhlaas*** ta karfafa lamarin.........
O Tauhidin bauta (Uluhiyyah). O Tauhidin Rububiyyah da tauhidin sunaye da sifofi.

**135.** Ma'anar **"Ka fada"** shine... O fadi da harshe kawai.O fadi, aiki, da akida.

**136.** Fadin Allah **"Ka ce: Shine Allah Makadaici"** yana nufin, Makadaici a cikin RububiyyarSa, da UluhiyyarSa, da sunayenSa da sifofinSa ( Haka ne– A'a ).

**137.** Fadin Allah **"AsSamad"** yana nufin.........
O Wanda ake nufi cikin dukkan bukatu. O Wanda ya tsayu da kansa, kuma waninsa ya tsayu da shi. O Shugaban da ya cika cikin shugabancinSa, kuma yake da kamala cikin RububiyyarSa da UluhiyyarSa da sunayenSa da sifofinSa. O Duka gaba daya .

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUL FALAK

139. ***Suratul Fala***k sura ce da ta sauka a… O Makkah. O Madinah.

140. Ana karanta ***Suratul Fala***k a…
O Bayan sallolin farilla. O Gabanin yin barci. O Duka biyun.

141. Rubuta ma'anonin wadannan kalmomin:
*'A'uzu*.................................................................
*AlFalak*................................................................
*Gaasik*................................................................ ...
*wakab*................................................................ ..
*An-Naffaasaat*.........................................................
*Al'ukad*................................................................
*Haasidin*..............................................................

142. Wannan surar a cikinta akwai…
O Neman tsari, gamamme, da kebantacce. O Sihiri abu ne tabbatacce (yana da hakika). O Duka biyun.

## TAMBAYOYI AKAN TAFSIRIN SURATUN NAAS

143. ***Suratun Naas*** sura ce da ta sauka a… O Makkah. O Madinah.

144. Ana karanta ***Suratun Naas*** a…
O Bayan sallar farilloli. O Gabanin yin barci. O Duka biyun.

145. Menene ma'anar kalmar *Al Khannaas*"?

. ........................................................................................................

# DARASI NA BIYU

## DARASI NA BIYU: RUKUNNAN MUSULUNCI

Bayani akan rukunan Musulunci; Na farkonsu, mafi girmansu shine: Shaidawa babu abin bautawa bisa cancanta sai Allah, kuma annabi Muhammadu manzon Allah ne, tare da fassarar ma'anar kalmar shahada da bayanin sharudan LA ILAHA ILLAL LAHU.

Ma'anar kalmar Shahada: (La'ilaha) yana kore cancantar bauta ga dukkan abin bauta koma bayan Allah. (IllalLahu) kuma, yana tabbatar da bautar ga Allah Shi kadai; ba tare da an hada shi da abokin tarayya ba.

**Amma SHARUDAN KALMAR SHAHADA KUWA SU NE:**

1. Sanin ma'anar wannan kalama wanda yake gusar da jahiltar ta.
2. Tabbatar da abin da take nuni a kai, wanda yake gusar da kokanto.
3. Tsarkake ta da ikhlasi, wanda yake gusar mata da shirka.
4. Gaskata ta, wanda yake gusar da karyata ta.
5. Nuna kauna da soyayya, wanda yake gusar da kiyayya.
6. Janyuwa (da'a) a gare ta, wanda yake gusar da saba mata.
7. Karba da yarda da ita, wanda yake gusar da yin watsi da ita.
8. Kafircewa dukkan abinda ake bauta masa koma bayan Allah. Kuma an hada wadannan sharuddan a cikin baitin waka guda biyu:

| | |
|---|---|
| Ilimi, yakini, da ikhlasi da gaskatawarka, tare da | Soyayya, da mika wuya, da karbarka ga kalmar shahada |
| An kara na takwas, wanda shine kafircewarka | da duk abinda aka bauta masa koma bayan Allah |

Sai bayani akan (Shahadatu anna Muhammadan rasululLahi). **Kuma abinda take hukuntawa shine:** Gaskata Manzon Allah ﷺ cikin abinda ya ba da labari, da yin biyayya ga abinda ya yi umurni , da nisantar abinda ya yi hani ya tsawatar, da kuma, kada a bauta wa Allah face da abinda ya shar'anta.

Sa'annan ya bayyana wa dalibi sauran rukunan Musulunci guda biyar, wato: Sallah, Zakka, Azumin watan Ramalana, Aikin Hajji ga wanda ya samu iko.

**RUKUNNAN KALMAR "*LA ILAHA ILLAL LAHU*"**

| Korewa: "Babu abin bautawa bisa cancanta…" Tana kore cancanta ga dukkan abin bauta koma bayan Allah (Kafirce wa Dagutu) | Tabbatarwa: "Face Allah" Tana tabbatar wa Allah cancantar bauta shi kadai. (Imani da Allah) |
|---|---|

Kalmar LA ILAHA ILLAL LAHU tana da rukunai biyu, sune korewa da tabbatarwa, Ka rike su.

**Bayani akan sharuddan kalmar *"La ilaha illalLahu"***

Sharuddan *"La ilaha illalLahu"* kamar hakoran mabudin kofa ne. *Kuma kalmar "La ilaha ilalLahu"* ita ce mabudin Aljannah, kuma mabudi baya budewa sai da hakora. Don haka duk abinda ya zo a cikin Alkur'ani da hadisi, cewa lallai wanda ya fadi: *"La ilaha illalLahu"* yana da kaza, to lallai gabanin ya samu wannan sakamakon sai ya tabbatar da wadannan sharuddan, guda takwas:

**1- Sanin ma'anarta:** kishiyan haka shine jahiltar ma'anarta, Kuma wanda ya jahilci ma'anarta to ba zai amfana da ita ba, don haka ya wajaba ga wanda yake son shiga Musuunci ya san ma'anarta. Manzon Allah - ﷺ - ya ce: *"Wanda ya mutu, alhalin yana sane da cewa babu abin bautawa bisa cananta face Allah, ya shiga Aljannah"* (Muslim).

**2- Yakini:** Dari bisa dari (100%). Idan ya samu shakku koda daya cikin dari (1%) cikin kafirce wa ababen bauta koma bayan Allah, ko yace bashi da matsaya, ko ya yi taraddadi, to bashi da tauhidi, haka idan ya yi shakka akan kafircin Yahudawa da Nasara, wadanda addinin annabi Muhammadu ﷺ ya iske su, to bashi da tauhidi, Annabi ﷺ ya ce: *"SHAIDAWA BABU ABIN BAUTA BISA CANCANTA FACE ALLAH, KUMA NI MANZON ALLAH NE; Babu Bawan da zai sadu da Allah da wadannan biyun; alhalin baya shakka akansu face ya shiga Aljannah"* (Muslim).

**3- Ikhlasi:** Duk wanda ya yi riya cikin al'amarinta, ko ya yi babban shirka –kamar Mutumin da ya bauta wa wanin Allah- to lallai kalmar baza ta amfane shi ba, Annabi ﷺ ya ce: *"Wanda yafi rabauta da samun cetona, shine: Wanda ya fadi: La ilaha illalLahu yana mai tsarkake ta daga zuciyarsa, ko daga ransa"* (Bukhari).

**4- Gaskantawa** Duk wanda ya fade ta yana mai karyata ta - kamar Munafiki - to ba za ta amfane shi ba. Daga Annabi ﷺ lallai ya ce: "Babu wanda zai shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma Muhammadu bawanSa ne manzonSa, yana Mai gaskata hakan daga zuciyarsa, face Allah ya haramta shi daga Wuta" (Bukhari da Muslim).

**5- Soyayya:** Sai ya so Allah, ba zai so wani tare da Allah ba, kuma zai so dukkan wadanda Allah ya yi umurnin a so su. Kishiyarta kuma shine kiyayya. Domin hakan yana daga abubuwan da suke warware Musulunci**: (Wanda ya ki wani abu daga cikin ababen da Manzon Allah SAW ya zo da su, koda kuwa ya yi aiki da shi, to ya kafirta. Allah Ta'alah ya ce**: "Daga cikin Mutane akwai wanda yake rikon kini baicin Allah, yana sonsu kamar son Allah…" (2:165).

6- **Mika wuya:** Wannan yana nuna cewa dole mu yi aiki da kalmar. Domin idan Mutum ya ki yin aiki da ita, to ba zai amfana da ita ba. Allah Ta'alah ya ce: "**Lallai ina rantsuwa da Ubangijinka, ba za su yi imani ba, har sai sun yarda da hukuncinka cikin abinda ya auku a tsakaninsu, sa'annan ba za su sami wani kunci a cikin zukatansu dangane da abinda ka hukunta ba, kuma su sallama maka sallamawa**" (4:65).

7- **Karbarta:** wato, kada ya yi watsi da fadinta, ko aiki da ita, ko kudurta ta. Allah ya ce: **"Lallai su, sun kasance idan an ce musu: Babu abin bautawa face Allah, sai su dora girman kai * suna cewa: Shin za mu bar gumakanmu, saboda maganar wani mawaki mahaukaci?"** (37:35).

8- **Kafircewa:** Ma'ana, Duk wanda aka bauta masa koma bayan Allah, to bautarsa batacciya ce, saboda babu wanda ya cancanci a masa bauta face Allah.

## FADAKARWA

Lallai babu makawa, dangane da kalmar shahada, sai an fade ta da harshe, an yi aiki da ita, an kuma kudurce ta a zuciya.

## RABE-RABEN SOYAYYA

**Son halitta tare da Allah**

Wannan babbar shirka ne. Allah ya ce: "Daga cikin Mutane akwai wanda yake rikon kini baicin Allah, yana sonsu kamar son Allah…" (2:165).

**Son halitta domin Allah**

Wannan wajibi ne, hasali ma soyayya don Allah itace mafi karfin igiyar imani! Allah ya ce: "Muhammadu manzon Allah ne. Wadannan dake tare da shi masu tsanani ne akan kafirai, masu rahama ne a tsakaninsu…" (48:29). Kuma wannan nau'in soyayyar tana kasancewa cikin abu hudu:

- Son aikin da Allah Ta'alah ya ke so; wanda kuma shine dukkan abinda shar'a ta zo da shi, kamar Tauhidi.
- Son mai aiki; kamar Annabawa da Manzanni da Mala'iku da Sahabbai, da dukkan mai Tauhidi.
- Son lokatan da Allah yake so; kamar daren lailatul Kadr da kaso na ukun karshe a cikin kowane dare.
- Son wuraren da Allah Ta'alah yake so; misalin Makkah da Madinar Annabi ﷺ

**So na al'ada**

Wannan halal ne, matukar ba a fifita ta akan son Allah ba. Misalinta: Son da, da son mata. Annabi ya ce: "'Dayanku ba zai yi imani (cikakke ba) face na kasance wanda yafi soyuwa a gare shi fiye da dansa da mahaifinsa da sauran Mutane gaba daya".

Menene ma'anar kalmar (BawanSa) a cikin fadin Musulmi '**Ina shaidawa lallai Muhammadu Bawan Allah ne kuma ManzonSa**?

Ma'anarsa shine ba za a yi bauta ga Annabi ﷺ ba; saboda bashi da wani abu na sifofin cancantar kebanta da wani abu na Rububiyya da Uluhiyya da Asma'u wasSifaat.

Kuma Annabi ﷺ shi yafi daukacin halittun Allah kyautata bauta ga Allah, domin ya tabbatar da kammalalliyar bauta ga Allah Mabuwayi da daukaka.

## KASHE-KASHEN BAUTAR ALLAH TA'ALAH

**Ubudiyyah mai gamewa**

Ita ce bauta mai alaka da Rububiyya, wannan kuma ta game dukkan halittun Allah. Allah Ta'alah ya ce: "Kuma Babu wani a cikin sammai da kasa, face zai je wa Mai rahama yana matsayin Bawa" (19: 93). Wannan kuma ya kunshi Muminai da Kafirai.

**Kebantacciya**

Wannan ita ce bautar da'a gamammiya, Allah Ta'alah ya ce: "Kuma bayin Mai rahama sune wadanda suke yin tafiya akan kasa da sauki…"(25:63). Wannan kuma ya game duk wanda ya bauta wa Allah SWT da shari'arSa.

**Wanda tafi kebantuwa**

Ita ce irin bautar Manzanni – A.S- Allah ya ce: "… Lallai shi ya kasance Bawa mai godiya" (17:3). Wannan nau'in na bauta da aka jingina ga Manzanni tafi zama kebantacciya; saboda babu wanda zai sha gaban Manzanni cikin al'amarin bautar Allah SWT.

## TARIHIN ANNABINMU ﷺ

| | |
|---|---|
| **NASABARSA** | Shine: Muhammadu dan Abdullahi dan Abdul-Muttalib dan Haashim, Shi kuma Haashim daga kabilar Kuraishawa ne, Kuraishawa kuma suna cikin Larabawa, su kuma Larabawa daga zuriyar annabi Ismaa'il dan Ibraahim Al- Khalil (badadin Allah), Salatin Allah ya kara tabbata a gare su. |
| **HAIHUWARSA** | An haife shi ﷺ a shekarar giwaye, a garin Makkah, a watan Rabiyul Awwal. Ya rayu tsawon shekaru 63. Daga cikinsu shekaru 40 gabanin manzanci, Shekaru 23 yana Annabi Manzo. Ya kasance maraya; domin Mahaifinsa ya rasu gabanin haihuwarsa. Sai ya kasance karkashin kulawar Kakansa Abdulmuddalib, Bayan rasuwar kakansa kuma sai Baffansa Abudalib ya dauke shi. |
| **MANZANCINSA** | An turo shi ﷺ zuwa ga Mutane da Aljanu. Kuma duk wanda sakon Annabi ya iske shi, sai bai yi imani da shi ba, to wannan kafiri ne, ko wanene shi. |
| **KIRANSA** | Annabi ﷺ ya yi kiransa ne zuwa ga bautar Allah, da riko da kyawawan dabi'u, da yin ayyuka masu kyau. Ya yi hani kan bautar wanda ba Allah ba, da kuma nisantar munanan dabi'u, da ayyuka. |
| **AN MASA ISRA'I DA MI'IRAJI** | An yi isra'i da shi ﷺ; aka dauke shi daga garin Makkah zuwa Baitul Makdis. Daga nan aka hau da shi zuwa sama ta bakwai (Mi'iraji), Allah ya yi magana da shi, kuma ya farlanta masa salloli 5 na farillah. |
| **HIJIRARSA ZUWA RASUWARSA** | Annabi ﷺ ya yi hijira daga garin Makkah zuwa Madinah, kuma ya rasu a Madinah. Kuma an bunne shi a dakin Uwar Muminai; Aishah – Allah ya kara yarda a gare ta-. |

| | |
|---|---|
| **ISAR DA MANZANCI** | Allah ya cika addini da shi. Kuma Annabi ﷺ ya isar da manzanci isarwa mabayyani, ya sauke amana, ya yi nasiha ga Al'ummah, ya yi kokari a hanyar Allah iyakar kokari da dukkan nau'ukan jihadi. Don haka, ba zai yiwu ga wani ya kara wani abu a cikin wannan addini ba. |
| **MANYAN YAKUKANSA** | Guda bakwai ne, sune: Yakin Badr, Uhud, AlKhandak, Khaibar, da Fat-hu Makkah, Tabuka, da Hunain. |
| **'YA'YANSA BAKWAI** | AlKasim, Ibrahim, Abdullah wanda kuma shine Dayyib Dahir, Zainab, Rukayyah, Ummu Kulsum da Fatimah; kuma dukkansu sun rasu a cikin rayuwar Annabi ﷺ in banda Fatimah wanda ta rasu bayan rasuwarsa da watanni shida –Allah ya kara yarda a gare su gaba daya-. |
| **MATANSA GOMA SHA BIYU** | Khadijah, A'ishah, Saudah, Hafsah, Zainab AlHilaliyah, Ummu Salamah Hindu, Zainab bint Jahsh, Juwairiyyah bint AlHaris, Safiyah bint Huyay, Ummu Habibah Ramlah, Rayhanah bint Zaid, da Maimunah bint AlHaris –Allah ya kara yarda a gare su gaba daya-. |
| **WADANDA SUKA SHAYAR DA SHI ﷺ** | Mahaifiyarsa Aminah bint Wahb, Suwaibah barar Baffansa Abu- Lahabi, Halimah bint Abiy Zu'aib As-Sa'diyyah –Allah ya kara yarda a gare ta-. |
| **FARKON WAHAYIN DA YA SAUKA GARE SHI ﷺ** | Shine fadin Allah Ta'alah a farkon Alak: "1. **Ka yi karatu da sunan Ubangijinka wanda ya yi halitta-,** 2. **Ya halitta Mutum daga gudan jini,** 3. **Ka yi karatu, kuma Ubangijinka shine Mafi karamci -,** 4. **Wanda ya sanar da Mutum alkalami-,** 5. **Ya sanar da Mutum abinda bai sani ba". (Alaq: 1-5)** |

| | |
|---|---|
| **FARKON WANDA YA YI IMANI DA SHI ﷺ** | Daga cikin manyan **mazaje** shine AbuBakr As-Siddik. Daga cikin manyan **mata** kuma Uwar Muminai Khadijah bint Khuwailid. Daga cikin **yara** kuma Aliyu dan Abiy Dalib. Daga cikin **barori** kuma Zaid bn Harisah. Daga cikin **Bayi** kuma Bilal bn Abiy Rabah. |
| **HAJJINSA DA UMRARSA ﷺ** | Ya yi Umrah sau hudu 4; dukkansu a watan Zulka'adah. Kuma ya yi hajji sau daya 1, wanda ake kiransa da hajjin bankwana, a shekara ta goma 10 bayan hijira. |
| **DABI'UNSA ﷺ** | Allah Ta'alah ya ce: "*Kuma lallai kana kan halayya masu girma*". Uwar Muminai, A'ishah ta ce: "Dabi'unsa sun kasance Alkur'ani". |
| **MUHIMMANCIN KARANTA TARIHIN ANNABI ﷺ** | Ibnul Kayyim –Allah ya yi masa rahama- ya ce: Tun da samun sa'idar Bawa a Duniya da Lahira ya zamto ya rataya ne kawai da bin shiriyar Annabi ﷺ, to ya wajaba ga wanda ya yi nasiha ga kansa kuma yake son tsirarta da samun sa'idarta ya san shiriyar Annabi ﷺ da tarihinsa da sha'aninsa gwargwadon abinda zai fitar da shi daga cikin wadanda suka jahilce shi, ya shigar da shi daga jerin mabiyansa da mataimakansa da rundunarsa. Mutane kuma dangane da wannan lamari; tsakanin mai karantawa ne, da mai yawaitawa, da wanda bashi da komai. Kuma falalar tana hannun Allah; yana bayar da ita ga wanda yake so. Allah shine Ma'abucin falala mai girma. |

# DARASI NA UKU

## RUKUNNAN IMANI

Rukunnan imani guda shida ne: Ka yi imani da Allah, da Mala'ikunSa, da LittatafanSa, da ManzanninSa, da ranar karshe, kuma ka yi imani da kaddara na alherinsa da sharrinsa daga Allah Ta'alah ne.

**Imaani**: Furuci ne a harshe, da akida a zuciya, da kuma aiki da gabbai, yana karuwa da ayyukan biyayya, kuma yana raguwa da sabo. Dalilin haka shine:

**Furuci da harshe:** Dalilinsa shine fadinsaﷺ, "Mafi kololuwarsu shine *fadin*: La ilaha illal Lahu".

**Aikin gabbai:** Dalili akansa shine fadinsa ﷺ: "Mafi karancinsu shine *gusar* da abu mai cutarwa daga hanya".

**Aikin zuciya**: Dalili akansa shine fadinsa : "*Kunya* sifa ce daga imani".

**Karuwar imani:** Dalili akansa fadin Allah: " Wanene a cikinku wannan ayar ta kara masa imani?" (9:124).

**Raguwar imani:** "Ban ga masu nakasar hankali da addini…" (Bukhariy, Muslim).

## Sabubban karuwar imani

- Karatun tauhidi, musamman babin sunayen Allah da sifofinsa
- Yawaita ayyukan da'a
- Barin ayyukan sabo
- Yin tunani cikin halittun Allah

## Sabubban raguwar imani

- Barin Karatun tauhidi, musamman babin sunayen Allah da sifofinsa
- Barin ayyukan da'a
- Aikata sabo
- Barin tunani cikin halittun Allah

## Rukunnan imani shida

- Imani da Allah
- Imani da Mala'iku
- Imani da Littatafai
- Imani da Manzanni
- Imani da Ranar Karshe
- Imani da Kaddara Na Alherinsa da Sharrinsa

## RUKUNIN FARKO: IMANI DA ALLAH

| Imani da samuwar Allah, yana kasancewa da al'amura hudu: | Imani da Rububiyyar Allah | Imani da Uluhiyyar Allah | Imani da SunayenSa da sifofinSa |
|---|---|---|---|
| **Jin samuwarsa da dalili na hankali** A hankalce ba za a iya suranta samuwar halitta ba tare da Mahaliccinta ba. "Shin an halitta su ba tare da komai ba ne? Ko kuma sune Masu yin halittar?" (Kur'an52:35). | **Da dalili na ji da jiki** Ka kan kasance a cikin bala'i da tsanani, sai ka daga hannayenka biyu sama kana cewa: Ya Ubangina! Sai ka samu wannan bala'in da izinin Allah ya kau. | **Da fidirar halitta Annabi ﷺ ya ce:** "Dukkan abin haihuwa ana haihuwarsa ne akan *Fidrar addini*. Iyayensa biyu sune suke mayar da shi Bayahude, ko Banasare ko Bamajuse…" (Bukhariy, Muslim). | **Da dalili na shari'a** Ibnul kayyim –Allah ya masa rahama- ya ambaci cewa, Babu wata aya a cikin littafin Allah, face a cikinta akwai dalili akan Tauhidi. |

## RUKUNI NA BIYU: IMANI DA MALA'IKU

Mala'iku: halitta ce ta gaibu. Allah ya halitta su daga haske. Suna yin biyayya ga Allah; basu saba masa. Suna da ruhi; "Rai mai tsarki (Jibrilu)" (Kur'ani 16:102), da gangar jiki; "Allah Mai sanya Mala'iku 'yan aike (manzanni) ma'abota fukafukai" (Kur'ani 35:1), da hankula da zukata; "Har a lokacin da aka kwaranye tsoro daga zukatan Mala'iku sai suce: Menene ubangijinku ya ce?"(Kur'an 34 :23). Muna yin imani da Mala'iku, da kuma dukkan abinda Allah ya sanar da mu na sunayensu (*Jibril*, *Mika'il*, *Israfil*, da sauransu.), da sifofinsu "Ba su saba wa Allah cikin abinda ya umurce su", da ayyukansu.

## MALA'IKUN DA AKA BAMU LABARI

Daga cikinsu akwai, Takwas da suke dauke da Al'arshi, *Jibril* da aka wakilta ga al'amarin wahayi, da *Mika'il* wakilin ruwan sama. Mun yi imani da su gaba dayansu, da kuma dukkan labarun da aka bamu akansu, a dunkule ko a fadade.

## RUKUNI NA UKU: IMANI DA LITTATAFAI

Wajibi ne mu yi imani cewa, littatafan maganar Allah ne a hakika (ba majazi ba), wanda aka saukar zuwa gare mu, ba halitta ba. Kuma Allah ya turo da littafi tare da kowane Manzo. Mun yi imani da su, da dukkan abinda Allah ya bamu labari akansu; na sunayensu da labarunsu da dokokin cikinsu, a dunkule da kuma a fayyace, matukar ba a soke hukuncinsu ba. Kuma mun yi imani cewa, lallai Alkur'ani ya soke dukkan abinda ya sauka gabaninsa na littatafai, wanda kuma sune*:* At-Taurah, Injila, Zabura, Suhuf Ibrahim da Musa (Amincin Allah ya kara tabbata a gare su).

## RUKUNI NA HUDU: IMANI DA MANZANNI

Wajibi ne mu yi imani cewa su mazaje ne, kuma basu da wani abu na sifofin da suka kebanci Ubangiji; kuma su, bayi ne na Allah ba a yin bauta a gare su. Allah ya turo su, kuma ya saukar da wahayi a gare su, kuma ya karfafe su da ayoyi (mu'ujizozi). Kuma lallai su, sun sauke amana, sun yi nasiha ga al'ummai, sun iyar da manzanci, kuma sun yi kokari akan tafarkin Allah iyakar kokari. Za mu yi imani da su gaba daya, da abinda Allah ya sanar da mu na sunayensu, da sifofinsu, da sauran labarunsu, a dunkule da kuma a fayyace. Kuma lallai farkon Annabawa shine annabi Adam (AS), farkon Manzo kuma annabi Nuh (AS), Kuma cikamakon Annabawa da Manzanni shine annabi Muhammadu –SAW-. Kuma dukkan dokokin da suka gabata an soke aiki da su da zuwan shari'ar annabi Muhammadu ﷺ . Kuma **ULUL AZMI CIKIN MANZANNI** guda biyar ne; an ambace su a cikin surori biyu; wato AsShurah da Ahzab, sune: (Muhammadu SAW, da Nuh AS, da Ibrahim AS, da Musa AS, da Isah AS).

## RUKUNI NA BIYAR: IMANI DA RANAR KARSHE

Ya kunshi yin imani da dukkan abinda Annabi SAW ya bada labari akansa, na abubuwan da za su kasance a bayan mutuwa, misalin, tambayoyin kabari (azabar kabari), busa a cikin kaho, tasowar Mutane daga kabarinsu da awun ayyuka, da bayar da takardu, da ketare siradi, da shan ruwa daga tafkin alkausara, da yin ceto, da shiga Aljannah, ko Wuta, da ganin da Muminai za su yi ga UbangijinSu a yinin kiyama, da kuma a cikin gidan Aljannah, da sauran al'amura na gaibu.

**RUKUNI NA SHIDA:**

**IMANI DA KADDARA NA ALHERINSA DA SHARRINSA**

Yana da rukunnansa hudu, Mai wake ya hada su a cikin fadinsa:

**ILIMI, RUBUTUN MAJIBINMU, NUFIN ALLAH HALITTARSA; WANDA KUMA ITA CE, SAMARWA DA KASANTARWA**

**ILIMI:**

Imani da cewar Allah ya san kowane abu; a dukunle da kuma a fayyace. Dalilin haka shine fadin Allah Ta'alah: " Yana sanin abinda yake gaba gare su, da abinda yake a bayansu…"

**RUBUTU:**

Imani da cewar Allah ya rubuta kaddarorin kowane abu, har zuwa kiyama lokaci da za ta tsaya. Dalilin haka fadin Allah Ta'alah: ''Kuma babu wata mai boyuwa a cikin sama da kasa, face tana a cikin littafi bayyananne " (27:75).

**NUFIN ALLAH:**

Imani da cewar abinda Allah ya so shine yake kasancewa, abinda kuma bai so ba, to ba zai kasance ba. Da kuma cewa lallai Bawa yana da nufi, sai dai ya na karkashin nufin Allah. Allah ya ce: "Kuma ba za ku so ba (sai ya tabbatu) face idan Allah Ubangijin halittu ya nufa" (81:29).

**HALITTA:**

Imani da cewar Bawa halitta ne; shi da ayyukansa, haka sauran halittu, Dalilin haka shine fadinsa:

"Allah ne Mai halittar dukkan komai" (39:62), "Allah shi ne ya halitta ku, da kuma abinda kuke aikatawa" (37:96).

# DARASI NA HUDU

## RABE-RABEN TAUHIDI, DA KARKASUWAR SHIRKA

Bayanin rabe-raben Tauhidi, lallai ya kasu gida uku: Tauhidin Rububiyya, da Tauhidin Uluhiyya, da Tauhidin sunaye da sifofi.

**Tauhidin Rububiyya:** Shi ne yin imani da cewar; Allah shi ne Mahallicin kowane abu, kuma shi yake gudanar da komai, ba shi da abokin tarayya a cikin haka.

**Tauhidin Uluhiyya kuwa shi ne:**Yin imani da cewar Allah shi ne abin bauta na gaskiya, ba Shi da abokin tarayya a cikin haka, Wannan kuwa ita ce ma'anar kalmar (LA ILAHA ILLAL LAHU). domin ma'anarta ita ce: Babu abin bauta bisa cancanta da gaskiya sai Allah. Kuma ibadodi gaba daya, kama daga Sallah, azumi da sauransu, wajibi ne a tsarkake su ga Allah shi kadai, bai halatta a karkatar da wani abu daga cikin ibadodi ga wanin Allah ba.

**Shi kuwa Tauhidin (al'asma'u wassifati), shi ne:** Imani da duk abin da ya zo a ciikin Alkur'ani Mai Girma, da kuma ingantattun hadisai, na sunayen Allah da sifofinSa, tare da tabbatar da su ga Allah shi kadai; ta fiskar da ta dace da Shi, ba tare da an canja ma'anar sunayen ko sifofin naSa ba, ko lalata ma'anarsu, ko kuma kwatanta Shi ko misalta Shi da waninsa. Domin aiki da fadin Allah Madaukaki: (Ka ce: Shine Allah Makadaici. Allah wanda ake nufi da bukata. Bai haifa ba kuma ba a haife shi ba. kuma babu daya da ya yake kwatankwaci a gare shi). (Suratul Ikhlas 1-4). Da fadinsa Mabuwayi da daukaka: (Babu wani abu da ya yi kama da shi, Kuma shi Mai ji ne Mai gani) (Suratus Shura:11).

Sai dai wasu Maluman sun kasa Tauhidi gida biyu ne, sai suka shigar da Tauhidin sunaye da sifofi a cikin Tauhidin Rububiyya. Amma babu komai akan hakan, domin manufar a fili take a dukkan kashe-kashen guda biyu.

Shi kuma kashe–kashen shirka, uku ne: Babbar shirka, da karamar shirka, da boyayyiyar shirka.

**Babbar shirka:** Ita ce take hukunta lalacewar ayyuka, da dawwama acikin Wuta ga wanda ya mutu akan haka, kamar yadda Allah Ta'alah ya ce: (Da za su yi shirka-wato, Annabawa- da duk abinda suke aikatawa ya lalace) Suratul An'am, /88. Kuma Allah ya ce: (Baya kasancewa ga mushirkai, su raya Masallatan Allah, alhali kuwa suna masu shaida ga kawukansu da kafirci, Wadannan su ne wadanda ayyukansu suka lalace, kuma su a cikin wuta masu dauwama ne) Suratu Tauba/ 17.

Kuma duk wanda ya mutu akan babbar shirka to ba za a gafarta masa ba, kuma Aljanna ta haramta a gare shi, kamar yadda Allah ya ce: (Hakika Allah baya gafara idan aka hada shi da wani –shirka-, amma yana yafe laifin da bai kai girman shirka ba ga wanda yaga dama). Surstun Nisa'i/48. Kuma Allah ya ce: (Lallai wanda ya hada Allah da wani -ya mutu bai tuba daga shirka ba- to lallai hakika Allah ya haramta masa Aljannah, kuma Wuta ce makoma a gare shi. Kuma azzalumai basu da mataimaka -a wurin Allah-) Suratul Ma'ida/72.

Daga cikin nau'ukan babbar shirka akwai: rokon matattu da gumaka, da neman agajinsu, da yi masu bakance, ko yanka a gare su, da makamantan haka.

**Karamar Shirka:** Ita ce: wanda nassin Alkur'ani da Sunnah suka kira ta da sunan shirka, sai dai bata cikin jinsin babbar shirka, kamar yin riya a wasu ayyuka, da rantsewa da wanin Allah, da fadin: Allah ya so, Wane yaso. Da makamantan hakan.

Saboda fadar Annabi -ﷺ: (Abinda nafi jiye muku tsoro shine karamar shirka, sai aka tambaye shi cewa: mecece karamar shirka? Sai ya ce: ita ce; Riya-yin ibada don a gani).

Da fadinsa -Tsira da amincin Allah su kara tabbata a gare shi-: (Wanda ya rantse da wanin Allah to hakika yayi shirka).

Da fadinsa - ﷺ -: (Kada ku ce: Allah Ya so, Wane ya so, maimakon haka, ku ce: Allah ya so, **sannan** wane ya so) Abu-Dawud ya ruwaito shi da isnadi ingantacce daga Huzaifa dan Alyaman - رضي الله عنه

To, wannan nau'i na shirka baya fitar da Mutum daga Musulunci, kuma ba ya hukunta dawwama a cikin Wuta. Saidai yana shafe cikar Tauhidi.

Amma nau'i na uku, wanda shine: Boyayyar shirka Dalilinta shine fadin Annabi -ﷺ-: (Shin ba zan ba ku labarin abin da nafi jiye muku tsoro, sama da Dujal ba? Sai suka ce: a ba mu labari ya Ma'aikin Allah, sai ya ce: boyayyar shirka, Mutum zai tashi yana sallah sai ya rika kawata sallar; saboda abinda yake gani, na wani yana kallonsa).

Ana iya raba shirka zuwa gida biyu kadai, wato babba da karama. saboda boyayyar shirka tana fadawa cikinsu; domin ta kan iya faruwa a cikin babbar shirka, kamar misalin shirkar Munafikai; saboda suna boye lalatattun akidunsu, su rika bayyana musulunci, saboda riya, da kuma tsorace wa kai. Kuma hakan ya kan kasance cikin karamar shirka, kamar riya, irin yadda hakan ya gabata a cikin hadisin Mahmud dan Labid, da hadisin Abu Sa'id wanda aka ambata. Allah Shi ne mai datarwa.

## RABE-RABEN LAIFUKAN HARAMUN

**Babbar shirka:** Ita ce babba a cikin jerin laifuka.

**Karamar shirka**: Ita kuma bata kai babbar shirka girma ba, amma tafi laifukan kaba'irai girma.

**Laifin Kaba'rai:** Kaba'ira: ita ce: duk laifin da aka rataya mata kebantacciyar ukuba; kamar la'ana, da kora daga rahama, ko barranta daga mai aikata ta, ko ace yana daga cikin kafirai ko mushirkai, ko baya cikin muminai, ko aka sifanta shi da dabbobi mafiya muni …

**Kananan laifuka**: Laifin da Allah ya haramta shi, saidai bai rataya masa wata ukuba kebantacciya ba.

## LAIFIN KABA'IRAI

**Adadin laifukan kaba'irai?** Ba a san adadinsu ba, saidai an iyakance da ka'idar da muka ambata a sama.

**Hukuncin Mai aikata Kaba'irai**
-Mumini ne me tauyayyen imani.*Ko mu ce: Mumini ne da imanin da yake tattare da shi, fasiki ne saboda aikata laifin da ya yi.*
-Ana son wannan Mutumin gwargwadon abinda ya ke tare da shi na imani, A kuma ki shi gwargwadon abinda yake tare da shi na aikin laifi.
-Ba a zama tare da shi a lokacin da yake aikata wannan aikin.

**Girman kaba'irai**
Wani yafi wani, saboda fadin Annabi ﷺ: "Shin ba zan baku labari akan laifin da yafi girma ba?..." (Bukhari/

**Hukuncin Kaba'irai**
Dole babu makawa sai an tuba, saboda fadin Annabi ﷺ: "Mai kukan mutuwa idan ba ta tuba a gabanin mutuwarta ba…" (Muslim). A wani hadisin kuma "… matukar an nisanci aikata kaba'irai …" (Muslim).

## BANBANCE-BANBANCE TSAKANIN BABBAR SHIRKA DA KARAMA

### BABBAR SHIRKA

1. Tana fitar da Mutum daga Musulunci.
2. Tana rushe kyawawan ayyuka gaba daya.
3. Tana hukunta dawwama na har abada a Jahannama.
4. Tana halatta jinni da dukiyar wanda ya yi ta ga Shugaban Musulmai.
5. Dole a samu dalilan da ya nuna cewa babbar shirka ce.
6. Ya kudurta cewa, lallai sababi yana da boyayyen tasiri (zai iya halitta) a Duniya.
7. Ba a yafe wa Mutumin da ya mutu akanta.
8. Idan Bawa ya tuba daga aikata shirka Allah zai karbi tubarsa, saidai a yanayi biyu: Idan tubar ta kasance a lokacin da rana ta fudo daga mafadarta, ko ya tuba a lokacin gargara, wato lokacin halartowar mutuwarsa.

### KARAMAR SHIRKA

1. Bata fitarwa daga Musulunci.
2. Bata rushe dukkan ayyuka, saidai tana lalata aikin da ta shiga cikinsa.
3. Bata hukunta dawwama na har abada a cikin Jahannama.
4. Bata halatta jini da dukiya.
5. Dalili ya nuna cewa karamar shirka ce.
6. Ya dauki abinda Allah bai sanya shi sababi ba, a matsayin sababi.
7. Duk abinda ya zama hanya ce da take kaiwa ga babbar shirka, to karamar shirka ce.
8. Duk abinda Alkur'ani da hadisi suka kira shi *shirka ko kafirci*, sai ba a sanya masa (*Alif da Lam* ال) ba, to wannan karamar shirka ce, matukar ba a samu dalilan da suka nuna cewa babbar ba ce.

## DARASI NA BIYAR

### IHSAAN

Rukunin *Ihsaan* shine: Ka bauta wa Allah kamar kana ganinsa, idan kai baka ganinsa, to shi yana ganinka.

***Ihsaan***

Rukuni ne guda daya, amman yana da martabobi biyu:

**Ibadar kamar mai ganin Allah (Mushahadah)**

Ita ce ibada cikin kauna da kwadayi da begen samun abinda yake wurin Allah SWT. Misalin: Ibadar Annabawa da Manzanni-Allah ya kara yarda a gare su-, kamar fadin Annabi ﷺ: "...*Shin ba zan kasance Bawa mai yawan godiya ba*" Sai abinda ya tunkuda Mutum zuwa ga yin ibadar ya kasance shine kwadayi da so da fatan abinda yake wurin Allah, tare kuma da tsoron Allah.

**Ibadar wanda ya san ana kallonsa (murakabah)**

Ibada ce cikin tsoro da guje wa Wuta. Musulmi babu yadda za a yi fice daga wannan martabar.

## TAMBAYOYI AKAN TAUHIDI

1. Adadin martabobin addini nawa ne? O Uku O Hudu. O Biyar.

2. Adadin rukunnan Musulunci nawa ne? O Biyar. O Shida. O Bakwai.

3. Martabar Musulunci tafi girma akan martabar imani.
( Gaskiya ne - A'a ).

4. Rukunnan kalmar shahada **"La ilaha illalLahu"** adadinsu nawa ne?
O Bakwai. O Takwas. O Biyu.

5. Nawa ne sharuddan **"La Ilaha illalLahu"** ?
O Takwas. O Bakwai. O Biyar.

6. *Ilimi* yana cikin sharuddan **"La ilaha illalLahu",** kuma ma'anarsa shine:
O Ka fahimci ma'anar abu, akan hakikaninsa. O Babu abin bauta bisa cancanta face Allah.

7. Idan ya yi shakku kan kafircin Mutanen da sakon Musulunci ya kai gare su amma basu yi imani ba, hukuncisa shine:...
O Ya yi babban kafirci. O Idan yakininsa yafi shakkunsa, to bai *kafirta* ba.

8. *Karbar* **"La ilaha illalLahu"** yana cikin sharuddanta, kuma ana nufin a karbe ta da:
O Zancen baki. Aiki. O A zuci. O Duka gaba daya.

9. *Riya* a cikin **"La ilaha illalLlahu"** kamar riya a cikin ibadar sadaka ne, tana cikin karamar shirka ( Haka ne – A'a ).

**10**. Wanda ya fadi "La ilaha illalLahu" da harshe, ba tare da kudurta ta a zuciya ba:
O Yana da Tauhidi. O Musulmi ne ba Mumini ba. O Ya yi babban kafirci.
O Imaninsa yana da rauni.

**11**. Da zai so Annabi daidai da son Allah; wato ya musu soyayya iri daya:
O Ya yi babban kafirci. O karamin kafirci. O Babban laifi (kabirah).

**12**. Nawa ne rabe-raben soyayya? O Hudu. O Uku. O Biyu.

**13**. *So don Allah* yana kasancewa ga aiki, Mai aiki, zamannai da wurare ( Haka – A'a ).

**14**. *Son wani tare da Allah* hukuncinsa shine…
O Shirka karama. O Wajibi. O Babbar shirka.

**15**. Son wani don Allah, hukuncinsa shine…
O Halal. O Wajibi. O Babbar shirka.

**16**. Nawa ne rabe-raben bauta ga Allah (*Ubudiyyah)*? O 2 O 3 O 4

**17**. Dukkan halittu bayin Allah ne, bauta ta rinjaye, har kafirai ( Haka – A'a ).

**18**. Idan wani ya ce: "La ilaha illalLahu" sai ya ki yin aiki gaba daya; babu sallah babu wata ibada, to fadin kalmar : O Zata amfane shi. O Ba za ta amfane shi ba.

**19**. "*BawanSa ne ManzonSa*" a cikin kalmomin shahada: wato, *Bawa* ne ba za a yi masa bauta ba. Kuma *Manzo* ne ba za a karyata shi ba ( Haka – A'a ).

**20**. Dangane da shaidawa "*Lallai annabi Muhammadu bawanSa ne ManzonSa*"; Bin umurninsa, da gaskata labarinsa…Wannan ana daukarsu:
O Ma'anansa O Abinda kalmar take hukuntawa (muktadi).

**21.** Wanda ya baiwa Annabi ﷺ wani abu na sifofin Ubangiji, to lallai bai shaida shi *Bawa* ba ne ( Haka – A'a ).

**22.** Mafi kololuwar sifar Annabi ﷺ ita ce, kasancewarsa:
O Manzon Allah.ﷺ O BawanSa kuma ManzonSa. O Cikamakin Annabawa.

**23.** "Wanda ya kirkiri wata bidi'a a cikin Musulunci wanda yake ganin tana da kyau, to lallai kamar ya riya cewa annabi Muhammadu ﷺ ya ha'inci manzanci; domin Allah Ta'alah yana cewa: "A yau na cika muku addininku". Don haka; duk abinda a wancan yinin bai kasance addini ba, to a yau ba zai taba kasancewa addini ba". Wannan maganar wanene?
O Ibn Taimiyyah O Ibn Baaz O Imam Malik

**24.** Annabi Muhammadu ﷺ yana cikin zurriyar annabi… O Is'hak O Isma'il

**25.** Cike wuraren da babu rubutu: An haifi Annabi ﷺ a shekarar …………………….. a garin: …………… Rayuwarsa ta kasance tsawon **she**karu
……. Daga cikinsu shekaru; …………….. gabanin manzanci, da kuma shekaru ……….. yana Annabi Manzo. Ya zama annabi ne da saukar ayar …………… Ya kuma zama Manzo da saukar fadin Allah …………………......

**26.** An tura Annabi ﷺ ne zuwa ga:
O Mutanensa (Larabawa) O Mutane gabadaya. OMutane da Aljanu.

**27.** Mi'irajin Annabiﷺ shine tafiyar da ya yi daga Makkah zuwa Baitul Makdis ( Haka – A'a ).

**28**. Annabiﷺ ya yi hijirarsa zuwa garin…
O Da'if O Habasha O Madinah O Duka gaba daya.

**29**. Nawa ne yawan muhimman yakukan Annabi ?
O Daya O Biyu O Uku O Hudu O Biyar.

**30**. Nawa ne yawan 'ya'yan Anna ? O Uku O Hudu O Bakwai.

**31.** Annabi ﷺ ya yi hajjin bankwana, Wannan ya nuna cewar ya taba yin hajji gabanin haka. ( E – A'a ).

**32.** Karatun tarihin Annabi ﷺ hukuncinsa… O Wajibi ne. O Sunnah O Halal.

**33.** Cike wuraren da babu rubutu: Imani a shar'ia yana nufin: Magana ne da …………., da kudurtawa a …………., da aiki da ……………, yana karuwa da ayyukan ……….. …………, kuma yana raguwa da ………..

**34.** Rukunnan *Iman*i nawa ne? O Shida O Biyar O Hudu.

**35.** Imaninka da Allah yana hukunta yin imaninka da wasu abubuwa. Nawa ne adadinsu?
O Hudu O Uku O Biyu.

**36.** Dalilai kan *samuwar Allah* a dunkule… O Hude ne O Basu kirguwa.

**37.** *Mikaa'il* shine Mala'ikan da aka wakilta da al'amarin ruwan sama ( E, – A'a ).

**38.** Zukata na kasancewa ne ga 'Yan Adam, yayin da Mala'iku basu da zukata ( E – A'a )

**39.** Nawa ne adadin littatafan da muka sansu da sunayensu?
O Shida O Hudu O Bakwai O Dayawa.

**40.** Allah ya saukar da littafi ga kowane Annabi ( E – A'a ).

**41**. Farkon Manzanni shine annabi Adamu –A S- ( E – A'a ).

**42**. Muhammadu ﷺ manzo ne, ba Annabi ba ( E – A'a ).

43. Nawa ne adadin *Ulul azmi* daga cikin Manzanni? O 5 O 4 O Dayawa

44. Imani da ranar karshe ya kunshi imani da dukkan abinda yake kasancewa bayan mutuwa, har zuwa tasowar Mutane daga kaburburansu ( E – A'a ).

45. Imani da kaddara yana da martabobi, Nawa ne adadinsu?
O Hudu O Biyar O Uku

46. Shin Allah yana sanin abu gabanin aukuwarsa? ( E – A'a ).

47. Shin duk abinda Mutane suke aikatawa, Allah ya sani? ( E – A'a ).

48. Shin duk abinda Mutane suke aikatawa, Allah ya rubuta shi? ( E – A'a ).

**49.** Shin Bawa yana da nufi kebantacce, yana aikata abinda yake so da shi ( E – A'a ).

**50.** Shin ayyukan Mutane halittarsu aka yi? ( E – A'a ).

**51.** *Tauhid* ya kasu zuwa … O kashi biyu O uku O 2 , 3 babu matsala.

**52.** Ambato biyar, daga banbance-banbancen da suke tsakanin *shirka babba, da karama*.

1- ……………………………………………………………………………….

2-……………………………………………………………………………….

3-……………………………………………………………………………….

4-……………………………………………………………………………….

**5**-……………………………………………………………………………….

53. Kawo *misalai* biyar-biyar ga *babbar shirka, da karamar shirka*.

| Babbar shirka | Karamar shirka |
|---|---|
| ...................................... | ...................................... |
| ...................................... | ...................................... |
| ...................................... | ...................................... |
| ...................................... | ...................................... |
| ...................................... | ...................................... |

54. Munafurci na akida karamar *Shirka* ne wanda baya fitarwa daga Musulunci ( E – A'a ).

55. *Ihsaan* Ya kunshi ... O Rukuni daya O Rukunnai biyu ne.

# DARASI NA SHIDA

## SHARUDDAN SALLAH

***Sharuddan sallah guda tara ne:***

**1. Musulunci 2. Hankali 3. Iya rarrabe abubuwa (Tamyiz; kaiwar yaro wannan mataki)**
**4. Dage hadasi 5. Kawar da najasa 6. Suturce al'aura 7. Shigan lokaci**
**8. Fiskantar alkiblah 9. Niyyah.**

### Sharadi na daya: Musulunci

Kishiyansa shine kafirci. Da Mutumin da yake zagin Allah, ko yake yin bauta ga wanin Allah zai yi salla, to sallarsa batacciya ce, saidai idan ya tuba zuwa ga Allah.

### Sharadi na biyu: Hankali

Kishiyansa hauka. Wanda yake cikin maye shi yafi cancantar a ki karbar sallarsa.

### Sharadi na uku: Tamyiz (iya rarrabewa)

Ba balaga ake nufi ba. Abin nufi shine iya rarrabewa tsakanin abubuwa; wato ya san tambaya da amsa. Wannan kuma bashi da iyakantacciyar shekara. Saidai galibi dan shekaru bakwai yana yin hakan (tamyiz).

Yaushe sallar karamin Yaro take inganta? Amsa: Idan ya iya rarrabewa tsakanin tambaya da amsa, tsakanin ruwa da wuta, Idan ba haka ba, sallarsa batacciya ce.

**Sharadi na hudu: Dage hadasi**
Kuma ya kunshi:

**Babban hadasi**
Baya daguwa sai da wanka.

**Karamin hadasi**
Mai gushewa da alwala.

**Sharadi na biyar: Gusar da najasa**

Daga *jiki, bagiren salla, da tufafi*. Da Mutum zai yi salla da najasa, yana sane, kuma yana da ikon gusar da ita, yana tune da ita; bai manta ba, to sallarsa batacciya ce.

- Kuma gusar da najasa tana kasuwa zuwa kashi uku:

**Mai tsanani:**
Ita ce gusar da najasar kare, saboda Annabi ﷺ ya bada umurnin a wanke kokon da kare ya yi lallagi a cikinsa har sau 7; Na farkonsu da turbaya. Muslim ya ruwaito.

**Mai sauki:**
Ana gusar da ita ta hanyar yayyafa ruwa, *kuma yana kasancewa ne ga fitsarin yaro namiji wanda bai fara cin abinci ba, da maziyyi da maniyyi, tare da kasancewar maniyyi mai tsarki ne, saboda Annabi*ﷺ ya kasance yana yayyafa masa ruwa idan danye ne, yana kuma kankare shi idan ya bushe.

**Wanda take tsakanin biyun:**
Ana gusar da ita da yayyafa ruwa tare da matsewa, kuma yana kasancewa ne ga duk abinda ba na farko ko na biyun ba, kamar fitsarin namiji da mace, da wasu najasosin.

### Najastattun abubuwa

Fitsarin dan Adam da kashinsa, da fitsarin dabbar da ba a yi izinin cin namanta ba, da dabbobi masu farauta gaba daya, sai wanda za a wahala ga shamakantuwa daga gare su, kamar kuliya, alfadari, jaki. Da jini mai kwarara daga dabba bayan yankanta, da jinin da ya fito ta hanyoyi biyu (gabbai biyu na al'aura), da dukkan matattu, in banda gawar Mutum, da mataccen abinda bashi da jini a jikinsa, da dabbar kogi wanda ta mutu a cikinsa, da matacciyar fara.

### Sharadi na shida: Suturce al'aura

Al'aura guda uku ne:

**Mai sauki:**

Ita ce al'aurar namiji dan shekaru bakwai zuwa goma, an shardanta ya suturce farjinsa biyu (gaba da baya).

**Mai tsanani**

Al'aurar Mace 'ya (ba baiwa ba) balagaggiya; Wajibi ne ta suturce gaba dayan jikinta in banda fiska, Shima ya wajaba ta rufe shi a gaban wadanda ba muharramanta ba.

**Wanda take tsakanin biyun:**

Ba wadanda suka gabata ba; Shi kuma an shardanta musu lullube abinda ya ke tsakanin cibiya zuwa guiwa. Kuma mustahabbi ne su sitirce kafadu biyu, har ma su yi ado (a lokacin salla).

### Sharadi na bakwai: Shigan lokaci

Salla bata inganta gabanin shigan lokacinta, haka bayansa; sai idan za a yi jam'inta tare da 'yar'uwarta idan da uzuri. Idan kuma ya yi gangancin jinkirta ta; ya fitar da ita daga lokacinta, to ya yi sabo.

**Sharadi na takwas: Fiskantar Alkiblah**

An togance daga hakan, sallar nafila a halin balaguro; a nan zai yi sallar duk inda dabbarsa ta fiskanta. A wannan zamanin kuma kamar yin salla a cikin jirgi. Haka shima wanda ya gaza fiskantar alkibla (jinya), ko ya ji tsoron makiya idan ya fiskance ta, suma an togance su.

**Sharadi na tara: Niyyah**

Mahallin yin niyya shine zuciya. Furta ta da harshe bidi'a ne. Koda niyyar ta gabata gabanin yin sallar da wani lokaci, ko kuma ya yi niyyar sauke farillar lokacin, to sallar ta inganta.

**Fadakarwa masu mihimmanci**

**1-** Ba a karbar jahilci a matsayin uzuri ko mantuwa ko ganganci wajen barin sharadi; saidai idan ya yi salla alhalin a jikinsa akwai najasa bai sani ba, ko ya manta, to sallarsa ta inganta, saboda yin salla da najasa (da jahilci) bari ne; ba aiki ba.

**2-** Sharudda su kan kasance ne a wajen ibada (ba cikinta ba), kuma dole su rigaye ta, haka, dole ne a cigaba da samunsu har zuwa karshen ibadar.

## DARASI NA BAKWAI

### *RUKUNNAN SALLAH*

*Rukunnan salla guda goma sha hudu:*

***1-** Tsayuwa matukar akwai iko**. 2-** Kabbarar harama. **3-** Karatun Fatiha.*

***4-** Ruku'u. **5-** Daidaituwa bayan ruku'u.*

***6-** Sujjada akan gabbai bakwai (7).*

***7-** Dagowa daga sujjada. **8-** Zama a tsakanin sujjadodi biyu.*

***9-** Natsuwa a cikin dukkan ayyuka. **10-** Jerantawa tsakanin rukunnan.*

***11-** Tahiyar karshe. **12-** Zama domin yin tahiyar karshe.*

***13-**Salati ga Annabi . **14-**Yin sallama guda biyu.*

**Rukunin farko:** Tsayuwa matukar akwai iko

### A SALLAR FARILLA:

Tsayuwa rukuni ne a sallar farilla. Idan Mutum ba zai iya tsayuwar ba kwata-kwata, ko kuma idan ya tsaya ba zai samu natsuwa ba, to ya sauka akansa.
Idan ya samu ikon tsayuwar koda a wani bangare ne na sallar to sai ya tsaya.

### A SALLAR NAFILA

Ya inganta idan ya yi sallar nafila a zaune, saidai zai samu rabin ladan wanda ya yi a tsaye ne. Idan kuma a kwance ya yi to zai samu rabin na wanda ya yi a zaune.

## Rukuni na biyu: Kabbarar harama

Babu wani lafazin da zai wadatar face fadin

"*Allahu Akbar*" Allah shine Mafi girma"

## Rukuni na uku: Karatun Fatiha

Wajibi ne karatun fatiha, da dukkan ayoyinta da wasalinta da kalmominta da harrufanta a kowace raka'a ta salla, sallar da ake boye karatu a cikinta ne ko wanda ake bayyanawa. Amma karatunta yana sauka idan ya riski Limami a cikin ruku'u.

## Rukuni na hudu: Natsuwa a cikin dukkan ayyukan sallah

Kuma natsuwarta wajibi tana tabbatuwa da fadin zikiri na wajibi a cikin kowane rukuni.

## FADAKARWA MAI MUHIMMANCI

Rukunnai suna kasancewa ne a cikin ibada. Kuma jahilci ko mantuwa ko ganganci basu zama uzuri wajen barin rukuni daya; daga cikin rukunnai. Kuma ba a yin sujjadar rafkanuwa domin gyara sallar da aka bar wani rukuni a cikinta. Kawai ana umutarsa da ya yi ramukon sallar da ake cikin lokacinta, Amma sallolinsa na baya wadanda ya bar wasu rukunnan, to za a masa uzuri; ba sai ya yi ramukonsu ba, saboda Annabi ﷺ bai umurci Mutumin da ya munana sallarsa da cewar ya maimaita dukkan sallolinsa na baya ba, kawai ya umurce shi ne da yin ramukon wanda ake cikin lokacinta, tare da cewa abinda ya barin natsuwa ne a sallah, wanda kuma rukuni ne. Allah shine Mafi sani.

## DARASI NA TAKWAS

### WAJIBAN SALLAH

**Wajiban sallah guda takwas ne:**

1- Dukkan kabbarori, in banda kabbarar harama (ta farko).

2- fadin : "Sami'alLahu liman hamidah": ga Limami da mai yin salla shi kadai.

3. Fadin: "Rabbana wa lakal hamdu": ga kowa (Limami, Mamu, Mai yi shi kadai).

4. Fadin: "Subhana Rabbiyal Azim" a cikin ruku'u.

5. Fadin: "Subhana Rabbiyal A'alah" a cikin sujjada.

6. Fadin: "Rabbig fir liy" a tsakanin sujjada biyu.

7. Tahiyar farko.

8. Zama domin tahiyar farko.

### FADAKARWA MAI MUHIMMANCI

Ya wajaba ya fadi *"Subhana Rabiyal Azim"* a cikin ruku'u da wannan lafazin. Daga nan mustahabbi ne ya kara da fadin sauran zikirorin da suka tabbata. Haka a sujjada, wajibi ne ya ce: *"Subhana Rabiyal A'alaa" da wannan lafazin,* sannan ya kara da sauran zikirorin (mustahabbi).

# DARASI NA TARA

## BAYANI GAME DA TAHIYA

Bayani kan Tahiya, Ita ce: ***"ATTAHIYYATU LILLAHI, WASSALAWATU, WADDAYYIBATU, ASSALAMU ALAIKA AYYUHAN NABIYYU WA RAHMATUL LAHI WA BARAKATUHU, ASSALAMU ALAINA WA ALA IBADIL LAHIS SALIHINA, ASH-HADU AN LA ILAHA ILLAL LAHU, WA ASH-HADU ANNA MUHAMMADAN ABDUHU WA RASULUHU"***. Sai ya yi salati ga Annabi ﷺ ya nema masa karin albarka, ya ce: ***"ALLAHUMMA SALLI ALA MUHAMMADIN WA ALA ALI MUHAMMADIN, KAMA SALLAITA ALA IBRAHIMA WA ALA ALI IBRAHIMA, INNAKA HAMIDUN MAJID. WA BARIK ALA MUHAMMADIN WA ALA ALI MUHAMMADIN, KAMA BARAKTA ALA IBRAHIMA WA ALA ALI IBRAHIMA INNAKA HAMIDUN MAJID"***. Daga nan, a tahiyar karshe sai ya nemi tsarin Allah daga azabar Jahannama, da azabar kabari, da fitinar rayuwa da mutuwa, da fitinar Dujjal. ***"ALLAHUMMA INNI A'UZU BIKA MIN AZABI JAHANNAMA, WA A'UZU BIKA MIN AZABIL KABRI, WA A'UZU BIKA MIN FITNATIL MAHYA, WAL MAMAT, WA A'UZU BIKA MIN FITNATIL MASIHID DAJJAL"*** (Bukhari da Muslim). Sai kuma ya yi addu'ar da yake so, musamman wadanda suka tabbata daga Annabi ﷺ . Daga cikinsu: ***"ALLAHUMMA A'INNIY ALA ZIKRIKA WA SHUKRIKA WA HUSNI IBADATIKA. ALLAHUMMA INNIY ZALAMTU NAFSIY ZULMAN KASIRAN, WALA YAGFIRUZ ZUNUBA ILLA ANTA, FAGFIR LIY MAGFIRATAN MIN INDIKA, WAR HAMNIY, INNAKA ANTAL GAFURUR RAHIM"***. A Tahiyar farko kuma, bayan ya yi tahiya zuwa: Abduhu wa rasuluhu, sai ya tashi zuwa ga raka'a ta uku, a sallar azahar da la'asar, da magriba, da isha. Idan ya kara da salati ga Annabi kuma shine yafi, saboda gamewar hadisan da suka zo akan haka. Sai kuma ya tafi zuwa ga raka'a ta uku.

## DARASI NA GOMA
### Sunnonin Sallah

Daga cikinsu, akwai:

**1-** Addu'ar bude sallah.

**2-** Dora tafin hannun dama akan na hagu, a saman kirji, a lokacin tsayuwa, gabanin ruku'u da bayansa.

**3-** Dagatafin hannaye biyu, daura da kafadu ko kunnuwa, 'yan yatsu a hade kuma a mike, yayin kabbarar farko, da lokacin yin ruku'u da dagowa daga ruku'u, da yayin mikewa daga tahiyar farko zuwa raka'a ta uku.

**4.** Fadin abinda ya karu akan sau daya na tasbihin ruku'u da sujjada.

**5.** Fadin abinda ya karu a kan *"Rabbana wa lakal hamdu"*, bayan dagowa daga ruku'u, da abinda ya karu akan fadin *"Rabig fir liy"* sau daya, a tsakanin sujjada guda biyu.

**6-** Sanya kai daura da baya, a lokacin ruku'u.

**7-** Nesanta damatsu biyu daga kuibi, da kuma ciki daga cinyoyi biyu, da kuma cinyoyin daga duga-dugai, a lokacin sujjada.

**8-** Dage zira'i biyu daga kasa, yayin sujjada.

**9-** Zaman mai sallah akan kafarsa ta hagu da take shumfude, da kafe kafar dama a lokacin tahiyar farko, da tsakanin sujjadodi biyu.

**10-** Zaman *tawarruk* a sallah mai raka'o'i hudu da uku, Sifarsa shine Mutum ya zauna akan mazauninsa na bangaren hagu, da sanya kafarsa ta hagu a karkashin ta dama, tare da kafe ta damar.

**11-** Nuni da manuniyar yatsa, a tahiyar farko da ta biyu, daga lokacin da ya zauna har zuwa karshen tahiyarsa, da karkada ta a lokacin yin addu'a.

**12-** Salati da neman karin albarka ga annabi Muhammadu da iyalan annabi Muhammadu, da kuma annabi Ibrahim da iyalan annabi Ibrahim, a tahiyar farko.

**13-** Yin addu'a, a tahiyar karshe

**14-** Bayyanar da karatu, a sallar asuba, da sallar juma'a, da sallolin idi biyu, da ta neman shayarwa (rokon ruwa), da kuma a cikin raka'oi biyun farko na sallar magriba da isha.

**15-** Boye karatu, a sallolin azahar da la'asar, da kuma raka'a ta uku ta magriba, da raka'oi biyun karshe na isha.

**16-** Karanta abinda ya karu akan Fatiha, daga surorin Alkur'ani.

Tare da kulawa da sauran sunnonin sallah wadanda suka tabbata; kari akan wanda muka ambata, Daga cikinsu akwai: Kari akan fadin: "RABBANA WA LAKAL HAMD" bayan dagowa daga ruku'u, ga Limami, da Mamu, da Mai yin sallah shi kadai, domin kara wani abu akan hakan shima sunnah ne. Da kuma dora hannaye biyu akan guiwoyi biyu, tare da bubbude tsakanin yatsu, a lokacin ruku'u; shima sunnah ne.

## Addu'ar bude sallah (Du'a'u listiftahi)

Akan yi addu'ar bude sallah ne, bayan an yi kabbarar harama, ta hanyar karanta abinda ya zo daga Annabi SAW, kamar fadinsa: *Allahumma ba'id bainiy wa baina khadayaya kama ba'adta bainal mashriki wal magribi. Allahumma nakkini min khadayaya kama yunakkas saubul abyadu minad danas. Allahumma igsilniy min khadayaya bil ma'i was salji wal barad.* Ma'ana: Ya Allah! Ka nesanta tsakanina da kurakuraina kamar yadda ka nisanta tsakanin mafudar rana da mafadarta, Ya Allah ka tsaftace ni daga kurakuraina kamar yadda ake tsaftace farin tufafi daga dauda. Ya Allah ka wanke ni daga kurakuraina da ruwa da kankara da raba. (Bukhari da Muslim). Ko ya ce:*"SUBHANAKAL LAHUMMA WA BI HAMDIKA, WA TABARAKAS MUKA, WA TA'ALAH JADDUKA, WA LA ILAHA GAIRUKA".*

# DARASI NA GOMA SHA DAYA

## ABUBUWAN DA SUKE LALATA SALLAH

**Abubuwan da suke bata sallah guda takwas ne:**

**1-** Yin magana da ganganci, tare da tunawa da sani. Amma wanda ya yi magana da mantuwa ko jahilci, sallarsa ba ta baci da aikata hakan ba.

**2-** Yin dariya. **3-** Cin abinci. **4-** Shan abin sha. **5-** Yayewar al'aura.

**6-** Karkacewa mai yawa daga bangaren alkibla. **7-** Wasa mai yawa a jere a cikin sallah. **8-** Karyewar alwala.

**Mai lalata sallah na daya:** Yin magana da ganganci tare da tunawa da sani
An togance daga haka, Lamarin tunatar da Limami idan ya yi rafkanuwa ko ya yi kuskure a cikin karatu.

### Nau'ukan motsi a cikin sallah

| Motsi Na Haram | Motsi Na Makruhi (abin ki) | Motsi Na Halal | Motsi Na Mustahabbi | Motsi Na Wajibi |
|---|---|---|---|---|
| **Motsi Na Haram:** Shine motsi mai yawa a jere, ba tare da bukata ba, kamar cin abu. | **Motsi Na Makruhi (abin ki):** Shine motsi kadan, ba tare da bukata ba, kamar juyawa kadan. | **Motsi Na Halal:** Shine motsi a yayin bukata, kamar ya sosa gemun sa. | **Motsi Na Mustahabbi:** Shi ne wanda kamalar sallah yake rataya akanta, kamar ya motsa domin toshe kafa a cikin sahu. | **Motsi Na Wajibi:** Shine ingancin sallah yake ratayuwa akansa, kamar motsawa don gusar da najasa. |

## Fadakarwa mai muhimmanci

Menene banbanci tsakanin sharuddan sallah, da rukunanta, da wajibanta, da sunnoninta?

<table>
<tr><th>SHARADI</th><th>RUKUNI</th><th>WAJIBI</th><th>SUNNAH</th></tr>
<tr><td>Yana wajen ibada</td><td colspan="3">Suna cikin ibada</td></tr>
<tr><td>Ya kan cigaba a cikin dukkar ibadar</td><td colspan="3">Suna takaita da sashe daga cikin sassar ibadar</td></tr>
<tr><td colspan="2">Ba za a maka uzuri ka bar su ba, saboda, jahiltarsu, ko mantuwa, ko ganganci (dole sai an zo da su).</td><td>An yi uzuri idan baka yi shi ba saboda jahilci ko mantuwa, banda ganganci.</td><td>Ana uzuri ga wanda ya bar sunnar salla, da jahilci ko mantuwa ko ganganci.</td></tr>
<tr><td>Ba a yi wa sharadi sujjadar rafkanuwa</td><td>Ba a magance matsalar barin rukuni da sujjadar rafkanuwa.</td><td>Wajibi ana magance shi, da yin sujjadar rafkanuwa</td><td></td></tr>
</table>

## SUJADAR RAFKANUWA

Sabubban sujjadar rafkanuwa guda uku ne:

**Kari:**

Kamar Mutum ya kara ruku'u ko sujada ko tsayuwa ko zama.

**Ragi:**

Kamar Mutum ya rage wajibi daga cikin wajiban sallah, sai ya wuce mahallin yinsa.

**Shakka:**

Kamar ya yi taraddadi kan raka'o'i nawa ya yi; uku ne ko hudu. Wannan nau'i biyu ne:

**Yin shakka bayan gama ibada:**

Wannan kwata-kwata ba a waiwaitarsa, Saidai idan ya samu yakini (100%).

**Shakka a cikin ibada:**

Idan shakka ta yawaita a wurinsa ba zai karkata gare ta ba. Idan kuma kadan ce, sai ya gina akan abinzatonsa ya rinjaya a gare shi. Idan bangarori biyun suka daidaita sai ya gina akan mafi karanci.

**Abin Lura**

-Idan Mai sallah ya yi rafkanuwa a cikin sujjadar rafkanuwa, to babu komai akansa, kuma sallarsa ta inganta.

-Idan Mai sallah ya bar *rukuni*, to sallar ba zata inganta ba, har sai ya zo da shi, da kuma abinda yake bayansa, sannan ya yi sujjadar rafkanuwa.

-Idan Mai sallah ya bar *wajibi* da mantuwa, ya tsallake gurbin yinsa, to sai ya yi sujjadar rafkanuwa.

## SIFAR SALLAH a takaice a cikin fotuna

-Daga farko, Musulmi zai yi tsarki da alwalarsa a gidansa, ya sanya mafi kyan tufafi.

- Sai ya tafi zuwa Masallaci - ko ya hau abin hawa - cikin yanayi na natsuwa, kada ya yi gudu ko ya yawaita waiwaye.




- Idan ya isa Masallaci sai ya cire takalmansa ya sanya su a wurin da aka kebe musu, sai kuma ya ajiye Duniya tare da su; don haka haramun ne ya yi saye da sayarwa da cikiyar abinda ya bace a cikin Masallatai.

- Ya gabatar da kafar dama yayin shiga yana mai cewa: ***"BISMILLAHI, WASSALATU WASSALAMU ALA RASULILLAH, ALLAHUMMAF TAH LIY ABWABA RAHMATIK"***. A lokacin fita kuma sai ya gabatar da kafar hagu; ya ce: ***"BISMILLAH, WASSALATU WASSALAMU ALA RASULILLAH, ALLAHUMMA INNI AS'ALUKA MIN FADLIK".***

- Sai Maza su matsa zuwa sahun farko, Mata kuma su tafi baya.

- Idan an shiga sallah, to sai ya yi kabbarar harama ***'Allahu Akbar'*** ya kuma jona tare da Limamin a kowane hali Limamin yake ciki. Kuma zai samu raka'a ne idan ya samu limamin a tsaye ko a halin ruku'u, Idan Limamin ya sallame daga salla sai ya rama abinda ya kubce masa.


- Idan kuma ya shiga Masallaci alhalin ba a shiga sallah ba, sai ya yi nafilar gabanin sallah, Idan kuma sallar bata da sunnar da take rigayarta, sai ya yi raka'oi biyu na gaisuwar Masallaci, gabanin ya zauna.
- Kada ya keta alfarmar Masallaci, yana ta duba agogo, ko gyaran murya wai don neman a tayar da sallah.
- Sunna ne, Liman, da Mai yin Sallah shi kadai su yi sallah zuwa ga sutrah. Kuma sutran Limami ita ce sutran wadanda suke bayansa.




- A tsayuwarsa ya sanya tsakanin duga-dugansa biyu kamar tsakanin kafadunsa, kada ya kara kada ya rage, kuma ya dai daita wajensu.



- Bayan ya zo da dukkan sharuddan sallah, sai ya ce: "*Allahu Akbar*" tare da daga hannaye biyu yatsunsu a hade, zuwa setin kunnuwa ko kafadu biyu, ya kuma sanya cikin tafin hannayensa biyu su fiskanci alkibla.



- Sannan ya yi (wada'u); wato ya sanya cikin hannun dama, akan tafin hannun hagu, da wuyan hannu, da tsintsiyar hannu. Ko ya yi kabalu.



- Ya sanya kallonsa a wurin sujjadarsa, kuma kada ya yi waiwaye.



- Mustahabbi ne ya karanta "**Addu'ar bude sallah"** a raka'ar farko kawai; Kuma abinda yafi shine ya rika nau'intawa tsakanin addu'o'in da suka zo a sunnah "Addu'oin bude sallah".
- Sai ya yi addu'ar neman tsari, da abinda ya tabbata a sunnah: "AUZU BILLAHI MINAS SHAIDANIR RAJIM".
- Sai ya karanta *Fatihah;* a jere, da wasalinta, da kalmominta, da harrufanta, da ayoyinta.
- Sannan mustahabbi ne ya karanta abinda ya sawwaka na Alkur'ani (surori), ba tare da ya yi a'uzu ba, kuma zai yi Bismillah ne a farkon surori kawai.
- Sannan ya daga hannayensa kamar yadda ya daga su a lokacin kabbarar harama yana mai cewa: "*Allahu Akbar"* sai ya tafi ruku'u.
- Sai ya kama guiwowinsa biyu, ba zai lankwashe guiwar hannaye ba. Kuma ya sanya bayansa ya daidaitu da kansa.
- Kuma wajibi ne ya fada sau daya: "SUBHANA RABBIYAL AZIM". Mustahabbi ne ya kara abinda ya tabbata akan haka.



- Sannan, a lokacin da yake dagowa gabanin ya gama daidaituwa zai ce: **"SAMI'AL LAHU LIMAN HAMIDAHU"** tare da daga hannayensa daura da kunnuwansa, ko kafadunsa biyu.
- Idan ya gama daidaituwa, sai yace: **"RABBANA WA LAKAL HAMD"**. Kuma mustahabbi ne, ya kara daga zikirorin da suka tabbata a sunnah.
- Sai ya ce **"ALLAHU AKBAR"** ba tare da ya dago hannaye ba, sai ya yi sujjada akan gabbai bakwai: Goshi da hanci, da cikin tafukan hannaye biyu, da guiwowi biyu, da cikin yatsun kafofi biyu.
- Ya nesanta tsakanin hamatansa biyu, da tsakanin ciki da cinya, da tsakanin cinya da kwabri, kuma ya daga zira'insa biyu daga kasa.



- Sai ya ce: **"SUBHANA RABBIYAL A'ALAH"** sau daya, kuma wajibi. Kuma an so ya yi kari da fadin abinda ya tabbata a sunnah. Kuma yana da damar ya roki Allah dukkan abinda yake so, musamman addu'o'in da suka tabbata.
- Sai ya ce: "*Allahu Akbar"* ya kuma zauna akan kafarsa ta hagu wanda take shumfude, ya kuma kafe ta dama, ya sanya cikin yatsun kafar dama akan kasa, kuma yatsunsa suna fiskantar alkibla. Sai kuma ya sanya cikin tafin hannu biyu a karshen cinyoyinsa biyu. wannan shine zaman da zai rika yinsa a dukkan zaman cikin sallah, sai dai a sallah mai raka'o'i uku da hudu, a tahiyar karshe zai yi zaman *tawarruk;* wato ya sanya kafarsa ta hagu a karkashin sarangalin kafar dama.



- Sai ya ce: "*Allahu Akbar*" ya tafi sujjada, kamar yadda ya yi sujjadar farko.
- Sai ya ce: "*Allahu Akbar*" ya kuma tashi domin raka'a ta biyu, kuma zai aikata irin abinda ya aikata a raka'ar farko, sai dai raka'a ta biyu babu kabbarar harama a cikinta, kuma babu addu'ar bude sallah.
- Idan ya gama sujjada ta biyu, sai ya yi zaman tahiya.
- Sai kuma ya yi nuni da yatsarsa da yake tasbihi (manuniya), ya kuma lankwashe yatsarsa ta tsakiya da babbar yatsa, yana motsa manuniyar, kuma yana addu'a.
- Zai karanta addu'ar tahiya, kuma wajibi ne.
- Idan sallar mai raka'o'i biyu ce, to wajibi ne ya yi salatin Annabi (irin na Annabi Ibrahim), ya kuma nemi tsarin Allah daga abu hudu: Azabar Jahannama, da azabar kabari, da fitinar Dujjal, da fitinar rayuwa da mutuwa.

Sai kuma ya roki bukatar da yake so, sai dai abinda yafi shine ya yi addu'a da abinda ya zo a hadisi, kamar ya ce: "Ya Allah ka taimake ni akan zikirinka, da godiya a gare ka, da kyautata bauta a gare ka".



- Sai ya yi sallamomi biyu; ta damansa da hagu, yana juya kansa kawai; banda kafadunsa biyu, kuma ba tare da ya motsa kansa da sama ba, kuma ba tare da ya yi nuni da hannayensa ba.



- Idan sallar mai raka'o'i uku ce ko hudu, sai ya tashi bayan ya gama karatun tahiyar farko, kuma itama mustahabbi ne ya yi salati irin na Annabi Ibrahim.
- Yace: "*Allahu Akbar"* sai ya sallaci raka'a ta uku ya zauna zaman tahiya idan sallar mai raka'o'i uku ce, idan kuma hudu ce, sai ya karo ta hudu gabanin ya yi zaman tahiyar karshe.
- Zai karanta tahiyar, ya kuma yi salati irin na Annabi Ibrahim, ya nemi tsarin Allah daga abu hudu: "ALLAHUMMA INNI A'UZU BIKA MIN AZABI JAHANNAM, WA A'UZU BIKA MIN AZABIL KABR, WA A'UZU BIKA MIN FITNATIL MASIHID DAJJAL, WA A'UZU BIKA MIN FITNATIL MAHYA WAL MAMAAT". Zai kuma roki bukatarsa, amma an fi son addu'ar da ta tabbata a sunnah, tare da fadin: ALLAHUMA A'INNI ALA ZIKRIKA, WA SHUKRIKA, WA HUSNI IBADATIKA.
- Idan sallar farilla ce, to Mustahabbi ne ya karanta zikirorin da suka tabbata a bayan salla, Wato: Ya ce: *AstagfirulLah, AstagfirulLah, AstagfirulLah, ALLAHUMMA ANTAS SALAMU WA MINKAS SALAMU, TABARAKTA YA ZAL JALALI WAL IKRAM.*
- Sa'annan ya ce: "SubhanalLah, Alhamdu lilLah, Allahu Akbar" kowanne sau 33, gaba daya sau 99. Sai ya cika da fadan *"LA ILAHA ILLAL LAHU WAHDAHU LA SHARIKA LAHU, LAHUL MULKU, WALAHUL HAMDU, WA HUWA ALA KULLI SHAI'IN KADIR.*
- Sai ya karanta *Ayatul Kursiy, Suratul Ikhlas, Suratul Falak, da Suratun Nas.*

## Fadakarwa masu muhimmanci

- Mun gabatar cewa, *suturce al'aura* yana cikin sharuddan ingancin sallah, don haka Mai sallah wajibi ne ya kiyaye budewar al'aurarsa a cikin sallah, domin kada sallarsa ta baci.



- Idan Mamu zai yi salla da Limaminsa, to zai tsaya ne ta damansa, kuma za su daidaita idonun sawunsu; kada ya yi gaba da shi, ko baya. Haka Mutum yake tsayuwa tare da sauran masu sallar da suke yi a tare.



## SALLAH a takaice

| Sunanta | Hukuncinta | Lokacinta | Raka'o'inta | Bayanin sifarta |
|---|---|---|---|---|
| SALLAR JUMA'A | Farilla ce | Lokacin azahar | 2 | Sallar Juma'a a bayyane ake yinta, kuma ana yinta da jama'a ne; wato Mutane uku ko abinda yafi haka. |
| SALLAR KISFEWAR RANA KO WATA | Farilla ce ta kifaya | Lokacin da aka samu kisfewar. | 2 | Sallar kisfewar rana ko wata, ana yinta a bayyane, kuma ruku'u biyu ake yi a cikin kowace raka'a. |
| SALLAR WUTRI | Sunnah ce mai karfi | Daga bayan isha har zuwa asuba | Daga Raka'a I zuwa II | Tana kasancewa ko raka'a **1**, ko raka'oi **3** a hade sai ya zauna a karshenta domin yin tahiya, ko ya yi raka'a 2 sai ya yi sallama, sai kuma ya kara raka'a daya. Ko raka'o'i **5** wanda zai zauna ya yi tahiya a karshensu. Ko raka'oi **7** wanda zai zauna don tahiya a raka'a ta bakwai. Ko raka'oi **9** wanda zai zauna ya yi tahiya a raka'a ta 8, sannan ya tashi zuwa ta 9 ba tare da ya yi sallama ba, sai bayan ya kare raka'a ta 9. Ko kuma duk bayan raka'o'i biyu ya yi sallama, sai ya yi wutiri da guda daya a karshe. |

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| **RAKA'A-TAYIL FAJR** | Sunnah ce mai karfi | Gabanin sallar asuba | 2 | A raka'ar farko Mutum zai karanta *Kul ya ayyuhal kafiruna*, a raka'a ta biyu kuma: *Kul huwal Lahu ahad* |
| **SUNNAR AZAHAR** | Sunnah ce abar so | Raka'oi hudu kafin sallar azahar, da biyu bayanta | 4/2 | Rako'i bibbiyu a rabe |
| **SUNNAR MAGRIBA** | Sunnah ce abar so | Bayan Magriba | 2 | A raka'ar farko Mutum zai karanta *Kul ya ayyuhal kafiruna*, a raka'a ta biyu kuma: *Kul huwal Lahu ahad* |
| **SUNNAR ISHA** | Sunnah ce abar so | Bayan Isha | 2 | |
| **TARAWIH** | Sunnah ce abar so | Daga bayan Isha zuwa Asuba | Daga raka'o'i 2-10 | |
| **GAISUWAR MASALLACI** | Wajibi | Kafin zaman mutum a Masallaci | 2 | |
| **SALLAR WALAHA** | Sunnah ce abar so | Daga lokacin da rana ta daga har zuwa kusa da zawali | Daga raka'o'i 2-8 | |

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| **SALLAR ISTIHARA (neman zabin Allah)** | Sunnah ce abar so | ko yaushe | 2 | Zai yi addu'ar neman zabin Allah gabanin ya yi sallama. |
| **SALLAR NEMAN SHAYA-RWA/ ROKON RUWA** | Sunnah ce a lokacin bukatuwa ga hakan. | Daga lokacin da Rana ta daga, dai dai da kan Mashi. | 2 | A raka'ar farko, zai ce, "Allahu Akbar" sau 7, tare da kabbarar harama. Sai kabbarori 5 a raka'a ta biyu, kari akan kabbarar dagowa. Kamar yadda ake yi a sallar idi. |
| **SALLAR IDI BIYU** | Sunnah ce abar so | Daga lokacin dagowar Rana dai dai da kan Mashi. | Raka'o'i 2 da Hudubobi 2 | A raka'ar farko, zai ce, "Allahu Akbar" sau 7, tare da kabbarar harama. Sai kabbarori 5 a raka'a ta biyu, banda kabbarar dagowa. |

**Lokutan hani kan nafilfili mudlakai (wadanda basu da sababi):**

1) Daga sallar Asuba, har zuwa Rana ta dago, daidai da kan Mashi.

2) Daga sallar La'asar zuwa faduwar Rana.

3) Daga takewar Rana har zuwan lokacin da zata yi zawali.

## TAMBAYOYI AKAN SALLAH

1. Nawa ne adadin *sharuddan salla*? O 9 O 11 O 8

2. Sanya *Musulunci* daga cikin *sharuddan sallah* kuskure ne, saboda babu mai sallah sai Musulmi ( Haka – A'a ).

3. Iya banbance abubuwa (*tamyiz*) shine lokacin balagar yaro ( Haka – A'a).

4. Gusar da hadasi ya hada da, jiki, wuri, da tufafi ( Haka – A'a ).

5. Najasar *alade* najasa ce: O Mai tsanani O matsakaiciya

6. *Maniyyi* najasa ne, saboda idan ya fito sai mun yi wanka ( Haka – A'a ).

7. Babu banbanci tsakanin yayyafa ruwa (ga najasa) da wankewa ( Haka – A'a ).

8. Matattun dabbobi gaba dayansu najasa ne (Gaskiya ne – A'a).

9. Za a tsarkake kwano mai najasar kare koda ba da kasa ba, kamar omo ( Haka – A'a ).

10. Abinda katange kai daga gare shi yake wahalarwa, shine abinda yake yawaita shiga da fita, don haka kuliya zata iya zama mai tsarki ga wasu Mutane, wasu kuma najasa ( E – A'a ).

11. Dabbar da bata da jini a jiki dake gudana; ita ce wanda bata da rai ( E – A'a ).

12. Jinin da ya saura a cikin jijiya... O Najasa ne O Mai tsarki ne

13. Nawa ne adadin *rukunnan sallah*? O 14 O 9 O 8

**14.** Kabbarar harama itace daga hannaye biyu ( E – A'a ).

**15.** Idan Mutum ya bar *rukunin sallah* da rafkanuwa, to sai ya yi sujjadar rafkanuwa, kawai ( E – A'a ).

**16.** Nawa ne adadin wajiban sallah? O 8 O 14 O 9

**17.** A sujjadarsa ya ce: "*SUBBUHUN KUDDUSUN RABBUL MALA'IKATI WAR RUH*" idan ya san wajibi ne a ce: *"Subhana Rabiyal a'lah"* sau daya, to sallarsa ta baci (E – A'a ).

**18.** A sallah an shar'anta ya sanya cikin tafin hannunsa na dama akan saman tafin hagu da wuyan hannu da tsintsiyar hannu ( E – A'a ).

**19.** Bayyana karatu yana kasancewa ne, a raka'o'i biyun farko na farillar da ake yi da dare, da duk sallah mai raka'a biyu, wanda aka shar'anta haduwar jama'a; kamar idi (E – A'a ).

**20.** Nawa ne adadin abubuwan da suke bata sallah? O 8 O 9 O 14

**21.** Tawarruk wato sanya kafar hagu karkashin ta dama, da zama akan mazaunin **hag**u, yana kasancewa ne a tahiyar---- O Farko O Karshe O Gaba daya.

**22.** Kara lafazin "*WasShukr*" ga *"Rabana lakal hamd wasShukr"* hukuncinsa…
O Halal ne O Mustahabbi O Haramun.

**23.** Fadin: "*Rabbig fir liy wa li walidayya*" a tsakanin sujjada biyu…
O Halal ne. O Haram ne. O Makaruhi.

**24.** Sanya guiwowin hannu akan kasa, a sujjada…
O Haram ne. O Mustahabbi ne. O Makaruhi.

**25.** Sabubban sujjadar rafkanuwa guda nawa ne? O 2 O 3 O 4.

**26.** Yin shakku bayan gama aiki bashi da tasiri,Haka idan shakka ta yawaita (Haka – **A**'a )

**27.** *Raka'atayil Fajr* sun banbanta da sauran rawatib (nafiloli) a: falala, saurin kammalawa, karanta kebantattun surori, yinta koda Mutum yana halin bulaguro, da kuma kishingida bayan gama ta, matukar a gida aka yi ta ( E – A'a ).

**28.** Ambaci hukuncin mas'alolin da suke tafe:

| Mas'ala | Hukunci |
|---|---|
| Sallar Mutumin da yake zagin addini | |
| Sallar wanda yake cikin maye | |
| Sallar mai cutar Zahayimr | |
| Sallar karamin Yaro | |
| Wanda ya yi sallah babu alwala, da mantuwa | |
| Wanda ya yi sallah da tufa mai najasa, da mantuwa | |
| Fitsarin saniya | |
| Fitsarin hankaka | |
| Wanda ya yi sallah cinyoyinsa biyu a bude | |
| Wanda ya yi sallah kafin shigan lokaci, da mantuwa | |
| Yin sallah a cikin jirgi | |
| Wanda ya yi niyyar farillar wannan lokacin (bai ayyana ba) | |
| Wanda ya yi sallah a zaune | |
| Ya manta bai karanta Fatihah ba | |

| | |
|---|---|
| Ya samu Limaminsa yana cikin ruku'u | |
| Yin sauri a cikin sallah | |
| Mai yawan shakkun da ya yi shakka bayan kammala sallah | |
| Yin shakka akan alwalarsa bayan kabbarar harama | |
| Ya kara ruku'u da rafkanuwa | |
| Ya manta bai yi kabbarar harama "Allahu Akbar" ba | |
| Ya manta tahiyar farko | |
| Wanda ya manta tahiyar karshe | |
| Ya yi shakka; shin raka'o'i uku ya yi ko hudu | |
| Ya yi shakka bayan gama sallarsa | |
| Ya yi shakka yana tsakiyar sallarsa | |
| Ya yi rafkanuwa alhali yana cikin sujjadar rafkanuwa | |
| Ya yi magana a cikin sallarsa da mantuwa | |
| Ya yi sallah alhalin al'aurarsa tana bude, amma bai san da hakan ba sai bayan ya gama | |
| Yin alwala a gida, gabanin fitowa sallah. | |
| Sayar da abu, a Masallaci. | |
| Kasuwancin canjin kuḍaḍe a Masallaci. | |
| Ya riski Limaminsa alhalin yaṇa tahiyar karshe | |
| Sanya sitra da fiskantartạ a cikin sallah. | |
| Karamin motsi (juyawa kadaṇ) a cikin sallah. | |

| | |
|---|---|
| Jujjuyawa ḍayawa. | |
| Ya bubbuga sallar ḍa gaggawa | |
| Yin salatin Annabi Ibrahimạ a cikin Sallah. | |
| Yin magana a ciḳin sallah. | |
| Motsawa a ciḳin Sallah. | |
| Ya mance karatun Fatiha. | |
| Sallar Juṃa'a. | |
| Sallar ẉutiri. | |
| Yin sallah kafin zama a Masallaci (gaisuwar Ṃasallaci). | |

**29. Fadi banbance-banbancen da suke tsakanin Sharadi, Rukuni, Wajibi, da Sunnah**

| Sharadi | Rukuni | Wajibi | Sunnah |
|---|---|---|---|
| | | | |
| | | | |
| | | | |
| | | | |

## Darasi na Goma Sha Biyu

### SHARUDDAN ALWALA

**Sharuddan Alwala, guda goma ne:**

**1-** Musulunci. **2-** Hankali. **3-** Tantancewa (Tamyizi). **4-** Niyya. **5-** Lazimtar hukuncinta; wato kada ya yi niyar yanke alwalar har kammaluwarta **6-** Yankewar abubuwan da suke lazimta yin alwala. **7-** Yin tsarki da ruwa ko da duwatsu gabanin yin alwalar. **8-** Tsarkin ruwan, da kasancewarsa na halal. **9-** Gusar da duk wani abinda zai hana isar ruwa ga fata. **10-** Shigan lokaci; ga Mutumin da koyaushe yana cikin hadasi.

### SHARHIN WASU SHARUDDAN

- Fadinsa: "Lazimtar hukuncinta; wato kada ya yi niyar yanke alwalar har kammaluwarta": yana nufin niyyarsa ta alwala, ta cigaba tun daga farkon alwalar har karshenta.
- Fadinsa: "Yankewar abin da yake lazimta alwalar": Ma'ana, kada Mutum ya yi alwala, alhalin yana cikin cin naman rakumi, ko kuma yana tsakiyan fitsari, kenan, dole sai an samu yankewar abinda yake warware alwala gabanin fara ta.
- "Yin tsarki da ruwa ko da duwatsu gabanin yin alwalar": An togance daga haka, idan sababin alwalar ya zama tusa ne (ba sai ya yi tsarki ba), ko barci, ko cin naman rakumi.

- Fadinsa: "Tsarkin ruwan, da kasancewarsa na halal": yana nufin, ba a yin alwala da ruwa mai najasa, ko wanda aka yi kwacensa.
- Fadinsa: "Gusar da dukkan abinda zai hana isar ruwa ga fata": kamar kwababben gari, ko jan farce, domin suna hana isar ruwa ga gaba.

## Sunnonin Fidira

**Daga cikin sunnonin fidira (da suke nuna tsaftar Musulunci) akwai:**

**1. Kaciya:** Wajibi ce ga Maza. Sunnah ga Mata, matukar akwai bukata.

**2 - 5 Rage gashin baki, yanke farce, tuzge gashin hamate, aske gashin gaba:** An ruwaito daga Anas- Allah ya yarda da shi yace: **"Ya sanya mana lokaci, dangane da rage gashin baki, da yanke farce, da tuzge gashin hamata, da aske gashin gaba, cewa kada mu bar hakan fiye da kwanaki arba'in".** Wannan ya nuna cewa, bai dace ka jinkirta wadannan al'amuran su wuce kwanaki arba'in ba.

**6- Barin gem**u: Ajiye gemu wajibi ne, aske shi kuma laifi ne babba daga cikin manyan zunubai.

**7- Asiwaki:** Shine yin amfani da itace ko makamancinsa wajen tsaftace hakora. Hukuncinsa sunnah ne a kowane lokaci, sai dai yana kara karfi (sunnah mu'akkada), a lokacin yin alwala, da sallah, da shiga gida, da karatun Alkur'ani, da tashi daga barci, da lokacin canjin warin baki, da lokacin rasuwa.

## Darasi na Goma Sha Uku

# FARILLAN ALWALA

**Farillan Alwala, Guda shida ne:**

**1-** Wanke fiska, daga cikinsa kurkuran baki da shaka ruwa, suke.

**2-** Wanke hannaye biyu, tare da guiwoyin hannu.

**3-** Shafar kai gaba daya, daga jikinsa akwai kunnuwa biyu.

**4-** Wanke kafofi biyu, tare da idon sawu biyu.

**5-** Jeranta gabban (jeranta farillan).

**6-** Gaggautawa.

Mustahabbi ne maimaita wanke fiska, da hannaye biyu, da kafofi, sau uku. Haka kurkuran baki da shaka ruwa a hanci. Farillar itace wankewar farko. Amma shafar kai, ba a sunnanta maimaita ta ba, kamar yadda hadisai ingantattu suka nuna.

**TABBATAR DA GAGGAUTAWA A CIKIN ALWALA**

Yana kasancewa; ta yadda Mai alwala ba zai jinkirta wanke gabarsa, har gabar da take gabaninta ta bushe ba.

# Darasi na Goma Sha Hudu

## ABUBUWAN DA SUKE WARWARE ALWALA

**Abubuwan da suke warware alwala guda shida ne:**

**1-** Abinda yake fita ta dayan hanyoyi biyu. **2-** Da abinda ya fita dayawa mai najasa daga jiki. **3-** Gushewar hankali, saboda barci ko waninsa. **4-** Shafan farji, da hannu, gaba ne ko baya, ba tare da shamaki ba. **5-** Cin naman rakumi. **6-** Ridda da barin Musulunci.

**Fadakarwa mai muhimmanci:**

Amma **Wanke Matacce:** Ga magana ingantacciya, to lallai baya lalata alwala. Kuma wannan shine maganar mafi yawan Malamai; saboda babu wani dalili akan hakan. Saidai da hannun Mai wanke gawar zai taba al'aurar mamacin ba tare da shamaki ba, to a nan wajibi ne ya sake alwala. Kuma ya wajaba akansa kada ya taba al'aurar matacce, face ta bayan shamaki.

Haka shima al'amarin, Shafar Mace baya warware alwala a kowane hali, sawa'un da sha'awa ko babu sha'awa ya shafe ta, a maganar da tafi inganci daga cikin maganganun Malamai guda biyu; matukar wani abu bai fito daga gare shi ba. Saboda Annabi ﷺ ya sumbanci wata daga cikin matansa, sa'annan ya yi sallah ba tare da ya sake alwala ba. Amma fadin Allah SWT: "Ko idan kuka shafi Mata" manufar ita ce: kuka yi jima'i da su, a maganar da tafi inganci daga cikin maganganun Maluma guda biyu, kuma wannan ita ce maganar Abdullahi dan Abbas –Allah ya yarda da su- da wasu jama'a daga cikin magabatan kwarai, da wadanda suka zo a bayansu.

**Sharhin sashen abubuwan da suke warware alwala**

Fadinsa: "Abinda ya fita ta dayan hanyoyi biyu" mudlakan: Misalin fitsari, kashi, maniyyi, maziyyi, wadiyyi, tusa, duwatsu, jini, tsutsa, haila, da kuma jinin haihuwa (nifasi).


- Fadinsa: "abinda ya fita dayawa mai najasa daga jiki": Magana mafi rinjaye, hakan baya warware alwala, saidai idan abinda ya fitan daga jinsin fitsari ko kashi ne.

- Fadinsa: "Gushewar hankali, saboda barci ko waninsa": Barci a karan kansa baya warware alwala, saidai yanayi ne na fitar tusa, don haka, idan Mutum ya ji a ransa cewa babu abinda ya fita daga jikinsa, to lallai alwalarsa bata warware ba.

- Fadinsa: "Shafar farji, da hannu, gaba ne ko baya, ba tare da shamaki ba": Ibn Taimiyyah –Allah ya yi masa rahama- ya rinjayar da maganar cewa; wanda ya shafi al'aurarsa, mustahabbi ne ya maimaita alwala; ba wajibi ba.

## SIFAR ALWALA a takaice a cikin fotuna

- Idan Mutum ya yi niyyar alwala, lallai an shar'anta masa ya ce: « Bismillah »
- Sa'annan ya wanke tafin hannayensa sau uku, ta hanyar zuba musu ruwa.
- Sannan ya kamfaci kamfacen ruwa da hannun damansa ya kuskuri bakinsa da shi, tare da jujjuya ruwan a cikin bakinsa tare da furzar da shi. Sannan ya shaki ruwa a cikin hancinsa, sai kuma ya fyace, ta hanyar sanya manuniyarsa da babbar yatsa akan hancinsa, zai maimaita hakan sau uku.
- Sannan ya wanke fiskarsa sau uku, tsawonsa shine daga wurin da gashi yake tsirowa ga al'ada, har zuwa wurin da gemu da haba suke karewa. Fadinsa kuma shine tsakanin kunnuwa biyu.
- Sannan ya wanke hannayensa biyu, tare da guiwowin hannu sau uku, zai fara da hannun dama, sannan hagu.
- Sai ya shafi kai yana mai tafiyar da hannayensa daga gaban kansa, har zuwa keya, sannan ya komo.
- Sannan ya sanya manuniyarsa biyu cikin fatan kunnuwansa, ya shafe su.
- Sai kuma ya wanke kafofinsa biyu, tare da idon sawu, sau uku.









- Kuma sai ya ce bayan gama alwala: «*ASH-HADU AN LA ILAHA ILLAL LAHU WAHDAHU LA SHARIKA LAHU, WA ASH-HADU ANNA MUHAMMADAN ABDUHU WA RASULUHU*». A cikin littafin Tirmiziy « *YA ALLAH KA SANYA NI DAGA CIKIN MASU YAWAN TUBA, KUMA KA SANYA NI DAGA CIKIN MASU YAWAN TSARKAKA» Ma'ana: ALLAHUMMAJ ALNIY MINAT TAWWABINA, WAJ ALNIY MNAL MUTADAHHIRINA.*

**Hukuncin kari akan gwargwadon da aka shar'anta**

Bai halatta Mutum ya kara akan gwargwadon da aka shar'anta a cikin alwala ba; kamar karawa akan wankewa sau uku, ko ya wanke abinda yake sama da guiwar hannu; na damtse, ko saman idanun sawu; kwabri, ko kuma ya yi shafar wuya (kari akan shafar kai)



## Farko: Dahara

### TAIMAMA:

Ita madadi ce na tsarkin ruwa, idan ya gagara a yi amfani da ruwa a gabban alwala ko wanka, ko sashensu; saboda rashin ruwan, ko kuma idan aka ji tsoron cutuwa idan an yi amfani da ruwa, sai turbaya ta tsaya a madadin ruwa.

### SIFAR TAIMAMA:

Zai yi niyyar taimama, sai ya ce: BismilLahi. Sai ya bugi kasa sau daya. Sannan ya shafi fiskarsa da bayan tafukan hannayensa, da cikin tafukansa



Ba a shar'anta bubbuda yatsu ba, lokacin bugun turbayar, ko kuma tsettsefe yatsu; wajen shafar tafukan hannu



## Sifar wanka na wajibi

Ya yi niyyar wanka da dauke janaba, sai ya ce: BismilLah. Sai ya game gaba dayan jikinsa da ruwa, da kuma abinda yake karkashin gashinsa kadan ko mai yawa, tare da kurkurar baki, da shaka ruwa a hanci.

## Sunnah a al'amarin wanka

Wanke al'aurarsa guda biyu (gaba da baya), sannan hannayensa, sai ya yi alwalarsa irin ta sallah, ya kuma kosar da gashin kansa da ruwa, sai ya wanke gefen jikinsa na dama, sa'annan sai gefen hagu, sa'annan ya wanke kafofinsa biyu.

## Abubuwan da suke wajabta wanka

- **Janaba:** Tana kasancewa idan maniyyi ya fita, sakamakon jima'i, ko waninsa, ko saboda haduwar kaciyar Namiji da Mace. **2.** Fitan jinin haila da na haihuwa. **3.** Mutuwa ba ta hanyar shahada a yaki ba. **4.** Musuluntar kafiri.

## Sharuddan yin shafa akan huffi

Ya sanya huffin bayan cikar tsarki, wato ya kasance ya wanke kafofin biyu da ruwa, a alwala.

Huffi ko safar, su kasance masu tsarki.

Shafarsu ta kasance a karamin hadasi, ba ga janaba, ko abinda yake wajabta wanka ba.

Su kasance sun rufe mafi yawan kafar.

Shafar ta kasance a cikin lokacin da shari'a ta iyakance; wato yini da kwana ga wanda ba mai bulaguro ba (awa 24). Ko kwanaki uku da dararensu ga matafiyi (wato awoyi 72). Kuma lokacin zai fara ne daga farkon shafa a huffin, bayan hadasi.

### Yadda ake yin shafa a huffi

Ya tafiyar da hannunsa daga karshen yatsun kafa zuwa idon sawu; ta saman kafar kawai, kuma shafar zata kasance da hannaye biyu ne akan kafofi biyu, a lokaci guda, sai hannun dama ya shafi kafar dama, hannun hagu kuma kafar hagu, kamar yadda ake shafan kunnuwa, wannan shine zahirin sunnah.

### Mas'aloli da suke da alaka da shafar huffi

**1-** Idan lokacin shafan ya kare, ko aka cire huffin da aka shafa, to wannan alwalar tana nan; bata lalace ba.

**2-** Halal ne yin shafa a jikin wanda ya yage, da wanda ake ganin fata saboda haskensa, ko rashin kaurinsa.

## Ladubban biyan bukata

**MUSTAHABBI NE:**

- Idan zai shiga bandaki, ya shiga da kafar hagu, kuma ya ce: "***BismilLah, Allahumma inniy a'uzu bika minal khubsi wal khaba'is (Allah, ina neman tsarinka daga shedanu maza da mata".***

- Idan zai fita kuma, sai ya gabatar da kafar hagu ya ce: ***"Gufranak; Ina neman gafararka".***

**WAJIBI NE AKANSA:** Ya buya a bayan katanga ko waninsa. Idan kuma a fili ne, to ya tafi nesa (da Mutane).

**BAYA HALATTA A GARE SHI (HARAMUN NE):**

- Ya biya bukatarsa a kan hanya, ko wurin zaman Mutane, ko karkashin bishiyoyi masu 'ya'ya, ko a wurin da zai cutar da Mutane, ko a cikin ruwan da baya gudana.

- Ya fiskanci alkibla ko ya juya mata baya, a lokacin biyan bukata.

- Ya taba al'aurarsa da hannun dama.

- Ya ambaci sunan Allah Ta'alah (zikiri).

Idan ya gama biyan bukatarsa, to sai ya yi tsarkin ruwa, ko na duwatsu.

**Kuma sharuddan tsarki da duwatsu sune:**

- Sharewar ya zama sau uku ko fiye, kuma ba zai sake shafa da wurin da ya yi shafar farko da shi ba.

- Wurin ya kasance ya yi tsafta, kuma za a gane haka ne, idan dutsen ko fefar share kashi ya dawo a bushe (babu jika).

- Kar abin yin tsarkin ya zama mai najasa, kuma kada ya yi tsarki da abinda ake girmamawa, kamar abinci, ko kashi, ko kashin dabbobi.

- Ya halatta a yi fitsari a tsaye idan Mutum ya amintu daga dawowan tartsatsin sa ga jikinsa da tufansa, kuma ya tabbatar al'aurarsa ba zata bayyana ba. Saboda *Annabi ﷺ ya zo jujin wasu Mutane sai ya yi fitsari a tsaye* (Bukhari da Muslim)

## TAMBAYOYI AKAN TSARKI

1. *Sharuddan alwala n*awa ne adadinsu? O 9 O 10 O 8

2. *Farillan alwala* sune: O Gabbai hudu O Gabbai hudu, da karin: jerantawa da gaggautawa.

3. *Abubuwan da suke warware alwala*, guda nawa ne? O **6** O **5** O 8

4. Bayyana abinda yake warware alwala daga cikin abubuwan da suke tafe:
   O Naman rakumi O Naman barewa. O Bayyanar Sauti daga ciki. O Tusa
   O Gyangyadi O Yin wanka wa Matacce. O Shafar Mace.

5. Ambaci sifar *Taimama*:

   ..........................................................................

   ..........................................................................

   ..........................................................................

6. Ambaci, sifar wankan Musulunci:

   ..........................................................................

   ..........................................................................

   ..........................................................................

**7. Ambaci hukuncin kowace mas'ala daga cikin mas'alolin da suke tafe:**

| Mas'alah | Hukuncinta |
|---|---|
| Yin niyya da lafazi | |
| Ya yi niyyar ya yi sallah da alwalarsa, sai ya yi fiye da sallah daya. | |
| Yin alwala domin karatun Alkur'ani, sannan ya yi salla da ita | |
| Ya yanke niyya, alhalin yana tsakiyar alwala. | |
| Ya yanke niyyar alwalar, bayan gama ta. | |
| Ya yi alwala alhalin akwai kwababben gari a kwabrinsa | |
| Ya yi alwala alhalin yana cikin cin naman rakumi. | |
| Ya yi alwala da ruwan sata. | |
| Ya gama alwala, sannan ya yi tsarki da ruwa ko dutse. | |
| Daukar sabon ruwa domin shafar kunnuwa. | |
| Ya shafi kansa sau uku | |
| Wanke gabban alwala sau daddaya. | |
| Yin alwala, sau uku-uku. | |
| Wanke tafin hannu, a cikin alwala. | |
| Tsattsefe gemu. | |
| Cuccudawa, a cikin alwala. | |

| | |
|---|---|
| Shafan abinda wajibi ne a wanke. | |
| Wanke kai (a alwala). | |
| Shigar da tafin hannu biyu cikin butar alwala. | |
| Fara wanke gabban dama. | |
| Kari akan wanki uku. | |
| Wanke kwabrin kafa. | |
| Ya yi sallah bayan, wanka a kogi<br>(ba tare da ya yi alwala ba) | |
| Ya yi sallah bayan, wankan Musulunci;<br>bai sake alwala ba. | |

## NA BIYU: ZAKKAH

**Zakkah nau'i biyu ce:**

***Zakkar Dukiya***

Itace rukuni na uku daga cikin rukunnan Musulunci. Kuma wajiba ce, ga kowane Musulmi, 'da, wanda ya mallaki nisabi.

Kuma babu *Zakkah* a cikin dukiya, face shekara ya gewayo mata. Saidai ga abinda ya fita daga kasa. *Duk kuma abinda ya zama yana bin wani asali ne, kamar abinda ya karu akan nisabi, ko ribar kasuwanci, to lamarin kewayowar shekararsa, shine kewayowar na asalinsa*.

Kuma tana kasuwa kashi hudu:

***Zakkar jiki (wato, zakatul* Fidr)**

Tana wajaba ga kowane Musulmi, babba ko karami, namiji ko mace, Bawa ko 'Da.

**Fadakarwar Mai tarjama:**

Manya sune za su fitar da zakkar ga 'ya'yansu kanana.

**Zakkar zinare da azurfa**

Da abinda yake tsayuwa a matsayinsu na takardun kudade da wasunsu. Nisabin zinare shine miskali 20 (wato giram 85). Nisabin azurfa kuma shine Dirhami 200 (wato, giram 595).

**Zakkar dabbobin ni'ima**

(Sa'ima) wanda suke kiyo na halal na tsawon kwanakin shekara, ko mafi yawansa. Kuma *Bahimatul An'am* (dabbobin gida) ana nufin: rakumi, shanu, Awaki da tumaki

**Zakkar abinda ya fito daga kasa**

Sune kwaya da 'ya'yan itatuwa.

**Zakkar kayan kasuwa**

Duk abinda aka tanade shi, domin saye da sayarwa.

## Wanda ake basu zakkah (wanda suka cancance ta):

**1. Fakirai:** Sune mabukatan da basu da komai, ko suna da sashen bukatarsu.

**2. Miskinai:** Sune suke da mafi yawan abinda suke bukata, ko rabin abinda suke bukata. Da za mu kaddara bukatar shekara da cewa, itace: 12,000, To fakiri zai zama yana da kasa da dubu shida, ko kuma bashi da komai. Miskini kuma, wanda yake da dubu shida, ko fiye da haka, amma bai kai 12,000 ba; saboda fakiri da miskini za mu basu abinda zai ishe su ne na tsawon shekara daya, saboda zakkah ana bada ita a kowace shekara.

<u>**3. Masu aiki akan zakkah:**</u> Ya kunshi masu karbo ta, da masu tsare ta, da wadanda aka wakilta musu raba ta, wadanda shugaba ya nada su. Ba a shardanta musu kasantuwa fakirai ba, a'a za a bada zakkar ga masu aikinta koda mawadata ne.

**4. Wadanda ake rarrashin zukatansu domin:** wadanda ake fatan su shiga Musulunci, ko tunkude sharrinsu, ko su kara karfin imani.

**5. Bayi:** Sune:

**a.** Bawa Musulmi wanda aka masa rubutun fansar kai, wanda zai sayi kansa daga shugabansa.

**b.** 'Yanta Bawa Musulmi.

**c.** Bawa Musulmi da yake fursuna.

Baya shiga cikinsu, Bawan da shugabansa ya 'yanta shi, sai ya kirga hakan daga zakkarsa, saboda hakan bai halatta ba.

**6. Wadanda ake bi bashi:** Sune;

**a.** Wanda ya ci bashi domin yin sulhu a tsakanin Mutane.

**b.** Wanda ya ci bashi don radin kansa.

Bai halatta ka warware bashin talakan da ka ke bi, da niyyar *Zakkah* ba.

7. **Mayaka fi sabilil Lahi:** Ya kunshi Mayakan, da abinda suke bukata na makamai da waninsa.

8. **Matafiyin da guzuri ya yanke masa:** sai a bashi abinda zai mayar da shi garinsa ko kasarsa. Ya halatta a baiwa kaso daya daga cikin kashi takwas. Kuma bayar da *zakkah* ga mawadaci baya halatta, ko ga mai karfi wanda yake neman kudi. Haka kuma ba a bayar da ita ga iyalan annabi Muhammadu ﷺ; wanda sune kabilar Banu Hashim da bayinsu. Haka bata halatta ka bayar da ita ga wanda wajibi ne ka ciyar da shi a lokacin bayar da ita, haka kafiri; wanda ba Musulmi ba. Amma sadaka ta nafila, ya halatta ka bayar da ita ga wadannan da wasunsu; saidai duk lokacin da ta kasance tafi amfani gamamme ko kebantacce, to tafi kamala da lada.

## Ma'anoni masu muhimmanci

-*Bint Makhad* ('Yar mai nakuda, wanda uwarta tayi kusan Haifa mata kanwa) daga cikin rakumi itace, wanda ta cika shekara daya (1). An sanya mata wannan sunan, saboda uwarta tana da ciki.

- *Bint Labun* ('Yar mai nono) daga cikin rakumi, itace ta cika shekaru biyu (2). An sanya mata wannan sunan saboda uwarta tana shayarwa.

-*Al Hikkah* daga cikin rakumi, itace ta cika shekaru uku (3). An sanya mata wannan sunan saboda rakumi ya fara mata barbara. -*Al Jaz'ah* daga rakumi, itace wanda ta cika shekaru hudu (4). An sanya mata wannan sunan, saboda a wannan shekarun ta fara zubar da hakora.

-*At-Tabi'u ko At-Tabi'ah* daga cikin shanu shine wanda ya cika ko ta cika shekara daya.

-*Almusinnah*: Daga cikin shanu, itace wanda ta cika shekaru biyu (2).

## Gwargwadon zakkah

| Nau'ukan dukiyar Zakkah | Nisabi gabanin wajabcin zakkah | Gewayowar Shekara | Gwargwadon abinda za a bayar na zakkah |
|---|---|---|---|
| Zakkar dabbobin ni'ima (Rakuma, Shanu, Tumaki, Awaki) wadanda suke kiyo bada wahala ba. | Duba jadawalin dake | ana shardanta masa gewayowar shekara. | Duba jadawalin dake tafe |
| Zakkar abinda yake fitowa daga kasa | Sa'iy 300 | Ba a shardanta masa gewayon shekara ba | Ga abinda ruwan sama ya shayar, ko idaniya ko idan ya kasance yana shan ruwa da jijiyarsa za a bada 1/10 |
| | | | Wanda kuma aka shayar da shi da wahala za bada 1/20 |
| | | | Ga abinda aka shayar da shi da duka biyu (rabi da ruwan sama, rabi da wahala) za a bada 3/40. |
| Zakkar kudade | Giram 85 na zinare. Ko giram 595 na azurfa | Ana shardanta masa gewayowar shekara. | Zakkarsa shine 1/40 |
| Zakkar kayan kasuwanci | Za a kimanta shi da abinda talakawa za su fi morewa tsakanin zinare da azurfa | Ana shardanta masa gewayowar shekara. | Zakkarsa shine 1/40 |

## Nisabin dake wajabta zakka a cikin dabbobin gida, da bayanin gwargwadon abinda za a cire

### Nisabin dake wajabta zakka a cikin dabbobin gida, da bayanin gwargwadon abinda za a fitar

**Shanu da bauna**

| Gwargwado | | Zakkarsa |
|---|---|---|
| Daga | Zuwa | |
| 30 | 39 | Tabi'i 1 ko Tabi'ah mace |
| 40 | 59 | Musinnah daya |
| 60 | 69 | Tabi'ah 2 |
| Daga adadin nan, duk shanu 30, Tabi'a 1, Duk shanu 40, Musinnah guda 1 | | |

**Rakumi mai tozo 1 ko 2**

| Gwargwado | | Zakkarsa |
|---|---|---|
| Daga | Zuwa | |
| 5 | 9 | Tinkiya 1 |
| 10 | 14 | Tumaki 2 |
| 15 | 19 | Tumaki 3 |
| 20 | 24 | Tumaki 4 |
| 25 | 35 | Bint Makhad 1 |
| 36 | 45 | Bint Labun 1 |
| 46 | 60 | Hikkah |
| 61 | 75 | Jaz'ah |
| 76 | 90 | Bint Labun 2 |
| 91 | 120 | Hikkah 2 |
| 121 | 129 | Bint Labun 3 |
| Daga adadin nan, duk rakuma 40, Bint Labun 1. Duk rakuma 50, Hikkah 1 (Waks) kuma shine daga 9 iyi kasa, wanda yake tsakanin abinda ya wajaba 2) | | |

**Tumaki da awaki**

| Gwargwado | | Zakkarsa |
|---|---|---|
| Daga | Zuwa | |
| 40 | 120 | Tinkiya 1 |
| 121 | 200 | Tumaki 2 |
| 201 | 300 | Tumaki 3 |
| Daga adadin nan, duk tumaki 100, sai a cire tinkiya 1. | | |
| Ba'akarbar zakkar bunsuru, tsoho gajiyayye, mai wani aibi, haka mai sharri. Haka ba a karbar: ramammiya, mai nakuda, mai ci dayawa, da zababben dukiya. | | |

## TAMBAYOYI AKAN ZAKKAH

1. Babu zakkah a cikin dukiya har sai *shekara ta zagayo mata*, shekarar kuma ta ....... O Ta Islama (*Hijira*) O Miladiyyar Annabi Isah. O Babu banbanci.

2. An togance, daga sharadin *kewayowar shekara* a zakkar ..........
O *Rikaz*; Dukiyar da aka bunne a jahiliyya. O Abinda ya fito daga kasa
O Duka biyun.

3. Nisabin *zakkar* zinare shine ............
O Giram 85. O Giram 595 O Giram 95.

4. Nisabin *zakkar* azurfa shine .......
O Azurfa giram 200 O Giram 595. O Duka biyun.

5. *Bahiymatul An'am* sun hada da: Rakuma, Shanu, Bauna, Tumaki da awaki ( Gaskiya ne – A'a ).

6. Babu zakkah a cikin kayan marmari ( Haka ne – A'a ).

7. *Sa'imah* a cikin dabbobi Itace ....... O dabba mai tsada. O Dabbar da take kiyo na tsawon shekara, ko mafi yawansa.

8. Dabbar da ke kiyo da ciyawar da babu mai ita (–MUBAH- ciyawar da ta tsiro) itace ...... O Mai cin dadadan abubuwa. O Wanda batta da Mamallaki.

9. Idan aka ambaci kalmar *Miskinai* ita kadai, To *Fakira*i sun shiga ( Haka – A'a).

10. Fakiri za a bashi zakkar da za ta ishe shi tsawon... O Shekara 1 O Wata 1.

11. Masu aiki akan zakkah sune...
O Duk mai aiki a al'amarin *Zakka*h. O Kawai wadanda shugaba ya nada su.

**12.** Lissafa *zakkar* abinda yake tafe:

| Nau'in dukiya | Gwargwadon abinda ya wajaba a cire na *Zakkah* | *AlWaks* idan akwai |
|---|---|---|
| Dirhami 100 (na azurfa) | | |
| Dinari 300 (Zinari) | | |
| Dirhami 400 (na azurfa) | | |
| Giram 80, na zinari. | | |
| Giram 500, na azurfa | | |
| Tumaki 30. | | |
| Tumaki 60. | | |
| Tumaki 565. | | |
| Rakuma 4. | | |
| Rakuma 17. | | |
| Rakuma 449 | | |
| Shanu 30 | | |
| Shanu 49 | | |
| Shanu 77. | | |
| Shanu 99. | | |
| Riyal miliyan 20 | | |
| Riyal 40. | | |
| Riyal 45679. | | |
| Sa'iy 255 na alkama. | | |

**13.** Kafiri; wanda ba Musulmi ba, yana shiga cikin "*Mu'allafatu kulubuhum*" koda ba a yi fatan shigansa Musulunci ba, ( Haka – A'a ).

**14.** Idan wanda ya mallaki Bawa ya 'yanta shi, shin za a baiwa 'yantacce Bawan *zakkah* ( E – A'a ).

**15.** Mawadacin da yake bin fakiri bashi, sai ya bar wannan kudin, da niyyar *zakkah*. Hakan daidai ne ( E – A'a).

**16.** "Fiy sabilil Lahi" ya kunshi dukkan kofofin alheri, kamar gina *Masallaci* ( E –A'a ).

**17.** *Zakka*r zinare da azurfa (da kudaden zamani) ana fitar da daya ne bisa 40 ( E – A'a ).

**18.** *Zakkar* dabbobin gida tana wajaba ne a cikin masu kiyo da kansu (Sa'imah), bata wajaba cikin dabbobi masu aiki, da wanda ake ciyar da su ( E – A'a ).

**19.** *Zakkah* tana wajaba a cikin kwaya da 'ya'yan itace idan ya kai nisabi, a lokacin da kwaya da 'ya'yan itacen suka fara nuna ( E – A'a ).

**20.** Wajibin da za a cire a zakkar kwaya da 'ya'yan itace shine 1/20, ga abinda aka shayar da shi *da wahala* ( E – A'a ).

**21.** Wajibi ne a fitar da *zakkar* zinare idan ya kai nisabi, kuma gwargwadonsa shine: *miskalil* 20 ( E – A'a ).

**22.** Ka yi da'ira ga abinda *zakka*h take wajaba a cikinsa:

O Kaji O shagon kasuwanci O Tumakin da aka daure ake ciyar da su.
O Rakuman da suke sake. O Gonar dabino. O *miskali* 25 na zinare.

**23.** *Tabi'i'* a cikin shanu, shine yake da shekaru 2, ( E – A'a ).

**24**. Ana kimanta *nisabin zakkar* takardun kudi, da .........

O Kayan kasuwa . O Kimar nisabin zinare, ko azurfa.

O Kimar nisabin zinare da azurfa.

**25**. Wajibi a zakkar takardun kudi shine: O $^{1}/_{40}$ O $^{1}/_{20}$.

**26**. *Zakkar* giram 80 na zinare shine .......

O giram 2 O Giram 4 O Babu zakkah a cikinsa.

**27**. Wajibi ne a bada *zakkar* gidan da aka tanade shi domin zama ( E – A'a ).

**28**. Duk *Mai bulaguro* za a bashi *zakkah* tun da shi *Ibn Sabil ne.* ( Haka ne – A'a ).

## NA UKU: AZUMI

**A larabce,** Azumi na nufin kamewa. **A shari'a kuma**: Bauta wa Allah ta hanyar kamewa ga barin ci, da sha, da sauran abinda suke karya shi, daga fudowar alfijir na gaskiya. zuwa faduwar rana.

### Rukunnan azumi

**1 - Niyyah**

**2-Kamewa daga abubuwan da zasu karya azumi.**

**Niyyar azumin farilla**

Ba makawa dole, a kwana da niyya a azumin farilla, tun daga dare, ma'ana gabanin fudowar alfijir. Kuma yin niyya lokacin kamawan watan azumi yana isarwa. Kuma mahallin da ake kulla niyya shine zuciya, furta ta da harse kuma bidi'a ne.

**Niyyar azumin nafila**

Ya inganta ayi niyyar a cikin kowane lokaci na yini matukar Mutum bai yi abinda yake warware azumin ba. Sai dai ana fara samun ladan azumin ne daga lokacin da aka kulla niyya.

### Nau'ukan azumi

**Na wajibi:**

A ramadana, kaffarori, da bakance

**Nafila:**

Sauran azumi, ba wancan ba.

## Sharuddan wajabcin azumi

**1-** Musulunci. **2-** Hankali. **3-** Balaga: Wanda bai balaga ba, Waliyyinsa zai rika kwadaitar da shi kan azumi kuma ya umurce shi. **4-** Rashin bulaguro: Azumi baya wajaba akan matafiyi. Saidai abinda yafi shine ya yi azumin matukar ba zai wahalar da shi ba, saboda Annabi ﷺ ya aikata hakan, kuma saboda hakan yafi saurin sauke abinda ya rataya a wuyan Bawa, kuma yafi sauki ga Mutum, kuma domin riskar falalar da take cikin azumi a watan azumi. **5-** Lafiya.

### Nau'ukan rashin lafiya dangane da azumi

**Cutar da ba a zaton warkewarta:**
Ana riskarwa gare shi, babban da ya gaza yin azumi. Azumi ba zai lazimce shi ba, saidai ya ciyar da miskini a madadin kowane yini; ko ta hanyar ya hada miskinai gwargwadon yawan kwanakin; sai ya basu abincin dare, ko rana. ko kuma ya raba abincin ga miskinai daidai da yawan kwanakin; kowane miskini ya bashi 1/4 sa'in Annabi, wato abinda zai kai nauyin rabin kilo, da giram goma; na kyakkyawuyar alkama.
Kuma yana da kyau ya hada masa da da nama, ko mai.

**Cutar da ake fatan gushewarta, kuma azumi zai wahalar da shi:**

Ana hada su cikin hukunci, Mai haila, da jinin haihuwa, da mai shayarwa, da matafiyi. Sai kowa ya biya gwargwadon yawan kwanakin da ya karya azumi a cikinsu; wato kamar idan maras lafiya ya warke; idan kuma ya rasu gabanin ya warke, to azumin ya sauka akansa.

**Da me, shigan watan Ramadhana yake tabbatuwa?**

Ko ta hanyar ganin jinjirin watan Ramadhana,
ko cike kirgen watan Sha'abana kwanaki 30.

**Abubuwan da suke lalata azumi**

1- **Ci ko sha da ganganci:** Amma idan wani ya manta to azuminsa ya inganta.

2. **Saduwa:** Idan ya auku a cikin yinin *Ramadan* alhalin azumin wajibi ne akan wannan Mutumin, to kaffara mai tsanani ya wajaba akansa; itace: 'yanta Baiwa, idan bai samu ba, azumin watanni biyu a jere, idan ba zai iya ba, sai ya ciyar da miskini 60.

**3-** Fitar maniyyi ta hanyar taba mace, ko sumbatanta, ko runguma, ko makamancinsu.

**4-** Abinda yake daukar ma'anar ci da sha, kamar allurar da aka sanya mata abinci, idan ba a sanya mata abinci ba, bata karyawa.

**5-** Fitar da jini ta hanyar kaho; Amma fitar da jini kadan saboda gwaji ko makamancinsa, shi kam baya karya azumi.

6- **Yin amai** da ganganci.

7- **Fitar jinin haila da nifasi** (haihuwa)

**Abubuwan da aka halatta ga Mai azumi**

Hadiye yawu, dandanar abinci idan akwai bukatar hakan, yin wanka, siwaki, shafa turare, da wankan jin sanyi.

## Mustahabban Azumi

**1-** Cin *Suhur.* **2.** Jinkirta sahur **3.** Gaggauta buda baki

**4.** Buda baki da dabino da bai bushe ba, idan bai samu ba, sai busasshe; kuma an so su kasance guda uku. In ai samu ba, sai ya kwankwadi ruwa. Idan bai samu komai ba, sai ya yi niyyar karya azumi a ransa.

**5.** Addu'a a yayin buda baki, da kuma a tsawon lokacin azumi.

**6.** Yawaita sadaka. **7.** Kokari wajen sallolin dare. **8.** Karatun Alkur'ani.

**9.** Fadin: "Ni mai azumi ne" ga wanda ya zage shi. **10.** Yin Umrah.

**11.** I'tikaafi a goman karshe. **12.** Neman daren lailatul kadr.

## Makaruhan Azumi

1. Kaiwa makura wajen kurkuran baki, da shaka ruwa a hanci.
2. Dandanar abinci ba tare da bukatar hakan ba.

## Ya Haramta ga Mai azumi:

1. Hadiye kaki,amma azumin bai karye ba idan ya hadiye.
2. Sumbatar mace, ga wanda bai aminta kan lalacewar azuminsa ba.
3. Zancen karya (da dukkan aiki na haram).
4. Aikin jahilci (wauta da rashin hakuri)
5. Wisaal (wato, wucel a azumi; ta yadda ba zai karya ba; na tsawon yini biyu a jere).

## Azumin Nafila

**1-** Azumi 6 a watan *Shawwal* ga wanda ya cika azumin *Ramadan,*
Abinda yafi shine a yi su kai tsaye, daga yini na biyu.

**2-** *Azumin yinin Arafah* ga Mutumin da ba Mahajjaci ba.

**3-** *Azumin* Yinin *Ashutra* (ranar goma/Muharram) tare da yini biyu, na ranar tara, da sha daya. 4- Azumin litinin da alhamis, musamman litinin din

**5-** Azumin yini uku a kowace wata, Abinda yafi kuma shine yinnin darare masu haske, wato 13, 14, da 15.

**6-** Azumtar yini, da shan ruwa a yinin dake bayansa. **7-** Yin azumi a cikin watan Allah; Muharram. **8-** Azumi a kwanaki taran farko na Zul*Hijjah.* Azumtar mafi yawan kwanakin watan *Sha'ban;* sai dai kada ya kammala shi.

## Azumi na Makruhi

Makaruhi ne a ware yinin jumu'a, ko asabat, ko lahadi da azumi. Amma idan Mutum ya ware yinin da azumi domin wani sababi, kamar yinin *Arafah,* to wannan babu komai.

## Azumi na Haram

**1-** Ware watan *Rajab* da azumi.

**2.** Azumtar ranakun idi biyu.

**3-** Azumtar yinin shakku (yinin kafin *Ramadan);* sai dai ga wanda yake da wuridin azumi na sati, to sai ya yi.

**4-** Azumtar kwanakin *tashrik* (11, 12, 13/Zulhijjah), Sai dai ga Mutumin da bai samu hadayar yankawa ba.

**5-** Azumin kullum (azumtar shekaara).

## Hukunce-hukuncen ramukon azumi

- Mustahabbi ne, jeranta azumin ramuko.
- Ya dace, ya yi gaggawar ramukon, daga bayan yinin *Idi.*
- Baya halatta, ya jinkirta ramukon har zuwa bayan wani *Ramadan* na gaba.
- In kuma ya jinkirtan, to wajibinsa dai shine ramukon kawai, Sai dai ya yi zunubi.

## *Zakatul Fitr*

Tana wajaba ga wanda ranar yinin karshen Ramadhana ta fadi masa, alhalin yana: *Musulmi,* babba ne ko karami, namiji ko mace, Bawa ko ‘da (mai ‘yanci). Sai kuma yake da rarar sa’iy daya akan abincinsa na ranar idi da darensa da sauran bukatunsa na asali; shi da iyalansa. Mustahabbi ne a fitar da ita, ga wanda yake cikin mahaifiyarsa.

**Kuma hikimomin shar’anta ta su ne:**

**-** Lallai ita tsarki ce ga mai azumi daga wargi da kwarkwasa.

– Lallai a cikinta akwai wadatar da fakirai da miskinai, ba sai sun yi roko a ranar idi ba

### Lokacin fitar da zakatul fidr:

| Lokacin halacci | Lokaci na mustahabbanci | Lokacin haramci |
|---|---|---|
| Shine yini daya ko biyu gabanin idi | Bayan sallar asuba gabanin sallar idi | Bayan sallar idi |

## Gwargwadon zakatul fidr

Sa'iy daya ne na abincin da Mutane suka rike shi a matsayin abinci. Kuma bayar da kudi baya wadatarwa. **Gwargwadon sa'iy kuma shine:** kilogiram biyu da giram 40 na kyakkyawar alkama.

## Sallar Idi

Farillar ainihi ce akan kowa. kuma ana yin sallar idi bayan rana ta dago gwargwadon kan mashi, har zuwa lokacin zawali. Ba a yin ramukonta idan ta kubuce. Kuma sunnah a lamarinta shine, a aikata ta a sahara (wajen gari), ba a kewayen gari ba. Kuma ya halatta a yi ta a cikin Masallaci. Kuma sunnah ne mutum ya ci dabino wuturi gabanin yin sallar *'IdulFidr'*. Kuma sunnah ne Mutum ya yi tsafta ya sanya turare, ya sanya mafi kyan tufafi. Haka ya tafi ta wata hanayar, ya komo ta wata hanyar. Kuma babu laifi ayi gaisuwar murnar idi da fadinka: "Allah ya karba mana, kuma ya karba muku". Kuma an sunnata yin kabbarori a koyaushe; na daren idi, da kuma bayan salloli, har zuwa lokacin faduwar ranar yinin idi. Kuma sifar kabbarar ita ce: *"Allahu Akbar. Allahu Akbar. La ilaha ilLahu, walLahu Akbar, Allahu Akbar, wa lilLahil hamd".* **Sifar sallar idi:** Raka'o'i biyu ce, gabanin huduba. Bayan ya yi kabbarar harama (wato, fadin: *Allahu Akbar),* zai yi kabbarori guda 6 a raka'ar farko. A ta biyu kuma zai yi kabbarori 5, banda kabbarar tasowa.

## TAMBAYOYI AKAN AZUMI

**1.** Rukunnan azumi nawa ne adadinsu? O 2 O 3 O 4

**2.** Azumi, ga wa yake wajaba?

**a**. ...............................................................................

**b**. ...............................................................................

**c**. ...............................................................................

**d**. ...............................................................................

**3.** Kowace cuta, tana hana yin azumi ( E – A'a ).

**4.** Ka ambaci hukuncin ayyukan da suke tafe:

| Mas'alah | Hukuncinta |
|---|---|
| Ya yi niyyar azuminsa bayan sallar asuba. | |
| Azumin da babu niyyah. | |
| Azumin karamin yaro. | |
| Azumin Mai bulaguro (matafiyi). | |
| Azumin mai nifasi (jinin haihuwa). | |
| Azumin gajiyayyen da ba zai iya ba. | |
| Ya ci, alhalin yana azumi. | |
| Allura mai abinci, ga mai azumi. | |

| | |
|---|---|
| Sanya madigin ido ga mai azumi. | |
| Yin allurar anasiziya (don tafiyar da zogi) ga mai azubi | |
| Yin kaho ga mai azumi. | |
| Yin amai ga mai azumi. | |
| Hadiye yawu ga mai azumi. | |
| Dandanar abinci ga mai azumi. | |
| Yin wanka ga mai azumi. | |
| Wankan jin sanyi. | |
| Yin aswaki | |
| Shakar turaren hayaki ga mai azumi | |
| Lokacin yin suhur. | |
| Da me zai yi suhur? | |
| Da me zai yi buda baki? | ...................Idan bai samu ba, sai ya yi da............................ Idan bai samu ba sai ya yi da ...........Idan bai samu ba, sai ya ........................................ |
| Sallar Tarawih. | |
| Umrah a watan Ramadan | |

| | |
|---|---|
| Kaiwa makura wajen kurkurar baki ga mai azumi | |
| Kis (sumba) ga Mai azumi. | |
| Wucel (wisal); wato rashin karya azumi na tsawon yini biyu a jere. | |
| Azumin kwanaki 6 a watan Shawwal | |
| Azumin yinin Arafah | |
| Azumin ranar shakku (kafin Ramadhana) | |
| Azumin ranar Idi. | |
| Yin azumin kwanakin idi uku (tashrik, 11, 12, 13) | |
| Yin azumin watan Muharram | |
| Azumtar watan Rajab | |
| Yin azumin kullum (shekara). | |
| Azumin ranar juma'a. | |
| Ya jinkirta ramukon dake kansa har watan Ramadan | |

## NA HUDU: AIKIN HAJJI

Hajji shine rukuni na biyar daga cikin rukunnan Muslunci. Kuma yin sa wajibi ne ga, Musulmi, Mai hankali, Balagagge,, 'Da, Mai iko. Mace kuma ana kara sharadin samun Muharrami, idan a hajjinta tana bukatar sai ta yi bulaguro. Kuma rukunnansa guda hudu ne:

**Harama/Niyyah**
Wato niyyar shiga ayyukan hajji; a zuciya. Kuma ba shine fadin: Labbaikal *Lahumma labbaik....,* kuma ba shine sanya mayafai ba.

**Tsayuwa a filin Arafah**
Daga azahar din ranar tara ga Zulhijjah, har zuwa asubar ranar idi. Annabi ﷺ ya ce: "Hajji shine tsayuwar Arafah"

***Tawaaful ifadha***
(Dawafin ziyara). Bayan an yi tsayuwan Arafah. Kuma ba shine dawaful kudum ba.

***Sa'ayi***
Tsakanin dutsen Safah da Marwah. Allah ya ce: **"Lallai Safah da Marwah suna daga alamomin addinin Allah"** (2:158)

**Nau'ukan Hajji**

***Ifradi***
Shine ya yi niyyar aikin hajji kadai, ya kuma zo da ayyukansa su kadai.

***Kirani***
Ya yi niyyar hajji da umrah a tare, cikin ayyuka daya, amma akwai hadaya akansa.

***Tamatu'i***
Shine ya yi harama da umrah a cikin watannin hajji, sai ya gama ta ya warware, sannan ya yi harama da hajji a wannan shekarar, kuma akwai hadaya akansa.

## WAJIBAN HAJJI

Wanda ya bar wani daga cikin wadannan wajiban, yana wajaba akansa ya cike gibin hakan da zubar da jini; wanda kuma akuya ce da za a yanka a harami, a raba namanta ga fakiran Makkah, kuma bai halatta ya ci daga wannan naman ba.

| | |
|---|---|
| Yin harama daga mikati. | Tsayuwa a Arafah, har zuwa faduwar rana, ga wanda ya yi tsayuwarsa cikin yini. |
| Kwana a Muzdalifah. | Kwana a Minah a dararen kwanakin Tashrik. |
| Aski ko saisaye. | Jifan duwatsu (Shedan). |

Dawafin bankwana ga wanda ba Mai haila ko jinin biki ba, idan ya so fita daga garin Makkah, koda bayan ficewar watannin hajji ne.

**Mikatan daukar hajji da umrah**

**Mikati na lokaci**

Sune watannin hajji: Shawwal, Zulka'adah, da Zulhijjah. Wadannan watanni ne da suka kebanci hajji. Amma umrah kam bata da wani zamani ayyananne.

**Mikati na wuri**

-Zulhulaifa ga Mutanen Madina da wanda ya bi ta Madinah. - Al Juhfah ga Mutanen Sham, Misra, da Magrib. - Karnul Manazil ga Mutanen Najd. - Yulamlam ga Mutanen Yamen. -Zatu-irkin ga Mutanen Iraki,

## MUSTAHABBAN HAJJI

Yin wankan harama, da shafa turare.

Sanya mayafai biyu farare ga Maza.

Yanke farce da aske gashin da ya wajaba a aske shi gabanin harama.

Yin talbiyyah daga lokacin harama, har zuwa lokacin jifan jamratul akabah.

Dawafin kudum ga Mai hajjin ifradi da kirani.

Sassarfa a cikin kewaye uku na farkon dawaful kudum da dawafin umrah ga mai tamattu'i.
Sassarfa (ramlu) shine yin sauri a cikin tafiya.

Iddiba'i a cikin dawaful kudum da dawafin umrah ga mai tamattu'i, wanda shine fitar da kafadar dama.

Jam'ut takdim na sallolin magriba da isha a Muzdalifa, daga isowarsa wurin.

Kwana a Minah, a daren Arafah.

Sumbantar hajarul Aswad.

Tsayuwa a Muzdalifah, wajen Mash'arul haraam, daga asuba har zuwa lokacin shuruki, idan hakan ya saukaka.
Tare da cewa Muzdalifa dukkanta wurin kwana ne.

## Abubuwan da harama take hanawa (Mahazuratul ihrami)

Guda tara ne: Aske gashi daga kai da jiki, yanke farce, lullube kai da abinda yake taba kai ga Namiji, Sanya dinkakken tufafi ga Namiji, wanda shine abinda aka dinka ga jiki ko ga wata gaba daga cikin gabbai, sanya nikabi da safar hannu ga Mace, Shafa turare (haka sabulu mai kamshi). Kashe abin farautar tudu da neman kama shi, daura wa kansa ko ga waninsa aure, Jima'i, Shafa Mace (wanda bai kai ga saduwa ba). Wanda ya aikata wadannan cikin mantuwa ko da jahilci ko aka tilasta shi, babu komai akansa. Saidai yin farauta wannan kam akwai fidiya akansa a kowane hali. **Idan da ganganci ne kuma sun kasu kashi hudu:**

### Wanda bashi da fidiya

Shine: **daura aure,** ga kansa ko ga waninsa. Haka kuma, **shafa mace** ba tare da isa ga farjinta ba, matukar maniyyi bai fito ba; Shima babu kaffara akansa, kuma wajibi ne ya tuba.

### Wanda fidiyarsa itace bayar da kwatankwacinsa

Shine: **Kashe abin farautar tudu, da farautarsa**. Wanda ya kashe shi akwai fidiya akansa, ta kowane hali. Shine: Rakumi, Shanu, da awaki. Mutane biyu adalai su za su yi hukunci da hakan.

### Wanda fidiyarsa take da tsanani

Shine **Jima'i**; Amma Mutumin da ya yi jima'i gabanin warwarewar *Ihraami* na farko, To lallai ya bata hajjinsa, kuma zai kammala a bacen, kuma dole ya sake hajjin a shekaru na gaba, kuma dole ya yi kaffara da rakumi.

### Wanda fidiyarsa itace fidiyar cire dauda;

Sune sauran ababen da aka hana Maniyyaci aikata su: Kuma fidiyarsu dayan abubuwa uku ne, cikin zabinsa; Ko ya yi azumin yini uku, ko ya ciyar da miskinai shida, kowane daya rabin sa'iy, ko yankar dabba, da rabiyar namanta ga fakiran Makkah.

**Sunayen kwanakin hajji**

| | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| **Yinin Tarwiyah** Shine yinin **8/12** Sun kasance suna diban ruwan amfaninsu a cikinsa zuwa Minah. | **Yinin Arafah. Ko yinin tsayuwa;** Shine **9/12** | **Yinin idi ko yinin layya shine yinin 10/12** | **Yinin Karri (tabbatuwa a Minah), Shine yinin 11/12** | **Yinin ficewa daga Minah na farko,** Shine **12/12** | **Yinin ficewa daga Minah na biyu,** Shine **13/13** |

Daren *jam'u* (Muzdalifah), shine daren idi, an kira shi da sunan nan, saboda taruwan Mutane da haduwarsu a cikinsa, bayan tsayuwarsu a *Arafah*. Kuma saboda Mutanen Makkah a hajjinsu a jahiliyya, basu fita zuwa *Arafah*.

**Wuraren addu'a biyar, a aikin hajji**

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| **A ranar Arafah** wato yinin 9, bayan rana ta yi zawali | **A Muzdalifah** bayan ketowar alfijir, har zuwa lokacin da gari zai yi haske ya washe. | **Bayan jifan jamrah karama, da ta tsakiya,** a kwanakin tsashrik uku. | **Lokacin yin** ***Dawafi*** | **Lokacin tsayuwa akan dutsen** ***Safah da Marwah*** **a halin sa'ayi,** Haka a lokacin tafiya a tsakaninsu. |

**_Sifar Umrah da hajji_**

*Sheikh Ibn Usaimin –Allah ya yi masa rahama- ya ce:*

Idan kuka iso mikati, sai ku yi wanka, ku sanya turare a jikinku, kamar kai, gemu, sannan ku yi harama da umrah, da nufin yin tamattu'i ku tafi zuwa garin Makkah kuna yin *LABBAIKAL LAHUMMA LABBAIK*…. Idan Kuka isa daki mai alfarma, ku yi dawafi sau bakwai, a matsayin dawafin umrah. Kuma ku sani, gaba dayan Masallacin wuri ne na dawafi; kusa ne da dakin Ka'aban ko nesa, saidai kusantar ka'aban shine yafi falala; matukar ba za ka cutu da cunkoso ba. Amma idan akwai cunkoso, to ka tafi nesa da dakin, al'amarin yana da fadi, Wa lilLahil hamd. Idan kuka kammala dawafi, to ku yi raka'oi biyu a bayan makamu Ibrahima –عليه السلام-, ko ta kusa da shi, idan an samu damar hakan, idan kuma ba a samu ba, to koda nesa ne da shi, kawai dai Makamu Ibrahima ya kasance a tsakaninku da tsakanin ka'abah. Sai ku fita zuwa ga sa'ayin umrah a tsakanin Safah da Marwah, ku fara da dutsen Safah, idan kuka kammala zagaye bakwai, sai ku rage gashin kanku ta dukkan kan, domin rage shi ta gefe daya baya wadatarwa, kuma kada ku rudu da aikin Mutane dayawa (da kuke gani).

Idan ranar *takwas ga watan zulhijjah* ta zo, sai ku yi wanka, ku sanya turare, ku yi harama da hajji, daga masaukanku. Ku fita zuwa ga Minah, ku yi sallar aza*har*, *La'asar*, *Magriba*, *Isha'*i, da asuba. Kuna masu kasaru, ba tare da kun hade salloli biyu ba; saboda Annabinku ﷺ ya kasance yana yin kasarun salloli a *Minah* da *Makkah*, amma baya hada su. Idan rana ta fudo a ranar *Arafah,* sai ku tafi, kuna yin *Talbiyyah* cikin kankan da-kai ga Allah, zuwa ga *filin Arafah.* Sai ku hade sallolin *Azahar* da La'asar a *Arafah* a lokacin azahar (jam'u takdim), kuma raka'o'i bibbiyu ga *kowacce.*

Sannan ku shagaltu da addu'a da marairaice wa Allah, kuma ku yi kwadayin kasancewa cikin tsarki (da alwala), ku fiskanci alkibla, koda dutsen Arafah ya kasance a bayanku; domin abinda aka shar'anta shine fiskantar alkiblah, kuma ku kula sosai da iyakokin **Arafah** da alamominta, sai ku kasance ta cikinsu, domin Mahajjata dayawa suna tsayawa suna ba a cikin filin Arafah ba, kuma duk wanda bai samu Arafah ba, to bashi da hajji, saboda fadin Annabinmu ﷺ "**Hajji shine Arafah**"**.** Kuma matukar ka tsaya a farfajiyar Arafah, ta gabas ne ko ta yamma, ko ta kudunta ko ta arewa, to hakan ya yi, in banda **Badanul Wadiy** (Wadiy Uranah); saboda fadin Annabi ﷺ **"Na tsaya a nan, kuma Arafah dukkanta wurin tsayuwa ne".**

**Idan rana ta fadi, kuka tabbatar ta fadin, sai ku tafi zuwa ga *Muzdalifah*** kuna masu *Talbiyah* da kankan da-kai ga Allah. Kuma ku lazimci natsuwa, gwargwadon iko, kamar yadda Annabinku ﷺ ya umurce ku da aikata hakan, saboda ya fito daga Arafah alhalin yana jan linzamin rakumarsa baya, har kanta yana kokarin taba jikin tudun sirdinsa, alhalin yana fada da hannunsa mai karamci: **"Ya ku Mutane! Abi a hankali, a tafi a natse".**

Idan kuka iso farfajiyar *Muzdalifah,* ku yi sallar *Magriba* da *Isha'i,* sai ku yi barci har *asubah.* Kuma Annabi ﷺ bai yi rangwame ga wani ya bar *Muzdalifah ba, sai ga Mutane masu rauni; su kam ya musu rangwamen su tafi a karshen dare. Idan kuka yi sallar asuba, sai ku fuskanci alkiblah, kuna masu kabbara da gode wa Allah, da addu'o'i, har haske ya bayyana sosai, sai ku tafi gabanin fudowar rana, zuwa Minah.* Sannan ku tsinci duwatsu guda bakwai, ku tafi zuwa ga *Babbar Jamrah* wanda itace ta karshe, ta bangaren *Makkah,* Sai ku jefe ta, bayan fudowar rana, da duwatsu guda bakwai, kuna masu yin kabbara *Allahu Akbar* tare da kowane dutse, kuna masu kankan da-kai a gare shi, kuna girmama shi. Kuma ku sani lallai makasudin jifan shine girmama Allah, da tsayar da ambatonsa. Kuma wajibi ne dutsen ya fada cikin kewayen, amma ba sharadi ba ne, ya bugi ginshikin.

Idan kuka gama jifan duwatsun, sai ku yanka hadaya, kuma bata isarwa ga al'amarin hadaya; sai dabbar da take isarwa ga layya, kuma babu laifi ka wakilta wani ya yanka maka. Sannan bayan kun yi yanka, sai ku aske gashinku, kuma wajibi ne ku aske dukkan gashin, kuma baya halatta ku aske sashensu ku bar sashe. Mace kuma zata rage gashinta ta kowace kusurwa daga kanta gwargwadon kan 'yar yantsa.

Bayan haka, kun yi abinda ake kiransa *tahallulul Awwal,* sai ku sanya tufafinku, ku yanke farcenku, ku sanya turarenku, amma ba za ku sadu da matanku ba. Sa'annan ku sauka gabanin sallar azahar zuwa cikin *Makkah* domin yin dawafin hajji, kuma ku yi sa'ayi tsakanin Safah da Marwah. Sa'annan ku koma Minah. *Kuma yin dawafi, da aikata sa'ayi, tare da jifan Shedan da aski, shine kun samu abinda ake kiransa: Tahallulus Saniy, kuma komai ya halatta a gare ku, har kwanciya da Matanku.*

**Ya ku Mutane!** Lallai Mahajjaci a ranar idi yana ayyuka ne guda hudu: Jifan jamrah, sa'annan yanka, sa'annan aski, sa'annan dawafi da sa'ayi. Wannan kuma shine jeranta ayyukan, wanda yafi falala. Sai dai idan Mutum ya gabatar da wani akan wani, sai ya yi aski gabanin yanka ga misali, to babu komai. Kuma da za ku jinkirta dawafi da sa'ayi, har sai kun dawo garin Makkah daga *Minah,* to babu komai. Kuma da za ku jinkirta yanka zuwa ranar goma sha uku, sai ku yi shi a garin Makkah, babu komai, musamman idan akwai bukatar hakan, da maslaha. Ku kwana daren goma sha 11 a *Minah.* Idan Rana ta yi zawali (lokacin azahar) sai ku yi jifa jamraat guda uku, ku fara da jamrah ta farko, sa'annan ta biyu, sannan ta karshe; wato akabah, kowane daya da tsakuwa guda bakwai, za ku rika yin kabbara (*Allahu Akbar),* tare da kowace tsakuwa. Lokacin jifa, a ranar idi, ga mai iko (lafiyayye), daga fudowar Rana ne, Mai rauni kuma tun daga karshen dare ne. Karshen lokacin kuma zuwa faduwar rana. Lokacinsa kuma a sauran kwanakin (bayan idi), daga zawali ne, zuwa faduwar Rana. Amma baya halatta a yi jifan gabanin zawali. Kuma ya halatta ayi jifan a cikin dare, idan

akwai cunkoso mai tsanani, a cikin yini. Wanda ba zai iya jifa ba, ko saboda kasancewarsa karami, ko tsufa, ko cuta, to yana da damar ya wakilta wanda zai masa jifan. Kuma babu laifi, wakilin ya yi jifa wa kansa, da wanda yake wakilta a tsayuwa daya, sai dai zai fara jifa ga kansa. Idan kuka yi jifan ranar sha biyu 12, to lallai hajji ya kare. Kuma kuna da zabi kan dawowa Makkah, ko kuma ku sake kwana a *Minah* zuwa yini na 13 domin ku sake jifan, bayan *Azahar* ga wuraren jifan guda uku; Wannan kuma shine yafi, saboda shine aikin Annabi .

Idan kuka so ku bar garin *Makkah,* Sai ku yi *Dawafin bankwana.* Sai dai babu *dawafin bankwana.* Ga Mai haila da kuma mai jinin haihuwa (nifasi), kuma ba a shar'anta musu zuwa *jikin kofar Masallaci da tsayuwa a wurinsa ba.*

## TAMBAYOYI AKAN HAJJI

**5.** Ga wa hajji yake wajaba?

**a.** ..........................................................................................

**b.** ..........................................................................................

**c.** ..........................................................................................

**d.** ..........................................................................................

**e.** Mace kuma dole a samu karin sharadi; wanda da shine..........................................................................................

**6.** Nawa ne yawan rukunnan hajji? O 2 O 3 O 4

*7.* *Ihraam* rukuni ne daga cikin rukunnan hajji, kuma ma'anarsa ita ce: ka sanya mayafai biyu farare, daga mikati ( E – A'a ).

**8.** *Dawaful Ifadah* ya banbanta da *Dawafuz ziyarah*; Na farkon rukuni ne, na biyun kuma sunnah ( E – A'a ).

**9.** Annabi ﷺ ya yi hajji ne sau uku ( E – A'a ).

**10.** Wajibi ne a sauke hajji, da gaggawa ( E – A'a ).

**11.** Mutanen Madinah za su yi *ihrami* daga mikatin *Yalamlam* ( E – A'a ).

**12.** Mikatin *umrah* na zamani shine watan *Ramadana* ( E – A'a ).

**13.** Cike wuraren da babu komai, a jumloli masu zuwa: Hajj da Umrah ....... ... ........... a tsawon rayuwa, sau daya ........ . Kuma wanda ya yi hajji, bai yi .............. ba, kuma bai yi ...................... zai fita daga zunubansa kamar ranar da uwarsa ta haife shi, Kuma hajji kubutacce lafiyayye, bashi da wani sakamako

face ………………..

**14**. Mutanen garin *Makkah* za su yi haramarsu ta hajji, daga *Tan'im* ( E – A'a ).

**15**. Mace zata sanya farin tufafi ne, a lokacin *ihraminta* ( E – A'a ).

**16**. Mustahabbi ne ga maniyyacin harama ya sanya turare a jikin, …………..
kuma kada ya sanya turare a ………………..

**17**. Mace bai halatta ta sanya dinkakke kaya ba ( Gaskiya ne – A'a).

**18**. Baya halatta ga mai harama ya daura belt ( E, A'a ).

**19**. Mace, a wurin harama bata sanya ………. kuma bata sanya …………..

**20**. Sunnah ne bude saman kafadar hannun dama (Id-diba'i) a ……………….
O *Dawafin Umrah* O *Dawaful kudum* O *Dawafuz* ziyarah. O Na farko, da na biyu O Duka da aka ambata.

**21**. Mustahabbi ne ya yi *sa'ayi* tsakanin Safah da Marwah da gudu ( E – A'a ).

**22**. *Sa'ayi* yana farawa ne daga ………….. Ya kuma kare a ………………

**23**. Mahajjata suna *barin filin Arafah* ne kafin faduwar Rana (Magriba) ( E – A'a ).

**24**. Tsayuwar *Arafah* wajibi ne daga wajiban *Hajj* ( E – A'a ).

**25**. Ayyukan hajji suna farawa ne daga ranar ……. Su kuma kare, a ranar ……

**26**. Ba a shar'anta hawa dutsen *Arafah* ba ( E – A'a ).

**27**. Yin hadaya (yanka dabba) wajibi ne *ga Tamattu'i* da mai hajjin *kirani*, Mai i*fradi*

kuma sunnah ne ( E – A'a ).

**28.** Ana yanke fadin *Talbiyyah* ne daga lokacin jifan jamratul akabah na ranar idi ( E – A'a ).

**29.** Idan Mahajjaci ya ajiye dutsensa a cikin kewayen jifa, ba tare da ya samu abinda yake tsaye ba, jifansa ta inganta ( E – A'a ).

**30.** Mahajjaci a ranar goma/12, zai yi jifansa ne a wurare uku na jifa ( E – A'a).

**31.** Lokacin fara jifa, a ranakun Tashrik (11. 12, da 13) yana farawa ne bayan shigan lokacin azahar ( E – A'a ).

**32.** Bayan jifan jamratul akabah, mustahabbi ne a tsaya ayi addu'a ( E – A'a ).

**33.** Da Mutum zai jinkirta *Dawafin ifadah* har zuwa lokacin da zai fice daga garin *Makkah*, to hakan ya isar masa, ba sai ya yi *Dawafin* bankwana ba. Kuma *dawafin ifadha* kamar *Dawafin umrah* ne, saidai wurin …… da …………

**34.** Mai hajjin *kirani* da *Ifradi* wajibi ne akansu su yi *Sa'ayi* guda, yayin da Mai hajjin *tamattu'i* zai yi *Sa'ayi* guda ………………..

**35.** Ambaci hukuncin ayyukan da suke tafe:

| **Aiki** | **Hukuncinsa** |
|---|---|
| Hajjin karamin yaro | |
| Hajjin Mace, ba tare da Muharrami ba. | |
| Hajjin wanda ake binsa bashi. | |

# DARASI NA GOMA SHA BIYAR

***Sifantuwa da dabi'un da aka shar'anta su ga kowane Musulmi***

*Daga cikinsu: Yin gaskiya, da amana, da kamewa, da kunya, da jarumta, da kyauta, da cika alkawari, da nisantar dukkan abinda Allah ya haramta, da kyautata makwabtaka, da taimakon mabukata gwargwadon iko, da sauran halayen da Alkur'ani da Sunnah suka zo da lamarin shara'anta su.*

**Ta'aliki mai muhimmanci:**

-(Gaskiya) Wato, ya yi gaskiya wa Allah cikin zantukansa, da ayyukansa da akidarsa. Kuma ya yi gaskiya ga Bayin Allah. Kishiyarta kuma ita ce: karya.

-(Amana) Farilla ce mai girma, wanda Mutum ya dauke ta. Kuma amana kishiyar ha'inci ne.

-(Kamewa) daga aikata dukkan aiki na haram.

-( Kunya) Dabi'a ne da take sanya Mutum aikata abin yabo, ya nisanci abin ki.

-(Kyautata makwabtaka) Kuma hakan yana hukunta, ka rika rintse ganinka, kada ka leka asiri ko al'aurar makwabtanka.

-(Taimakon mabukata) Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya kwaranye wa Musulmi wani bakin cikin Duniya, Allah zai kwaranye masa bakin-cikin yinin kiyama. Kuma wanda ya saukaka wa Mutumin da yake cikin wahala, Allah zai saukaka masa a Duniya da Lahira. Kuma wanda ya rufa asirin Musulmi a Duniya, Allah zai rufa asirinsa a Duniya da Lahira. Allah yana taimakon Bawa matukar Bawan yana taimakon Yan'uwansa", Muslim ya ruwaito shi.

.

## DARASI NA GOMA SHA SHIDA

### *Aiki da ladubban Musulunci*

` Daga cikinsu akwai: *Yin sallama, sake fiska, ci da hannun dama, sha da hannun dama, fadin:* BismilLahi *a lokacin farawa,* da fadin: Alhamdu lilLahi bayan gamawa, fadin: *Alh*amdu lilLahi*" a lokacin atishawa, da yin addu'a ga mai atishawa, idan ya yi godiyar All*ah, *da ziyartar maras lafiya, da bin gawa domin yin sallah a gare ta, da bunne ta. Da aiki da ladubban shari'a wajen shiga Masallaci ko gida, da fita daga gare su, da lokacin bulaguro, da ladduban tarayya da iyaye biyu, da makusanta, da makwabtai, da manya da yara, da yin barka da samun haihuwa, da addu'ar albarka ga aure, da yin jaje da ta'aziya a lokacin musiba, da sauran ladubban shari'a, wajen sanya kaya, da tube su, da sanya takalma.*

**Ta'aliki mai muhimmanci:**

-Fadinsa: "Sallama" cikakken lafazinsa shine: *"Assalaamu alaikum wa rahmatul Lahi wa barakatuhu",* za ka yi sallamar ga wanda ka sani, da wanda baka sani ba, kuma zaka amsa wa Mutumin da ya maka sallama.

-Fadinsa: "Ci da sha da hannun dama" wannan wajibi ne: kuma mustahabbi ne ci da 'yan yatsu uku. Haka shima dauka da bayarwa da hannun dama.

-Fadinsa: "Da ambato sunan Allah, a lokacin farawa" wato ya ce: BismilLahi.

--Fadinsa: "Da yin godiya wa Allah a lokacin gamawa" da abinda ya tabbata kamar fadinsa: "Godiya ta tabbata ga Allah, wanda ya ciyar da ni wannan abincin, kuma ya azurta ni da shi, ba tare da dabarata ko karfina ba".

-Kuma an shar'anta masa, ya ci daga abinda yake gabansa, kuma kada ya aibanta abinci.

- Fadinsa: "Da yin godiya bayan atishawa" wato, a ce: *Alhamdu lilLahi*".

-Fadinsa: *"Da yin addu'a ga mai atisha, idan ya yi godiyar Allah"* Wato mu ce masa*: Yarhamukal Lahu, sannan sai mai atishawan ya amsa da cewa:* "*YahdikumulLahu wa yuslihu balakum*".

-Fadinsa: "**Da ziyartar maras lafiya**" Ma'ana, zai ziyarce shi, kuma ya maimaita hakan a lokutan da suka dace, saidai kada ya tsawaita zama a wurinsa, kuma kada ya rika sanya shi yana debe tsammani daga rahamar Allah.

-Fadinsa: "**Da rakiyar gawa, domin yin salla a gare ta, da bunne ta**", Rakiyar ga Maza ne, banda Mata.

Fadinsa: "**Da ladubban shari'a, wajen shiga Masallaci da gida, da fita daga gare su**", Mutum zai gabatar da kafar dama, a yayin shiga Masallaci, kuma ya ce: *"BismilLahi, was salaatu was salaamu ala rasulilLahi. Allahummaf tah liy abwaaba rahmatik* / Da sunan Allah, Salati da sallama su kara tabbata ga Manzon Allah, Ya Allah ka bude min kofofin rahamarka". Kuma zai fara gabatar da

kafarsa ta hagu, lokacin fita daga Masallaci, ya ce: "*bismilLahi*, *was salaatu was* salaamu ala rasulilLahi. Allahumma inniy as'aluka min fadlik / Da sunan Allah, Salati da sallama su kara tabbata ga Manzon Allah. Ya Allah ka buda min daga falalarka".

Amma dangane da shiga gida kuma da fita, to sai ya gabatar da kafarsa ta dama. Kuma ya fada a lokacin fitansa: "*BismilLahi tawakkaltu alal Lahi, wala haula wala kuwwata illa bilLah. Allahumma inniy a'uzu bika an adilla au udalla, au azilla au uzalla, au azlima au uzlama, au ajhala au yujhala alayya* / " Da sunan Allah, Ina dogaro ga Allah, Babu wayo babu karfi face ga Allah. Ya Allah! Ina neman tsarinka kada na batar ko a batar da ni, ko na zame ko a zamar da ni, ko na yi zalunci, ko a min zalunci, ko na yi wauta ga wani, ko a min wauta".

Idan kuma Mutum zai shiga gida sai ya ce: "*Allahumma inniy as'aluka khairal mauliji wa khairal makhraji. BismilLahi walajnaa wa bismilLahi kharajna, wa ala rabina tawakkalna* / Ya Allah, Lallai ina rokonka alherin shiga da alherin fita. Da sunan Allah, muke shiga, da sunan Allah muke fita, kuma ga Ubangijinmu muke dogaro", Sannan ya yi sallama ga iyalansa.

-Fadinsa: "**Da addu'ar neman albarka lokacin aure**",wato ya ce: BARAKAL LAHU LAKUMA, WA BARAKA ALAIKUMA, WA JAMA'A BAINAKUMA FIY KHAIRIN; Allah ya muku albarka, Allah ya sada ku cikin alheri.

-Fadinsa: "**Da jaje da taziya a lokacin musibu**", Kuma ta'aziya tana kasancewa ne cikin, kwanaki 3; ba a karawa akan haka.

## DARASI NA SHA BAKWAI

### *TSAWATARWA KAN SHIRKA DA NAU'UKAN SABO*

Kiyaya da tsawatarwa kan shirka da nau'ukan sabo; Daga cikinsu akwai: *laifuka bakwai masu halakarwa: Shirka wa Allah, da sihiri, da kashe rai wanda Allah ya haramta kashe ta face da hakki, da cin riba, da cin dukiyar maraya, da guduwa a ranar yaki, da yin kazafi ga kamammun muminai.*

*Kuma daga cikinsu akwai:* Bijire wa iyaye, da yanke zumunci, da shaidar zur, da rantsuwar karya, da cutar da makwabci, da zaluntar Mutane a cikin jininsu da dukiyarsu da mutuncinsu, da shan abinda yake bugarwa, da wasan lido, na caca, da *cin naman Mutum, da annamimanci, da wasun haka, cikin abinda Allah Mabuwayi da daukaka ya yi hani akansu, ko ManzonSa.* ﷺ

**Ta'aliki mai muhimmanci:**

-Fadinsa: "Shirka wa Allah" ya kunshi Babba da karamar shirka.

-Fadinsa: "Da sihiri" Daga cikinsa akwai sihirin raba masoya ko hada su. Duk wanda ya aikata shi, ko ya yarda da shi ya kafirta. Kuma haramun ne zuwa wurin masu sihiri, ko shiga shafukansu na intanet, ko kallon tashoshinsu, ko karatun jaridu da majalloli wanda akwai buruji ko masaukan taurari a cikinsu. Kuma bai halatta a warware sihiri da sihiri ba, a'a ana warware shi ne da rukiyyah ko addu'o'i na shari'a, da magani na halal kamar yin kaho.

-Fadinsa: "**Da kashe rai wanda Allah ya haramta**" sawa'un ran Musulmi ne, ko na kafirin amana, ko kafirin alkawari, ko wanda aka bashi aminci.

« **Face da hakki**" sune guda uku: "Rai da rai, da mazinacin da ya taba aure, da wanda ya bar addininsa, ya fice daga jama'a".

-Fadinsa: "**Maraya**" Shine wanda Mahaifinsa ya mutu, alhalin bai balaga ba.
-Fadinsa: "**Da juyawa a lokacin jama'a**" Ana nufin runduna ko sojojin Musulunci masu yaki fi sabilil Lahi.
-Fadinsa: "**da yin kazafi ga kamammu** (muhsanaat)" ana nufin; 'ya'ya (ba bayi ba), Ba wai kawai masu aure ba.
-Fadinsa: "**Da rantsuwar karya**" haka kuma, yin rantsuwa da wanin Allah, kamar rantsuwa da Annabiﷺ, ko rantsuwa da matsayi, ko rayuwa, ko da kabari, ko da furfura, da sauransu.
-Fadinsa: "**Ludo, wanda shine caca**" kuma shine duk wata mu'amalar da take tsakanin samun moriya da faduwa, kamar: Yansiyb.
-Fadinsa: "**Da cin naman Mutum**" Annabiﷺ ya yi bayanin ma'anarta,a cikin fadinsa: "Ambaton dan'uwanka da abinda yake ki".
-Fadinsa: "**Da annamimanci**" Wanda shine yawo da magana tsakanin Mutane, domin bata tsakaninsu.

**Hukuncin musabaka, da neman wani ya rinjayi wani**

**Wanda ya halata (takowace fiska), za a sanya wani abu a kai, ko a'a:** Shine na dokuna, da rakuma, da kibiyoyi, saboda fadin Annabi ﷺ: "Babu musabaka (tsere) sai cikin abinda yake da huffi (rakumi) da kofato (doki), da kuma kibau" (Abu Dawud, ya ruwaito shi).

**Haramun ta kowace fiska:** Ludo da shadranj, da abinda ya yi kama da su.

**Ya halatta, idan ba a sanya komai ba. Idan kuma aka sanya wani abu bai halatta ba:** Wannan ya kunshi dukkan nau'ukan musabaka da tsere, banda nau'ukan da suka gabata.

## DARASI NA SHA TAKWAS

### SHIRYA MAMACI DA YI MASA SALLAH DA BUNNE SHI

**Na farko:** An so a rika lakkanawa wanda yake gargarar mutuwa kalmar LA ILAHA ILLAL LAHU; saboda fadin Manzon Allah ﷺ: "ku lakkana wa mamatanku kalmar la ilaha illal Lahu".

Abinda aka nufa da mamata a nan: wadanda alamomin mutuwa suka bayyana tare da su.

**Na biyu:** Idan aka tabbatar da mutuwarsa, sai a rufe idanunsa, a daure gemunsa, kamar yadda sunnah ta zo da shi.

**Na uku:** Wajibi ne a yi wanka ga Musulmin da ya mutu, matukar ba shahidin da ya mutu a wurin yaki ba ne, saboda shahidin yaki ba a yi masa wanka, ba a yi masa sallah, haka ake rufe shi a cikin kayansa, saboda Annabi ﷺ bai wanke wadanda suka yi shahada a yakin uhudu ba, haka bai yi musu sallah ba.

**Na hudu: SIFAR WANKAN GAWA:** Za a suturce wa mamaci al'aurarsa, sannan a daga shi kadan, sai a tatse cikinsa a hankali, sai wanda zai yi masa wankan ya daura kyalle ko makamancinsa (handglove) a hannunsa, sai ya masa tsarki da shi. Daga nan sai ya masa alwala irin ta sallah, sannan ya wanke masa kansa da gemunsa da ruwa da kuma magarya, ko makamancinta, sannan ya wanke bangaren damansa, sannan sai bangaren hagu. Zai masa hakan har sau uku. A kowanne wanka zai bi da hannunsa ta cikinsa yana dan dannawa kadan-kadan, idan wani abu ya fito (daga al'aurarsa) ya wanke masa. Sai kuma ya toshe duburarsa da auduga ko makamacinta. Idan abin bai dena fitowa ba, sai ya toshe masa ita da tabon kasa, ko ya yi amfani da hanyoyin likitanci na zamani; kamar sanya gum, ko plaster ko makamancinsu.

Sannan ya sake masa alwala. Idan aka masa wanka sau uku, sai bai fita ba, to sai a kara adadin zuwa biyar ko bakwai. Sa'annan a tsane shi da tawul. Sannan a shafa masa turare a hamatarsa da matsematsinsa da makamantansu, da kuma guraben sujaddarsa. Da za a shafe gaba dayan jikin mamacin da turare to hakan shi ne yafi. Kuma an so a kunna turaren wuta a gaba dayan likafaninsa. Idan ya zama gashin bakinsa ko faratunsa sun yi tsawo dayawa sai a rage su, idan kuma aka bar su haka shima babu laifi. Ba zai taje masa kai ba, ko ya aske masa mara ko ya yi masa kaciya, domin babu dalilin da ya yi nuni akan hakan. Mace kuma za a yi mata kitso ne (yawo) guda uku daga goshinta su yi bayanta .

**Na biyar: SANYA WA MAMACI LIKKAFANI:** Abinda aka fi so shi ne: a yi likkafani wa mamaci namiji a cikin tufafi guda uku farare, ba tare da anyi masa Riga ko Rawani ba; kamar yadda aka yi wa Annabi ﷺ, sai a saka shi a cikinsu shigarwa. Idan kuma aka masa likkafani da Riga da Izari da Mayafi; to babu laifi.

Mace kuma ana sanya ta a cikin Likkafani biyar: Riga, da Zani, da dan kwali, sai kuma Mayafai biyu.

Yaro namiji, ana masa likkafani cikin tufafi daya zuwa uku.

Karamar yarinya kuma, cikin riga daya da mayafai biyu.

Likkafani daya wadatacce wanda zai rufe jiki gaba daya; shi ne wajibi ga mace ko namiji.

Amma idan mamacin ya dauki harama da umrah ko hajji sai ya rasu; to za a yi masa wanka ne da ruwa da magarya, sannan a lullube shi a cikin ihramansa ko wasunsu, baza a rufe kansa ko fuskarsa ba, ba za a sanya masa turare ba; domin za a tashe shi ranar alkiyama yana yin Talbiyya (wato yana cewa: labbaikal Lahumma labbaik), kamar yadda hadisi ingantacce ya zo daga Annabi Muhammadu ﷺ

Amma idan maniyyaciya ce, (da hajji ko umra) wato mace, to za a shirya ta ne kamar ba maniyyaciya ba, sai dai itama ba za a sanya mata turare ba, baza a rufe fuskarta da nikabi ba, ba za a sanya mata safar hannu ba, za a rufe fuskarta da hannayenta da likkafaninta ne kadai, kamar yadda bayanin ya gabata, a sifar yadda ake sanya wa Mace likkafani.

**Na shida:** Wanda ya fi kowa cancantar wanke mamaci namiji, da kuma yi masa sallah da rufe shi, shi ne wanda mamacin ya yi wasici da shi, sannan sai mahaifi, sai kaka, haka za a yi ta duba wanda ya fi kusa da shi a cikin magadansa. Wacce kuwa tafi cancantar wanke Mace ita ce wanda ta yi wasici da ita, sa'annan sai mahaifiyarta, sai kakarta, sannan sai wanda ta fi kusanci da ita a cikin mata.

Kowanne daya daga cikin ma'aurata biyu zai iya wanke dan'uwansa, (wato miji ya wanke matarsa, ko ita ta wanke shi); domin sayyidina Abubakar Assidik matarsa (Asma'u bnt Umais) ce ta wanke shi. Shi kuma sayyidina Aliyu shine ya wanke matarsa –wato, Fatima, Allah ya kara yarda a gare ta.

**Na bakwai: SIFAR SALLAR GAWA:** za a yi kabbara hudu ne, a kabbara ta farko ana karanta Fatiha, idan aka kara da gajeriyar sura ko aya daya ko biyu ya yi kyau, saboda ingantaccen hadisin da ya zo daga Abdullahi dan Abbas a kan hakan. A kabbara ta biyu kuma sai a yi salati ga Annabi Muhammadu kamar yadda ake yi a Tahiya (salatin ibrahimiyya). Sai ayi kabbara ta uku, a ita ne ake yin addu'a kamar haka:

« Ya Allah Ka gafarta wa wadanda suke raye a cikinmu da matattunmu, da wadanda suke nan da wadanda basu nan, da manyanmu da kananamu, Mazanmu da Matanmu. Ya Allah wanda ka rayar da shi a cikinmu, to Ka rayar da shi akan tafarkin Musulunci, wanda kuwa Ka karbi rayuwarsa to Ka karbe ta akan Imani. Ya Allah Ka gafarta masa Ka ji kansa, Ka ba shi lafiya Ka yi masa rangwame, Ka kyautata masaukinsa, Ka yalwata mashigarsa, Ka wanke shi da Ruwa da kankara da kuma Raba, Ka tsarka

kazanta, Ka canza masa gida mafi alheri daga gidansa, da iyali mafiya alheri daga nasa, Ka shigar da shi Aljannah, ka tsare shi daga azabar kabari da azabar Wuta, ka yalwata masa kabarinsa Ka haskaka masa shi, ya Allah kada Ka haramta mana ladansa, kada kuma Ka batar da mu a bayansa.

Sannan sai ya yi kabbara ta hudu, ya yi sallama daya bayanta a hannun dama. Kuma anso a daga hannaye a kowacce kabbara.

Idan kuma gawar mace ce sai a yi anfani da lamirin mata, a ce: ya Allah Ka gafarta mata ….har karshe). Idan kuma sama da Mutum daya ne sai a ce: (Ya Allah Ka gafarta musu….. har karshe).

Idan gawar yaro ce, sai a ce: (Ya Allah ka sanya shi ya zama marigayi kuma taska ga iyayensa, mai ceto abin amsawa. Ya Allah! Ka nauyaya ma'auninsu da shi, Ka girmama ladansu da shi, Ka riskar da shi ga muminan magabata nagari, Ka sanya shi karkashin rainon Annabi Ibrahim عليه السلام, Ka kare shi daga azabar jahimu da rahamarka.

Sunnah -a yayin sallah- ita ce: limamin ya tsaya daura da kan mamaci Namiji. Mace kuma a tsakiyarta, idan kuma mamatan sun hada da Maza da Mata, to namiji zai zamto yana bin liman ne –wato daga liman sai gawar Namiji-, ita kuma Mace tana bin alkibla. idan kuma akwai gawar yara sai Namiji babba ya zamto shi ne kusa da liman, sai karamin yaro, sai babbar Mace, sai karamar yarinya. Kan karamin yaro, zai kasance a setin kan gawar babban Mutum, tsakiyar babbar Mace kuma a setin kawukansu. Haka nan karamar yarinya kanta zai zamto a setin kan babbar Mace, itama tsakiyarta zai zamto yana dai-dai da kan Namiji;

Su kuma sauran Masallata za su zamto gaba dayansu a bayan liman, saidai wanda bai samu wuri a bayan liman ba, sai ya tsaya kusa da shi a hannunsa na dama.

**Na takwas: SIFAR BUNNE MAMACI**: Abinda aka shar'anta shi ne zurfafa kabari gwargwadon yadda zai kai kwankwason Mutum, sannan

Lahadu din ya zama a bangaren alkibla –za a tona shi-, kuma za a saka Mamacin ne ta bangaren damansa, sai a warware kullin likafanin, ba janye zaren za a yi ba, kuma ba za a bude fuskarsa ba; Namiji ne ko Mace, daga nan sai a sanya tubala a daure su da kwababbiyar laka; domin kada kasa ta shiga cikin kabarin. Idan kuma ba a sami Tubali ba sai ayi amfani da katanga/kasko, ko duwatsu, ko itace wanda zai iya hana kasa shiga cikin kabarin, sannan a tura turbaya a kai. An so yayin saka gawar a kabarinta a ce: *BismilLah wa ala millati Rasulillah*. Kuma za a daga kabarin gwargwado taki daya, in an sami dama sai a dora dan dutse a kai, sai kuma a yayyafa ruwa a samansa.

Abin da aka shar'anta ga wadanda suka yi rakiyar gawa shi ne: mikewa tsaye a makarbarta bayan rufe mamacin don su yi masa addu'a, saboda Manzon Allahﷺ ya kasance yana mikewa tsaye ne idan aka gama rufe gawa sannan ya ce: "ku nema wa dan'uwanku gafara, ku roka masa tabbatuwa, domin a yanzu za a masa tambayoyi".

**Na tara:** Shari'a ta yarda ga wanda bai samu damar yi masa sallah ba ya yi masa bayan rufe shi da kimanin wata daya kawai, domin Annabi ﷺ ya aikata hakan. Amma idan aka haura wata daya to bai halatta ayi sallah a makabarta ba, saboda rashin dalilin da ya nuna cewa Annabi SAW ya aikata hakan bayan wata daya daga rufe gawa.

**Na goma:** Haramun ne wadanda aka yiwa mutuwa su yi wa Mutane abinci, saboda hadisin Jarir dan Abdullahi Albajaliy -Allah ya yarda da shi- ya ce: (*Mun kasance muna kirga taruwa a gidan wanda dan'uwansu ya rasu, da kuma yin abinci bayan rufe gawa daga cikin kururuwar Mutuwa*). Amma su yi abinci don su ci, ko su baiwa bakinsu babu laifi. Kuma an shar'anta wa yan'uwa da makwabta su yi musu abinci, saboda lokacin da labarin kashe Ja'afar dan Abi Talib ya zo ga Manzon Allah ﷺ sai ya umurci iyalansa da su shirya abinci ga mutanen gidan Ja'afar, ya ce: "*Hakika abinda zai shagaltar da su ya same su*".

Babu laifi idan yan'uwan mamaci suka kira makwabtansu ko wasu domin cin abincin da aka kawo musu kyautarsa. Kuma wannan bashi da wani

kayyadajjen lokaci a iyakar saninmu da shari'a.

**Na goma sha daya:** Bai halatta Mace ta yi takabar sama da kwana uku ga wani mamaci ba, face ga Mijinta, shi kam wajibi ne ta yi masa takabar wata hudu da kwanaki goma, sai in ya barta da ciki, sai takabar ta zamto zuwa haihuwarta, saboda zuwan ingantattun hadisai daga Annabi Muhammadu ﷺ akan hakan.

Namiji kuwa haramun ne ya yi takaba ga wani mamaci dan'uwansa ne ko ba dan'uwansa ba.

**Na goma sha biyu:** An shar'anta wa Maza ziyartar makabartai, lokaci bayan lokaci; domin yiwa mamatan addu'a, da nema musu rahama, da kuma tuna mutuwa da abinda zai zo bayan mutuwar, saboda fadin Manzon Allah: "***Ku rika ziyartar makabartai; domin suna tunatar da ku Lahira***".

Kuma Manzo Allah ya kasance yana koya wa sahabbansa addu'ar ziyartar makabartai kamar haka: "Amincin Allah ya tabbata a gare ku, Ya ku ma'abuta wannan gida daga Muminai da Musulmai, mu ma za mu riske ku in Allah Ya yarda, Allah ya ba mu lafiya mu da ku. Allah ya gafarta wa wadanda suka rigaye mu da jimawa da mutuwa, har da wadanda basu jima ba".

Mata kuma basu yin ziyarar makabartai saboda Manzon Allah ya la'anci mata masu yawan ziyartar makabarta, kuma saboda tsoron fitina da gajen hakuri idan suka yi ziyarar .

Haka nan baya halatta ga Mata su raka gawa zuwa makabarta, saboda Annabi ya hana su, amma yi wa mamaci sallah a cikin Masallaci ko a wajensa halal ne ga Maza da Mata.

Wannan shi ne karshen abinda ya sawwaka.

**NAU'UKAN ZIYARTAR KABURBURA**

**Ziyara ta shari'a**
Ya yi niyyar tuna Lahira, kuma ta kasance a garin da yake ba tare da ya yi bulaguro (daga gari zuwa gari) saboda ita ba, kuma ya yi niyyar addu'a ga kansa da matattu da abinda ya tabbata a sunnah, kuma ba zai aikata abinda ya saba wa shari'a ba.

**Ziyara ta bidi'a**
Ya yi niyyar rokon Allah, a wurin kaburbura.

**Ziyara ta shirka**
Ita ce ya yi niyyar rokon wanda yake kwance a cikin kabarin.

## TAMBAYOYI KAN ABINDA YA GABATA

1. Kiyaye tsari da ladduban shari'a yana cikin halayen Musulmi ( E – A'a ).

2. Addinina yana umurtata da abotar Mutanen banza, da nisantar Mutanen kirki ( E – A'a ).

3. Musulunci ya koyar da mu, cewa mu kyautata mu'amala, tare da hadimai, da ma'aikata, da wasunsu ( Haka – A'a ).

4. Zan yi abotar Mutumin da yake cutar da Mutane da harshensa, da hannunsa ( E – A'a ).

5. Idan wani ya zage ni, to nima zan rama; na ji dadi ( Haka – A'a).

6. Musulunci ya koyar da ni, cewa, na taimaki mabukata, da masu rauni ( Haka – A'a).

7. Daga cikin hakkin Musulmi akan dan'uwansa, akwai ya ziyarce shi idan bashi da lafiya, domin ya masa addu'ar waraka ( Haka – A'a ).

8. Neman sanin sirrin makwabta yana cikin sifofin muminai ( E – A'a ).

9. Mutanen da Allah yafi so, sune wadanda suka fi amfanar da Mutane ( E – A'a)

10. Addu'ar fita daga gida ita ce: "BISMILLAH WALAJNA, WA BISMILLAH, KHARAJNA, WA ALAL LAHI, RABBINA TAWAKALNA" (E – A'a).

11. Zan fada ga wanda ya min addu'ar rahama, bayan atishawa: " YAHDIYKUMUL LAHU, WA YUSLIHU BALAKUM" (E – A'a).

**12.** Yin zikiri yana kiyaye Musulmi, kuma yana kusantar da shi ga Allah Mabuwayi da daukaka (E – A'a).

**13.** Menene alamar kana son dan'uwanka Musulmi?

.........................................................................................................

**14.** Yana daga abinda yake raunana imani: Yin hassada ga dan'uwanka Musulmi (E – A'a ).

**15.** Menene sabubban da suke janyo maka soyayyar 'yan'uwanka?

.............................................................................................................

**16.** Abinda aka haramta kawai, daga cikin abubuwan da suke sanya maye, shine abinda aka kira shi da suna giya (E – A'a ).

**17.** Makruhi ne, fura a cikin abin ci, da abin sha (E – A'a ).

**18.** Mustahabbi ne, tsotse yatsu, bayan cin abinci, gabanin wanke su (E – A'a ).

**19.** Tsakaitawa, shine salon da ake so, dangane da abinci, da tufa, da kayan ado (E – A'a ).

**20.** Wanda yafi cancantar, ya masa wanka, ya masa sallah, ya shigar da shi kabarinsa shine: ................ Sannan sai ..................sannan sai...................sannan sai..............

**21.** Biyan bashi ga Mamaci: ......... O Wajibi ne O Sunna ne O Halal ne.

**22.** Hukuncin bunne Mamaci ...... O Sunna ne O Wajibi ne O Farillar kifaya.

**23.** Hukuncin lakkana wa Mai mutuwa "La ilaha illal Lahu" ............
O Wajibi ne O Sunnah ne O Haramun ne.

**24.** Hukuncin halartar wanda ba taimako zai yi kan wankar gawa ba.........
O Haramun ne. O Ya halatta. O Makaruhi.

**25.** Ana warware kullin likkafani, idan aka shigar da Mamaci kabari (E – A'a ).

**26.** Dayan Ma'aurata biyu, ba zai wanke dan'uwansa ba, saboda kullin aure ya warware, daga aukuwar mutuwa (E – A'a ).

**27.** Namiji da Mace, suna da damar yin wanka ga wanda ........................

**28.** Wanda bai samu sallah, a gawa ba, zai iya masa salla a ........tsawon .....

**29.** Kuka ga mamaci, ya halatta ta kowace fiska (E – A'a ).

**30.** Ana sanya mamaci a cikin lahadun kabarinsa, yana fiskantar alkibla (E – A'a ).

## ABINDA KE CIKIN LITTAFIN


Sharhin mukaddimah ........................................................................2

**Sharhin darasin farko:** *Suratul Fatiha* da gajerun surori.............................4

Zababbun wurare daga " *Taisirul Karimir Rahman*" ...............................6

Tambayoyi a kan mukaddimah, da tafsiri ...........................................36

**Sharhin darasi na Biyu:** Rukunnan *Musulunci* ....................................56

**Sharhin darasi na Uku:** Rukunnan *Imani*...........................................64

**Sharhin darasi na Hudu:** Nau'ukan *Tauhid* da *Shirka*..........................70

**Sharhin darasi na Biyar:** *Ihsan*.......................................................75

Tambayoyi akan *Tauhidi*....................................................................76

**Sharhin darasi na Shida:** *Sharuddan Sallah*........................................82

**Sharhin darasi na Bakwai:** *Rukunnan Sallah*......................................86

**Sharhin darasi na Takwas:** *Wajiban sallah*.........................................88

**Sharhin darasi na Tara:** *Tahiya* ......................................................89

**Sharhin darasi na goma:** Sunnonin sallah...........................................90

**Sharhin darasi na sha daya:** Abubuwan da suke bata sallah.................92

*Sujjadar rafkanuwa*............................................................................94

Sifar sallah a takaice a cikin fotuna.....................................................95

Sallah da hukunce-hukuncenta, a takaice.........................................105

Tambayoyi akan sallah.......................................................................108

**Sharhin darasi na goma sha biyu:** Sharuddan alwala..........................113

**Sharhin darasi na goma sha uku:** Farillan alwala..............................115

**Sharhin darasi na goma sha Hudu:...........................................116**

Abubuwan da suke warware alwala.........................................116

Sifar alwala, a takaice, a cikin fotuna.........................................118

Karin bayani akan *Tsarki*.........................................120

Tambayoyi akan Tsarki.........................................125

Karin bayani akan *Zakkah*.........................................128

Tambayoyi akan Zakkah.........................................133

Karin bayani akan Azumi.........................................137

Tambayoyi akan Azumi.........................................144

Karin bayani akan *Hajji* da *Umrah*.........................................147

Tambayoyi akan Hajji.........................................156

**Sharhin darasi na goma sha Biyar:.........................................160**

Sifantuwa da halayen Musulunci.........................................160

**Sharhin darasi na goma sha Shida:.........................................161**

Ladabtuwa da ladduban Musulunci.........................................161

**Sharhin darasi na goma sha Bakwai:.........................................164**

Tsawatarwa kan *Shirka* da *Sabo*.........................................164

**Sharhin darasi na goma sha Takwas: Shirya Mamaci**.........................167

Tambayoyi akan Ladduba, da Sallar gawa.........................................174

## Littatafan da aka duba


**[1]** "Alkur'ani Mai girma".

**[2]** "Taisirul Karimir Rahmaan fi Tafsiri Kalamil Mannaan" Na Sheikh Abdur-Rahman bn Nasirus Sa'adi –Allah ya yi masa rahama- (ya 1376H).

**[3].** "Sahihul Bukhariy" Na Imam Abu Abdillah Muhammadu ibn Ismaa'il Albukhariy –Allah ya yi masa rahama- (Ya rasu 256h).

**[4].** "Sahih Muslim" Na Imam Abil Husain Muslim bn AlHajaaj An-Naysaburiy – Allah ya yi masa rahama- (ya rasu. 261h).

**[5]** " Sharhul Mumti' ala Zadil Mustakniy" Na Sheikh Muhammadu bn Salih Al-Usaimin – Allah ya yi masa rahama- (Ya rasu 1421h).

**[6].** "AlKaulul Mufid alaa Kitaabit Tauhid" Na Sheikh Muhammadu bn Saalih Al'Usaimin – Allah ya yi masa rahama- (Ya rasu 1421h).